https://chat.whatsapp.com/DAqtxT35oDPJgXIGyih8qT?mode=r_c

NIGERIA□□

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.□□

Proudly Nigerian □□□

MY FATHER'S LAND

The Noble Writters

Dedication is our strong □□□□□

Let's dive into the work of fiction □□

THE REGRET

(Dana sani)□□□

When Love meets temptation □ who survives?

BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM □

::

Tuna baya a Nigeria

Flash back □□

2004

Kwance ta ke akan gadonta ta ƙurawa wuri ɗaya ido, wanda kallo ɗaya zaka ma ta kasan cewa tayi nisa cikin tunanin da ta keyi, idon ta fal ya taru da hawayen dake neman hanyar gangarowa, fuskar ta a Kumbure yake wanda zai baka tabbacin cewa dukan ta akai.

Bankaɗo dakin da akai ne ya sata tayi saurin tashi daga kwancen da take wani ɗan saurayi wanda bazai wuce shekara 27 ba ya shigo yana ta muzurai.

Ƙara fashewa tayi da kuka mai tsuma zuciya cikin shashsheƙa tace " Ya Nabil nayi Alƙawarin bazan ƙara bijire maka ba amma kasani cewa bazan iya zubar da cikin da yake jikina ba dan Allah kai haƙuri ka barni da abinda yake cikina....

Bai barta ta ƙarasa ba ya wanka ma ta mari sannan ya ɗaura da cewa"Saboda kin samu wajen arziki gidan arziki shine zaki cika ni da yara, ban shirya na zama uba ba sai nan da shekaru uku.

Yana faɗin haka yasa kai ya fuce daga cikin ɗakin.

Duk kalmar da ya shigo bakinta furtashi take yi ta rasa ta ina zata fara, ta rasa Mey ke bibiyar rayuwarta shin wannan aure ne ko ƙaddara batafi shekara 17 ba auren shekara huɗu kenan saboda a gidansa ta fara jinin ta na al'ada.

In ta tattara ma zata koma gida, can ma iyayenta korar ta zasuyi wai ta ina zasu samu abinci in ba ita ta taimaka musu ba, tunda ta auri Nabil tun satin farko data tare da taji daɗi har yau bata san mey ne soyayyar miji ba.

"Ya Allah ka kawo min mafita ni ɗin na kasance baiwace agareka mai ƙasƙantar da kanta ya rabbi kar ka ganni da laifin zubar da cikin nan da zanyi akaro na shida, ya Ubangijina ka kawo min ɗauki ba dan ni ba, ya Ubangiji na ka ganar da bawanka ba a ƙurarren lokaci ba ta faɗa kuka na ƙara kufce mata.

Ta shiga rairawa kamar ba gobe mayafin ta ta sanya tunda atamfa ce ajikin ta riga da skirt, tanufi ɗakin sa ta sanar dashi abinda ta yanke, daman yasan za'a rina kuma yayi farin ciki sosai.

Hanyar asibitin Nassarawa suka nufa akai gwaje gwajen da za'ayi tunda likitan abokinsa ne.

Doctor hafiz numfashin sa ya furzar sannan ya ce" wannan ne ciki na ƙarshe da zaku iya zubarwa idan ta ƙara wani cikin sai dai ta haifeshi.

Ɗago kanta tayi suka haɗa ido da Nabil, hawaye ta shiga zubarwa bana wasa ba, cikin dasashhiyar muryarta ta ce" Ya Nabil dan Allah kar azubar da cikin nan ko sau ɗaya ne kaima ka amsa sunan ka a matsayin uba dan Allah. Wani banzan kallo ya wurga mata wanda ya saka cikinta kaɗawa, a take tayi shiru kawai ba tare da ta shiryawa shirun ba.

Doctor hafiz ne ya kalli Nabil ya ce " As I said earlier wannan ne ciki na ƙarshe da zaku zubar, sannan ku kiyaye, duk abinda yaje ya dawo babu ruwana a lamarin nan man.

Daga haka ya tashi ya zaga ta cikin office ɗinshi wani ɗan madaidaicin wuri da aka zagaye da labule irin labour room komai na wurin is beyond neatness.

Tana ganin ya tashi ita tabi bayan sa dan ta saba yanzu ba sai yace ta shigo ba, shiga ɗakin tayi ta saka kayan da aka tanada mata sannan yayi abinda zaiyi ya cire cikin daga jikinta abinka da ƙwararren doctor, sannan ya haɗa mata da wankin ciki.

Sai da aka bata rest bed na awa biyu sannan sukayi hanyar gida a cikin motar ma a takure ta ke motsi kaɗan in yayi akan idonta ne saboda tsoron kar ya sakar mata ranƙwashi.

Koma warsu gida ke da wuya yace da ita ta shiga kitchen ta dafa mai sakwara da miyar ganye daga haka ya shiga ɗakinsa ya kulle ƙofar sa.

sai da ta zauna ta fashe da kuka tukunna, saboda inda sabo ta saba amma ai ba'a sabo da wahala.

Sai da tayi mai isar ta sannan ta shiga ɗaki tayi wanka sannan ta dawo madaidaicin kitchen ɗin su, da ƙyar ta ƙarasa fere doyar sannan ta ɗora yar tukunyar ta a gas saboda ba laifi Nabil nada kuɗi sosai, sannan ta ɗauki 300 ɗin daya ajiye mata na cefane ta fita kafin ta dawo tasan doyar ya dahu.....

I just started this Novel OOO

I need yah reactions

Allah sarki Ikimat tun banyi nisa a Novel ɗin nan ba na fara tausaya miki

The Regret

Is not just a Novel

Buh matsalolin da yaya mata kan fuskanta agidan mazajen su.

What comes arround goes arround

Abinda ka shuka shi zaka girba

Pending Amarya as usual

Emotional Vibez https://chat.whatsapp.com/DAqtxT35oDPJgXIGyih8qT?mode=r_c

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.

::

The Noble Writters

Dedication is our strong □□□

THE REGRET □□□□□

when love meets temptation □ who survives?

Rayuwa ta kan zo da sauyi ko wani yanayi□

Gwara ka riƙe ƙaddara kan ka shigewa tsautsayi□□

NIGERIA □□

For Pending Amarya ✍✍

NDA DUBDO□

My Maiduguri ppl□😂

Page 2

★★★★

Zama tayi ta fashe da kuka tukunna saboda inda sabo ta saba amma ai ba'a sabo da wahala.

Sai da tayi mai isar ta sannan ta shiga ɗaki tayi wanka sannan ta dawo madaidaicin kitchen ɗin su, da ƙyar ta ƙarasa fere doyar sannan ta ɗora yar tukunyar ta a gas saboda Nabil na da kuɗi, ta ɗauki 300 ɗin daya ajiye mata na cefane ta fita kafin ta dawo tasan doyar ya dahu.....

Tana dawowa kam doyar data ɗaura har ya dahu tayi sauri ta yi jajjage.

Da ƙyar ta gama daka doyar sannan ta samu ta ɗaura miyar ganyen tana gamawa ta zuba su a madaidaiciyar coolernta ta nufi ɗan madaidaicin ɗakinsa dashi, shigar ta keda wuya ta ganshi zaune babu abinda yakeyi ya harɗe ƙafar sa, he looks very cute without faɗarsa agareta.

Ƙarasawa ta yi ta ajiye farantin a ƙasa ta ɗurƙusa a dai-dai wurin cikin nutsuwa irin na Ikimat ta ce "Yallabai ga abincin naka, shin zan iya tafiya ya shugabana (Ni kam yau pending naga iko)(lolz).

Bai ɗago ya kalleta ba sannan shi bai ce mata ta tafi ba, a haka tai ta tsugunnawa a wurin, har sai da ƙafar ta tayi tsami.

"Miƙo min ruwa" shine abinda ya faɗa ba tare da kuma ya ɗago ba, hannunta na karkarwa ta ɗauki cup ɗin ta miƙa masa, kaɗan ruwan ya ɗan fallatsa masa ba shiri ya ɗago kanshi ya kalleta idonsa da ya yi jaa wanda ke ƙara tsorata ta a duk lokacin da ta mai laifi suka kalleta.

Saboda rikicewan da ta yi bata san lokacin da ta sakar mai cup ɗin ruwan ya zubo mai ajikin sa ba.

A gigice ta fara magana "Yaya Nabil dan soyayyar ka da ma'aiki karka dake ni, wallahi juwa nake ji" ta faɗa tana ƙara fashewa da kukan da bata san ranar dainawar sa ba.

Baiyi mata magana ba sai da yayi mata kallon second biyar, sannan ya ce "Cinye abincin da kika dafa.", ɗago kai tayi tana kallonsa sosai, ta ga babu alamun sassauci a tattare da maganarsa.

"Ya Nabil Dan Allah Mai na maka? Mai na maka daka tsane ni ?? Mai na maka da baka son jin muryata ko mu zauna a inuwa ɗaya a tare dani da kai? am hurting billah just say something". ta ƙarasa maganar tana lulluɓe fuskar ta da mayafinta.

cikin muryarsa na i don't care yace "Ni da ke mun zama Sa'anni da za ki tambaye ni mai kika yi min ko?.'' Ya tambaye ta tare da ƙafeta da idanunsa masu firgitata.

"A'a wallahi Yaya bada kai nake ba dan Allah kamin rai kabarni na huta karka azabtar dani, ba nida masaniyya akan auren mu dakai Dan Allah yaya". taƙa rashe maganar cikin sanyin murya.

Haka rayuwar ta ta cigaba a gidan Nabil duk ranar da wani na gidan su ko danginsu zasu zo a ranar zasu yi farin ciki zai zauna a gaban su suyi wasa da dariya da ita yanca koda ta kai ƙara ba za'a taɓa yarda yana muzguna ma ta ba.

A ranar zasuyi wasa sosai har ta gaggaya masa magana son ranta in sun tafi yayi mata dukan tsiya.

Yanca yake lallaɓata acikin dangi, har cousins ɗinsu mata na crushing akan sa.

Har kishi ya kan bayyana a tattare da su musamman kishi irin na Shuwa Arab

Banbancin kishin su da larabawa kaɗan ne.

March 11 2006

Bayan shekaru biyu

Yau ta ke jummah ta tashi da zazzaɓi ga amai da take ji yana taso mata ta rasa mey ke damunta, ga bacci da kasala da take yawan yi.

Saukowa yake yi daga matattakalar benen dake cikin falon abinka da masu shi.

Cikin takunsa na isa ya ƙaraso kusa da inda take amai acikin sink ɗin dining area.

Girma ya ɗan ƙaru a tattare dashi, ga jikinsa ya buɗe ba kamar da ba, murtuke fuska ya ƙara yi cikin muryarsa mai Amo ya ce "Hope is not what I'm thinking?" Cikin Tsananin firgita

Da rashin sanin ya iso wurin da take ta ɗago ta kai duban ta gare shi, ƙamshin turarensa ne ya cika mata hanci ta ƙara yunƙurawa zatai aman, ta sake shi ajikin sa daga sama har ƙasa, gashi ta kasance jummah farar shaddarsa ce ajikinsa.

Duk da halin data ke ciki bai hana ya wanka mata mari ba anan ta zube a ƙasa sumammiyya.

Komawa yayi sama ya janza kayan jikinsa.

Ko duba halin da ta ke ciki beyi ba ya saka kansa ya fita daga parlourn.

Sabuwar Mercedes Benz ɗinsa 2006 brand ya hau ya figi motar ya bar harabar gidan zuwa gidansu Ikimat, wanda ko wani friday ya kanje gaida kawun nasa Sannan siriki agaresa.

Ko da ya isa gidan, ba wani gidan talakawa bane ba sosai da ɗan kyanshi ba laifi.

Bayan sun gaisa da Malam Umaru his Uncle, ya shiga ciki domin gaida mahaifiyyar Ikimat, har yake sanar mata ai yace su taho tare ta ke faɗin ba zata zo ba.

Mahaifiyarta ta mai nasiha sosai akan rayuwar Aure sai haƙuri, sannan ta ɗaura da zata zo ya sameni.

Daga haka ya ajiye mata dubu biyar ɗinsa yayi mata Godiya ya ƙara gaba.

Ɓangaren Ikimat kam sai da sink ɗin ya cika yayi famm yana zuba sannan Allah ya sa ya ɗigo a fuskarta ta ja wani dogon numfashin wahala.

Wani kukan baƙin ciki ta saka tana Allah wadai da halin ya Nabil.

Bayan ta gama raira kukan nata jiki ba ƙwari tai hanyar kitchen ta ɗauko sweeper da parker ta share wurin sannan tai mopping duba da abubuwan zamani sun fara fitowa.

Wanka ta sake yi ta zauna ta na kallon kanta a madubi, Ma Sha Allah shine abinda na furta, ga wife material amma ba ta faɗa hannun tailor mai kyau ba.

Ikimat kyakkyawar mace ce wanda kowani ɗa namiji ke buƙatar ya gani ya mallaki irinta.

Black beauty irin Kanuri mix with Shuwa Arabi ɗinnan.

Bata wani jin yunwa sosai hakan yasa bata wani damu da tayi girki ba, parking motar da ta ji a ƙasa shi yayi sanadiyar murza mata ciki kamar wacca ta ga shadown mala'ikan mutuwa.

Ko da ya shigo da bai ganta a parlour ba ɗakin ta ya shiga direct, zaune ya tarar da ita ta zubawa mirror Ido, idanun ta duk dishe dishen hawaye, zaro idanunsa yayi yace"Wifey what are you crying for?" ya tambayeta, ɗagowa tayi ta kalleshi dalala, baki sake, ƙarasa shigowa yayi ya ajiye ledar dake hannun sa Wanda yake cike da Hollandia yourghurt da suya sai ƙamshi ya ke.

"C'mon ta so kici abinda na siyo miki harda favorite drink ɗinki", ya faɗa mata haka yana kallon ta ido cikin ido wanda itama shi take kallo ta ga reactions da ke cikin zuciyarsa.

Cikin siririyar muryarta tace "Ya Nabil am full bana son cin komai da daddaren nan".

Ran shi ɓace yace"kinga ta lallami na biki ki cire cikin da ke jikin ki ba tare da kin sani ba, amma da ke daga ƙauyen Maiduguri kika fito bazaki taɓa ganewa ba, kuma Wallahi kinji rantsuwar musulmi ba zaki haifi cikin nan ba" daga haka ya saka kai ya fita daga ɗakin.

Kuka ta ke son yi amma ta kasa, so ta ke ya barta ta je wurin mahaifiyyarta ta sanar da ita halin da take ciki ko zata samu mafita a wurin ta amma ta san halin Nabil ba barinta zaiyi ba.

Yanzu duk da doctor yace last cikin da zata zubar kenan tayi surviving da mahaifarta ya Nabil still wants to abort it.

Wannan wani kalar rayuwa ne, Ya Ubangiji ka kawo min ɗauki ka ramamin cikin gaggawa.

Zuciyarsa na tafasa ya bar gidan wurin ƙarfe 10 na dare shi kansa bai san inda zai je ba , tsayar da motar yayi yana tambayar kansa Mey yasa yake cutar da yarinyar da bata da nufi akansa sai Alkhairi, maisa bashida wani buri sai dai ya ga ya baƙanta mata.

Laifi ne dan tace tana sonshi? Wannan wani kalar jarabawa ne? , wani zuciyar ne ya ƙara zugashi tace "kamanta itace ta shiga tsakaninka da farincikin ka?" daga haka ya ƙara kama hanyar shi direct gidan ya koma.

Time ɗin har ta kulle ɗakinta da key, because tana tsoron ya shigo ɗakin ya taka mata ciki dan ba yau ya fara ba.

Kuma babu abinda zai hana ta haifar cikin sai dai in mutuwa tai ko kuma zubarsa daga Allah ya ke.

Dan ta daina zubawa Nabil ido yayi mata abinda ya ga dama....

What's wrong with this guy readers?

Meke damun guy ɗinnan?

Ku dai ki biyo Pending Amarya dan jin yanca zata kaya✍✍

Ta tanada muku amsoshin ku

This is just the beginning.

We haven't started yet

This isn’t the end. It’s the beginning of who they must become.

Because the hardest trials... leave the richest scars.

The Noble Writters ○

Let's end the war together

Kuyimana share sannan

Reactions ɗinku Is All we need the Most

Try your possible best guys 😍

Let the world feel what we have written ✍✍✍

Don't forget with Pending Amarya as usual
https://chat.whatsapp.com/DAqtxT35oDPJgXIGyih8qT?mode=r_c*JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION*✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.□□

::

The Noble Writters □□□

Dedication is our strong □□□

THE REGRET □□□□□

when love meets temptation □ who survives?

□□

NIGERIA □□

For Pending Amarya ✍✍

NDA DUBDO□

My Maiduguri ppl□😂

CHAPTER ONE :THE STRUGGLE'S □□

★★★★

Kuma babu abinda zai hana ta haifar cikin sai dai in mutuwa tai ko kuma zubarsa daga Allah ya ke.

Dan ta daina zubawa Nabil ido yayi mata abinda ya ga dama....

Haka rayuwarsu ta cigaba da tafiya har cikin ta ya girma babu wani cigaba da ta samu a wurin Nabil, in banda tsangwaman daya fi na daa, kuma har yau bai barta ta je gidansu ba, gashi ba daman tayi girki yace mata heavy food yake so duk da tsohon cikin ta haka take yunƙurawa ta mai duk abinda yake so.

Ya sha dukan ta ya take mata ciki babu adadi, ita dai abinda tasani shine In Sha Allah sai ta haife abinda ke cikin ta lafiya.

In yana abu sometimes ta kanji akwai ranar da zai daina, saboda ba ta ce Za'a yiwa yaransa ba tunda ya'yanta ne itama.

Idan tana jin kwaɗayin abu ta kan gayamai ya taho mata da shi, amma duk lokacin da ya dawo ta tambaye shi ina abinda nace ma ka zanci, ya kan kalle ta yace mata babu ruwansa da cikin jikinta.

Ta rasa ya zatai da lamarin Nabil ace ɗan cikin ka ba ɗan wani ba.

15 of December 2006

Ranar ta kasance jummah tun safiyar ranar ta ke jin zafi sama sama bayanta gaba ɗaya ya riƙe ta kasa zaune ta kasa tsaye.

Fitowa yayi cikin sky blue ɗin shaddarsa wacca ta mai kyau, ya tarar da ita sai safa marwa ta ke yi, har zai wuce sai kawai ya tsinci kansa da dawowa baya.

Cikin muryarsa mai daɗi ya tambaye ta "What's wrong with you? ko baki ganni zan fita ba? baki iya gaisuwa ba?." Kallonsa tayi still duk da cikin halin da take be hanata kokarin durƙusawa da niyyar gaishe sa ba, duk da azabar da ta ke ji bata kai ga ƙarasawa ba ta durƙushe a wurin tana yarfa hannu, tsaki yayi ya wuce tare da furta "Munafuka kullum cikin ƙaryar ciwon tsiya". Daga haka ya wuce wurin da yake parking motarsa, har ya shiga motarsa yana ƙoƙarin tadawa ko mai yamanta sannan ya dawo cikin parlourn.

Tana nan durƙushe a yanca ya barta sai kiran sunan Allahn ta ta ke yi da yarfa hannunta.

Kallonta yayi sosai sannan ya ce "ke malama taso na kai ki asibiti". "Bazan iya tashi ba yaya, yaya ka yafemin mutuwa zanyi" ta faɗa tare da rushewa da kuka.

"Kinga am not ready for this drama, in za ki tashi ki tashi in kuma bazaki tashi ba toh kinga tafiyata". Ƙoƙarta tashi ta fara yi da ta ga da gaske tafiya zaiyi ya barta.

Sannu a hankali har ta miƙe ta fara tafiya a duƙe.

"Ina kayan haihuwar naki yake?" Ya tambaye ta as usual, "Baka siyamin ba" shine abinda Ikimat ta faɗa.

" Toh mai ya hanaki tambayata?" Ya tambaye ta tare da ƙafeta da ido, "Yaya zafi yake min Dan Allah kayi haƙuri, Ni tsoron gaya maka nake, kuma nasan inna faɗa ba siya min zakayi ba" ta ƙarasa maganar tana gunjin hawaye.

"Tun da ke kika yiwa kan ki cikin?".

Tsaki ya ƙara ja akaro na biyu sannan yace "Zakiyi tafiya ko saina ƙarasaki" tafiyan tafara yi sannu a hankali da ya gaji da tafiyar kawai ya sunkuce ta ya saka ta a bayan sit.

Bai kulle bayan motar da ya saka ta ba ya zauna a driver sit zai tayar da motar, juyowa yayi da kyau ya kalleta da kyau sannan yace "Kinga in zaki ware jikin ki ki ware ki kulle min ƙofar mota ba akanki aka fara samun ciki ba, mata nawa ne suke naƙuda basuyi haka ba saike, C'mon kulle min ƙofar motana.

A hankali ta lallaɓo ta kulle ƙofar saboda ita kaɗai tasan wani hali take ciki. Lallai Ya Nabil ya cika maƙiyin ta wanda kake cikin wannan halin da bai tausaya maka ba ai bazaku taɓa jituwa ba.

Tayar da motar yayi sannan ya ɗauki hanyar Hospital ɗin Nassarawa, basu wani daɗe ba suka ƙarasa Hospital ɗin.

A kiɗime ya fito daga motar ya ɗauke ta a hannu kamar yar baby yana ta zabga uban sauri (Namiji hankaka 😏).

 kallon fuskanta yayi tayi yana tafiya she looks pale.Mutanen wurin sai tausaya mishi suke, because kana ganin ta kasan son da yake mata bana wasa bane ba (Nabil ka ji tsoron Allah 😂)

Doctors ne suka duba ta, suka ga ba adai dai kan yaron cikin nata yake ba dole CS za'a mata idan kuma dole haifar sa za tayi za ta sha wahala ko kuma a rasa ta gaba ɗaya.

Ko da aka samu Nabil aka gayamasa ce wa yayi shi dai matarshi ta rayu (Ni pending Nabil zai min lahani 😂)

After 5 hours

..Cikin Ikon Allah aka ciro kyakkyawar yarta mai kama da ita.

Jijjiga ta farayi wanda da ƙyar likitoci suka tsayar da hakan.

Nabil aka kira ya kawo kayan baby a gurguje yaje bakin Hospital ɗin ya siyo kaya da

Kayan tea, da dai sauransu.

Bayan an shirya baby aka kawo masa ita Doctor ɗin tace "Here is your pink jet" , murmushi yayi ya ce "Tnx".

Kallon yarinyar yake wanda a ta ke ya ji wani matsanancin sonta ya ɗirar mai.

Duk da jaririya ce amma hakan bai hana bayyanar da kyawunta ba.

Sai motsi ta ke da bakin ta alamun yunwa ta keji.

Huɗuba yayi mata da sunan late sister ɗinshi FATIMA amma za'a ɗinga kiranta da LIYANA.

BAYAN FOUR DAYS

Yau ne aka sallami su Nabil daga Hospital, kafin suje gida kam kusan rabin familynsu na gidan amma ba kowa yazo daga Maiduguri ba, duba da yanca Nabil ke da zumunci da son yan uwa.

Ko da suka dawo gida bai yarda ya bar kusa da ita ba Ƙanwar Ikimat tai ta mai mita ya ƙi fita baƙi su shigo shi mai mata.

Ita dai Ikimat ba abinda ta keyi sai murmushi wanda yafi kuka ciwo.

Dan fatan ta bai wuce ace za'a tattara ta a mayar da ita gidansu ko gidansu Nabil ba.

Bayan anyi suna anci ansha an hantse bata ji alamun za'a ce ta tafi gida ba.

Ashe Nabil ya zaga baya yace ita ta faɗa mai babu inda zata je ta bar gidanta..

Babu wanda ya nuna mata alamar komai bayan taji abinda aka faɗa mata, tayi kuka sosai sannan tayi wa Nabil Allah ya isa ba adadi, haka rayuwarta ta cigaba kullum cikin ƙunci amma takan samu sauƙi ta sanadiyyar Liyana.

Idan ya dawo daga kasuwa kam Liyana ya ke ɗauka ya tafi ɗakinsa da ita har sai in kuka take sannan zai dawo da ita, kuma in ya dawo da ita ɗin zai tsaya akanta ne har sai ta gama breast feeding ɗinta zai amshe ta ya koma ɗakinsa da ita.

Liyana kam ta fi shaƙuwa da mahaifinta, kyakkyawar yarinya Ma Shaa Allah, bata da hayaniya ko kaɗan.

After 7months

Liyana ke rarrfe a parlour dake ranar Sunday ne bai fita kasuwa ba, ita kuma Ikimat na kitchen tana haɗa breakfast, rarrafen ta take yi hankali kwance, tana gwarancinta irin na yara jarirai, can jikin socket kam heater ne ta jona ruwan zafin da zata dama kunu saboda yanayi na mai shayarwa sai da abu mai ruwa da zai kawo mata ruwan nono.

Sam ba ta ji lokacin da ya ajiye Liya a parlour ba, kawai ita dai taji ihun Liyana tunawa da ruwan zafin da tayi ta saka a socket, Bata san lokacin da ta yar da wuƙar hannunta ba ihu ta ke yi tana kuka haɗe da gwarancinta a haukace Ikimat ta ɗauke ta sai taga ashe bata kunna socket ɗinba.

Ajiyar zuciya ta sauke, kafin ta juyo taji an fisge Liyana a hannunta tare da wanka mata mari, dafe ƙuncinta tayi ta kalli Nabil da yake kallonta kamar zai ɗaga ta sama, cikin muryarsa mai Amo ya ce "Ba ki da hankali ba kiga na ajiyeta ba da ban kashe socket ɗinba lokacin da na ajiyeta ba da tuni pink jet ɗina ta ƙone".

Kallonsa ta ke babu ko ƙiftawa sannan hannunta bai bar yar kafaɗar Liyana ba alamu dai kamar baka isa ka ƙwace min ya ba.

"Ba za ki saketa ba?" Cikin muryarta mai sanyi da kuma nuna gajiyawa da halin Nabil ta ce "Kai ka haifa min ita? Ba za'a saketa ba ɗin kai duk abinda zakayi".

Kallonta ya shiga yi bako ƙyaftawa, sannan ya juya ya ajiye Liyana akan kujera ya bata abin wasa haɗe da cewa "Lemme deal with your mom little princess" ƙyalƙyacewa Liyana tayi da dariya kamar taji abinda ya faɗa sannan ta maida hankali kan wasanta data keyi.

Zare belt ɗin jikinsa yayi ya naɗa shi a hannunsa sannan ya fara dukanta dashi ta ko ina ya samu a jikinta lafta mata yake yi, tun da ya zula ma ta ɗaya ta ke yaya kayi haƙuri amma ina Nabil zaneta ya ke taki ina, tun tana kuka har ta gaji.

Tsaki ya ja tare da faɗin "mara kunyar banza". Sannan ya ɗauki Liyana yayi sama da ita.

Haka rayuwarta ta cigaba babu wani sabo tsakanin ta da ɗiyarta har Liyana tayi shekara uku a duniya .

Kuma acikin shekaru ukun nan sau biyu ta taɓa zuwa gidansu duk da babu wani nisa tsakanin bachirawa da hotoro.

Shi zai kaita school shi zai dawo da ita can wurin aiki ma tunda tayi wayo tare suke zuwa tsakanin ta da Liyana sai dai gaisuwa da shiryata ta tafi school shima ba kullum ta ke shirya ta ba.

Yau dai ta kasance Sunday tun safiyar ranar ya sanar da ita akwai taron family , a gurguje tayi ayyukanta sannan ta shirya cikin wani after dress Mai ɗan kyau tunda Nabil duk iskancinsa yana wadata ta da komai na more rayuwa, tayi kyau ba laifi sannan ta riƙe hannun Liyana dake tsaye kusa da Abbanta sai da ta kalli fuskar mahaifinta sannan ta koma wurin Umminta .

Murmushi ya mata mai nuni da alamun ki je wurinta sannan yayi gaba cikin shigarsa mai kyau.

Sabuwar motarsa kirar Peugeot ya hau 2009 brand new blue color sai ɗaukar Ido take yi.

A hanyarsu na zuwa gidan suna zuwa aka fara gabatar da taro Ikimat kam kamar bare a cikin dangi, Nabil kuma kamar zai maidata ciki tsabar nuna kulawa da soyayya, cousins ɗinta da ba suyi auren ba sai taɓe mata baki su keyi.

Bayan dawowarsu gida kam ko kallonta be yi ba ballantana ta sa ran yau Liyana zata ɗan kwana a wurin ta ta samu taji ɗumin yarta.

Ɗakinta ta shiga tayi wanka ta saka kayan bacci mai ɗan kawri saboda yanayin damina dake saukowa a yan kwanakin nan.

Sai da ta gama shiryawa ta nufi ɗakinsa tsayawa tayi a bakin ƙofar ɗakin tana wasa da yatsunta ɗagowa yayi sosai ya kalleta na yɤan sakwanni sannan ya kawda kan sa gefe, cikin inda inda ta ce "emm.. Ya .. Nab...il please zak..... Kafin ta ƙarasa ya dakatar da ita da faɗin "I'm not in the mood of that nonsense".

"Ya Nabil that's not what you think, nace dan Allah Liyana zaka bani ta kwanta dani since Last week ko cikakken fuskarta ban gani b...a" ta ƙarasa faɗar maganar a yanke.

Tsaki ya ja ya cigaba da ordern atamfofin sa daga Ghana, ba tare da ko Kallonta ya sake yi ba.

A kwana a tashi ba wuya Ikimat nada wani cikin, lokcin Liyana shekarunta biyar amma tana da tsawon ƙafa Ma Shaa Allah.

Laulayin yazo mata da sauƙi amma sam bata iya aikin komai sai dai ta kira ƙannen ta suzo tunda yanzu ba laifi yana ɗan barinta ta fita amma ba sosai ba.....

The Regret wants your Reactions and comments for the person to regret 😂😂

Kaji wani turanci 😂😂

Omo ku biyu pending amarya dan jin yanca zata kaya ✍

Pending Amarya butterfly writter

Ɗawisu gidan ado marubuta masu muhimmanci

The Noble Writters Alhaji✍

What's wrong with this guy readers?

Meke damun guy ɗinnan?

Ku dai ki biyo Pending Amarya dan jin yanca zata kaya✍✍

Ta tanada muku amsoshin ku

This is just the beginning.

We haven't started yet

This isn’t the end. It’s the beginning of who they must become.

Because the hardest trials... leave the richest scars.

The Noble Writters ○ □

□

Let's end the war together □□

Kuyimana share sannan

Reactions ɗinku Is All we need the Most □□

Try your possible best guys 😍□

Let the world feel what we have written ✍✍✍

Don't forget with Pending Amarya as usual □
□https://chat.whatsapp.com/DAqtxT35oDPJgXIGyih8qT?mode=r_c

NIGERIA□□

MY FATHER'S LAND

The Noble Writters

Proudly Nigerian □□□□□□

Dedication is our strong □□□□□

NDA DUBDO THE REGRET FAMILY □😂□ □

Bana cikin THE REGRET ni kam □□□

Let's dive into the work of fiction □□

THE REGRET

(Dana sani)□□□□

When Love meets temptation □ who survives?

BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM □

What comes arround goes arround □ □

Abinda ka shuka shi zaka girba □

Abinda kayi wa yar wani za'a yi wa naka □

Duniyar kenan○□

Is not that easy with you here, buh I know I want you to stay.

See this could be us in a few years □□

Chapter two: The past that never let go.

Page 4

::

Laulayin yazo mata da sauƙi amma sam bata iya aikin komai sai dai ta kira ƙannenta suzo tun da yanzu ba laifi yana ɗan barinta ta fita amma ba sosai ba.

Tun da yasan daɗin yara kam yanzu yakan kaita scanning ba kamar Liyana ba amma fa Liyana na kusa da shi Ikimat kuma ita rayuwarta a bayan mota ne.

Tasan wasu daga cikin maƙotanta sosai barimma Ummin Salim maƙociyyarta ta ƙwarai takan shigo gidan su yi hira tun da ba kullum Nabil ke barinta ta fita ba.

Yau ma kamar kullum tazo tare da kawowa Ikimat Ɗanwake tun da ita gwanar son Ɗanwake ce sosai.

Suna zaune suna hira wanda duk akan mazajen su ne, Ummin Salim ke tambayar Ikimat "Kince za ki faɗamin sanadiyyar da ya sa Nabil ke muzguna miki kuma har yanzu baki gayamin ba.

Ko har yanzu ba ki yarda da ni bane ba?". Cikin muryarta mai sanyi ta ce "Ko ɗaya wallahi Ummin Salim, amma bara na baki labari."

Tuna baya

Nabil ya kasance cousin brother agareni ata dalilin mahaifinsa da mahaifina yan uwa ne mamansu ɗaya babansu ɗaya.

Na kanje gidansu Ya Nabil sosai duk da mahaifinsa na da kuɗi sosai bana wasa ba, yawanci acan nakan cinye hutuna na makaranta tun da bodin school nayi.

Ni kuma Ummi Salim tun da na taso naga Ya Nabil nake jin soyayyarsa araina, wanda har yau duk muzgunawarsa bai taɓa fita daga raina ba. Lemme just get straight to the point Ummi Salim.

"Yaya Nabil na soyayya da da wata yarinya mai suna Rufaidhat a unguwarmu ta ke muna magana da ita sosai duk da ni bansan suna soyayya da ya Nabil ba, nikam kawai dan inga ya Nabil ma nakan je gidansu na cinye kwanakin hutuna, inna zo gidanmu baifi nayi kwana biyu ba na koma school.

Soyayyar Nabil da Rufaidhat kam sai ƙara linkaya ta ke yi saboda zuwa lokacin mutane da dama a dangin sun sani wanda ni bansan da hakan ba.

Kwatsam ina school lokacin ina js2 ƙanwarsa wadda ta ke ƙawata mai suna Mansura ta sanar dani halin da ake ciki.

Na sha kuka sosai wanda har na cire rai da aurensa saboda magana na ƙoƙarin zuwa wurin magabata, in anzo min visiting akan zo da shi amma sai visiting na ƙarshe da za'a min a js2 na tarar ba' a zo da shi ba.

A ta ke na shiga cikin mawuyacin hali sa bo da indai a class ɗinmu kake kowa yasan alaƙata da Ya Nabil na yɾan uwantaka da ma wanda nake cusa kaina a wurin shi duk da ƙanƙantar shekaruna.

Har akai jarabawa wanda zai kai mu ga js3, mu kai hutu a lokacin shekaruna 13 na dawo gida still gidansu ya Nabil na sauka, Ummin Salim bazan miki ƙarya ba da ace ni Nabil ke so da nayi dace a duniya, saboda lokacin da na ke babu aure a tsakaninmu komai ya samu nice duk abinda ya samu ni yake bawa duk ƙanƙantar abun.

Bayan dawowata da sati ɗaya gidansu a lokacin Ya Nabil na maganar kai kuɗi gidansu Rufaidhat yana ƙoƙarin sanarwa da Abbana sai shikuma ya sanarwa da Abbinsa.

Toh ranar ta kasance Lahadi kowa na gida muna ɗaki ni da Mansura muna tattaunawa akan yadda zan cire soyayyarsa pldaga cikin zuciyata, ashe lokacin kuma Ammin ya Nabil ta gama jin duk wani feelings ɗina a kansa.

Dan kawai tasa ni farinciki ta sayar da farincikin ɗanta dan ta cika min nawa muradin.

Sai a lokacin ta sanar da Abbinsu Ya Nabil yadda taji ina magana harda kuka.

Bai yi ƙasa a gwiwa ba ya kira Nabil ya sanar dashi ya na son ya aureni, babu kunya Nabil ya ce wa mahaifinsa bazai iya aurena ba saboda ni ƙanwarsa ce sannan shi mai ra'ayin mata ɗaya ne ballantana ya aure ni ina yiwa Rufaidhat wanke wanke.

A take mahaifinsa ya wanka masa mari wanda a take fushi ya ɗebesa ya zo har inda nake yayi min barazana akan inna yarda na aure sa.

Ban mai magana ba sannan ban nuna alamar sanin abinda Abbih ke shirin yi ba.

An fi sati ɗaya ana bawa ya Nabil haƙuri mahaifinsa har alƙawarin zai bashi dubu hamsin yayi duk abinda yake so nan ma ya Nabil yace babu abinda zaiyi da kuɗi, kuɗi bazai iya siyan soyayyar sa da Rufaidhat ba.

Abin ne ya harzuƙa Abbinsa ya ce mai indai har ya auri Rufaidhat ya tsine mai daka cikin yʻayʻansa sannan in ya auri Rufaidhat ya ajiye duk wani abu da yake da wani abin family ɗin madaki saboda shi Aliyu Ibrahim ba'a haifi ɗan da zai juya sa ba.

Wannan shine sanadiyyar duk wani muzguna min da yake yi da kuma cin fuskar da yake min".

Ajiyar zuciya Ummi Salim ta yi sannan ta ce "Gaskiya Ikimat kinyi ƙoƙarin da ba ko wacca macace zata yi ba, kuma har yanzu babu wanda ya sani a gidanku ko dangin ku?"..

"Ummu Salim kenan ai babu wata alama da ya bari, ke da kike kusa dani ga baki ga hanci da ban gayamiki ba za ki sani?".

Nodding Ummi Salim ta mata alamar a'a.

Sannan ta cigaba da faɗin, "Ko bayan auren Ummu Salim Nabil bai bar ni na cigaba da school ba, sai dai idan Abbinsa ya tambaye sa yace ai ina zuwa day ya mayar dani.

Ni dai innace ban yafe ba wallahi zai bi Nabil.

One week ka ɗai na san mai daɗin aure wanda har yau kalubalen dake cikin ta nake fuskanta.

Nabil ya taɓa bari na for good ten days ba tare da ya bani abinci ba.

Haƙurin da nayi da Nabil bana fata Liyana ta samu kalar wannan mijin, bana fata wannan kalmar na abinda kayi wa ɗan wani ya yi ta si ri akan yʻayʻana duk da bansan mai ke cikina da zan haifa ba.

Haka ta gama korowa Ummu Salim duk wani abin da ke damunta irin cin fuskan da Nabil ke nuna ma ta for good nine years da aurensu.

Ita dai Ummu Salim babu abinda ta keyi in banda hawayen da ke zuba a idanunta wanda nima kaina pending amarya sai da na zubar da hawayena akan al'amarin Ikimat.

"Innalillahi ƙarfe huɗu yayi banyi girki ba kuma Wallahi yanzu zai dawo tun da da Liyana suka fita". Ikimat tayi maganar saboda ta kashe zancan duk da ta na son faɗawa wani, amma ba ta son abinda zai tona asirin wanda duk duniya shi ta ke son ta ƙare rayuwarta da shi sannan kuma ko ba komai shi ɗin ya kasance uban yʻayʻanta ne.

Da haka ta ƙarasa shiga kitchen ɗin da ke shaƙe da kayan abinci.....

Na yau ba yawa manage please

Wacece Rufaidhat?

Wannan ne kaɗai dalilin Nabeel?

Who's the real star the Mom or the daughter?☺

Who's the one regretting □

Readers mun kusa dawowa labari faa muyi paka paka mu gama mu ɗaura beyond heart break because nayi missing kowa wallahi 😂✍

This is just the beginning

We haven't started yet

This isn’t the end. It’s the beginning of who they must become.

Because the hardest trials... leave the richest scars.

The Noble Writters ○ □

Ɗawisu gidan ado □□□

Let's end the war together □□

Kuyimana share sannan

Reactions ɗinku Is All we need the Most □□

Try your possible best guys 😍□

Let the world feel what we have written ✍✍✍

Don't forget with pending amarya as usual □□□□ □

> THE REGRET ONLY ON PENDING AMARYA'S BOOK CORNER.

> THE REGRET (Dana sani)

> EXTRA ORDINARY EVERYDAY ONLY ON PENDING AMARYA'S BOOK CORNER □ □
https://chat.whatsapp.com/DAqtxT35oDPJgXIGyih8qT?mode=r_c

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.□□

::

The Noble Writters □□□

Dedication is our strong □□□

THE REGRET □□□□□

when love meets temptation □ who survives?

□□

NIGERIA □□

For Pending Amarya ✍✍

NDA DUBDO

My Maiduguri ppl😂

CHAPTER THREE : RUFAIDHAT

Page 05

"Innalillahi ƙarfe huɗu yayi banyi girki ba kuma Wallahi yanzu zai dawo tun da da Liyana suka fita". Ikimat tayi maganar tare da tashi tsaye tana ƙoƙarin shiga kitchen.

"Ikimat ba dai abinci za ki dafa ba?". Ummu Salim ta tambayeta cikin nuna kulawarta a gareta, "Eh Wallahi Ummu Salim yana hanya kinsan jiya ma haka na shirice ƙarshenta ni na cinye abincin ma".

Dariya Ummu Salim ta yi tare da ce wa "Malama zo ki huta abincin da na dafa da ke nayi ai".

Godiya Ikimat ta mata tare da zama suka cigaba da hira amma ba wanda suka fara ba, har magrib yaya Nabil bai dawo ba. Sai sannan Ummu Salim ta mata sallama tare da tambayarta yaushe zata cigaba mata labarin, "Duk lokacin da kike da time ta ce mata". Daga haka tayi mata sallama ita kuma ta wuce sama tun da har ta jera dambun da Ummu Salim ta ba ta.

Sai ƙarfe 12:00 Nabil ya dawo har Liyana tayi bacci, ƙwanƙwasa mata ƙofa yayi, ya bata Liyana sannan ya ce ta kawo masa abinci yana jiranta.

Zuciyarta na dukan uku uku ta ƙarasa ɗakinsa da farantin abincin nasa, da ya buɗe ya ga dambu ne ya mayar ya rufe, sai da ya duba agogon ɗakin sannan ya mayar da dubansa gareta ta re da ce wa "Make something heavy, and be fast about it". Duk da girman cikinta bai hana ta russunar da kanta agareshi ba cikin sanyin muryarta ta ce "Your wish is my command sir ". A hankali ta ƙarasa tashi, tayi gaba da ɣar ƙwallarta a idonta.

Ko da ta shiga kitchen ɗin rasa mai zata dafa masa tayi, kamar tayi kuka, ta fere doya ta dafa mai pourage yam (faten doya) sai 12:50 ta gama duk bacci ya baibaye mata ido a haka ta kawo mai gabansa ko da tazo a time ɗin bacci ya ke yi, anan ta ajiye mai abincin sannan ta zauna kusa da shi a ƙasan kujerar falonsa anan bacci ya ɗauke ta ita ma.

Can cikin bacci ya tashi ƙafarsa ta buge mutum da ke kwance ƙara matsar da ƙafar shi yaƙara yi wanda ya sauke shi a daidai cikinta, wani Ihu ta saka "zai kashe ni!" A haukace baccin da ke idon sa ya washe agogon ɗakin ya kalla ya ga 2:56 uku saura, Bai damu da yanca ta ke ba ya ce "Ina Liyana?" Ya tambayeta a tsawace, kamar za tayi kuka ta dafe cikinta ta ce "Yaya tana ɗakina, yaya cikina zan mutu".

Ko kallonta be yi ba ya shiga ɗakinta sai da ya tabbatar Liyana na nan, sannan ya shiga closet ɗinsa ya ɗauki belt. Dawowa yayi ya shauɗa ma ta a cinye, a zabure ta tashi ta na hawaye, cikin shashsheƙa ta ce "Yayanmu Please allow me to rest ba fa akanka aka fara first love ba, Rufaidhat ta riga tayi aure atleast kai ma kayi moved on mana".

Kallonta yayi sosai sannan ya ce" tun da ke kika aurar da ita, kinci darajar dare ne yanzu amma Allah ya kaimu da safe za ki san ko ni waye". Daga haka yayi bagging ƙofar ɗakinsa. Kullum da tunanin Rufaidhat ya ke kwana ya ke tashi, yana sonta amma sai Allah be yi zai mallaketa ba daga haka dai bacci ya kwashe sa ba tare da ya sani ba.

Washegarin ranar tun da ta tashi ya ke sata aiki sai da ta goge stairs, ta wanke bango, ta goge kujeru, ta wanke motocinsa kala uku, sai da ta tsaya a bakin gate ya fita da mota ya dawo cikin gidan fiye da sau 10 kuma ba nisa ya ke ba, tana zama daga buɗe mai gate ya ke ƙara fita.

Duk abincin da ta dafa sai ya ce ta sake wani shi heavy food ya ke so, ta dafa abinci yafi kala goma.

A ranar dai Nabil bai je kasuwar kwari ba.

Tun asuba da ta ta shi sai ƙarfe 12 na dare ya barta ta koma ɗaki ta kwanta ga cikinta da ya ɗan fara girma ba laifi

Tun Ummu Salim na turo almajirinta tana mai yaren kurame har ta gaji.

Ita ma Ummu Salim ɗin ba ta ƙara aiko wa ba.

After one week da lamarin Ummu Salim ta zo ta sanar da ita komawarsu Abuja saboda transfer ɗin wajen aiki da aka yiwa mijinta.

Bayan ta gayama Ikimat kaɗan ya rage bata yi kuka ba because a ranar zasu tafi, ha ka Ikimat ta yini a gidan duka bata da wani kuzari, ga shi Abbin Liyana sun fita Shopping na school ɗin Liyana. Sun je Grand Square siyan chocolates, a sukwane tayi aikin ta da zatayi ta gama, saboda ba ta jin daɗin jikin ta sosai.

Ɓangaren Nabil da Liyana kuwa ko da su ka bar gidan ba su wuce ko ina ba sai Grand Square, suna ciki shi da LIYANA suna siyayya ta riƙe mai hannu sai dariya ta ke, idanunsa su ka sauka akan wata matashiyyar mata wacca bazata fi shekaru 25 ba da jaririya a hannunta cikin kaya na alfarma.

Cikin dasashhiyar muryarsa da ta dishe a lokaci ɗaya ba tare da yayi noticing ba ya furta " RUFAIDHAT? RUFYNA?? Is that you?".

Wadda aka kira da Rufaidhat ce ta juyo da fuskarta cikin shigarta na super holland kyakkyawace amma ba ta kai Ikimat kyau ba.

Cikin Muryarta mai kyau ta ce "Nabil dama ka na nan". Ta faɗa tare da murmushi.

Murmushi shi ma ya mata ya ƙaraso kusa da ita ya ce " yar yaya Nafisat ɗin ce haka?".

"Yar yaya Nafisat kuma?, ai wannan yata ce ". Rufaidhat ta faɗa ta na kallon Nabil ta re da mai murmushi mai sanyi.

"Ban gane yar ki ba? Haka mukai da ke?? Daman yaudarata kike da niyyar yi?? For almost ten years da muke soyayya da ke did I deserve this from you?? Na cancanci haka daga gareki Rufaidhat???", kuma.....

Ba ta bar shi ya ƙarasa ba ta ce "Ban gane yaudara ba Nabil ya zaka na min faɗa kamar wani babana, kai ba'a kira ka mayaudari ba sai kai ne za ka kira wani da

kalmar yaudara?? Kai da kayi aure kafin nayi faa? Ka haifi yʼa kafin ni na haifa?, babu wanda baya shaidar kalar soyayyar da ka ke nunawa Ikimat.

Bayan auran ka ma ba ka barni ba sai da na ɓata kusan shekaru shida ina jiran ka, kullum ba kada zance sai you have to zeal something wanda har yau bana tunanin kayi zealing ɗinsa, maƙaryaci, mayaudari. Da tuni na tsaya jiranka kayi draining time ɗina da energy na wa gari zai waya??.....

> Readers mai makomarsu ? Mai rufy ke nufi da abinda ta gayawa Nabil □□

> Tsakanin Uwa da yʼa wace tauraruwa?

> Pending Amarya na ɗauke da amsoshin tambayar da zaku zo mata dasu□

This is just the beginning.

We haven't started yet

This isn’t the end. It’s the beginning of who they must become.

Because the hardest trials... leave the richest scars.

The Noble Writters ○ □

□

Let's end the war together □□

Kuyimana share sannan

Reactions ɗinku Is All I need the Most □□

Try your possible best guys 😍□

Let the world feel what we have written ✍✍✍

Don't forget with Pending Amarya as usual □ □

> Pending Amarya's book corner.

> The Regret only on Pending Amarya's book corner Extraordinary everyday □ □

https://chat.whatsapp.com/DAqtxT35oDPJgXIGyih8qT?mode=r_c

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.□□

NIGERIA□□

MY FATHER'S LAND

Proudly Nigerian □□□□□□

Hausa Writter from Igala land □ □

The Noble Writters □ □ □

Dedication is our strong □□□□□

NDA DUBDO THE REGRET FAMILY □😂□ □

Bana cikin THE REGRET ni kam □□□

Let's dive into the work of fiction □□

THE REGRET

(Dana sani)□□□□

When Love meets temptation □ who survives?

BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM □

What comes arround goes arround □ □

Abinda ka shuka shi zaka girba □

Abinda kayi wa yꞌar wani za'a yi wa naka □

Duniyar kenan○□

Chapter four: Her Womb □□

Page 6

::

Bayan auran ka ma ba ka barni ba sai da na ɓata kusan shekaru shida ina jiran ka, kullum ba kada zance sai you have to zeal something wanda har yau bana tunanin kayi zealing ɗinsa, maƙaryaci, mayaudari. Da tuni na tsaya jiranka kayi draining time ɗina da energy na wa gari zai waya??.

Kuma Bara kaji na gaya ma ka ina zaune da miji na lafiya fiye da yadda ka ke tunani, na barka lafiya."

Shopping ɗin da ba'a yi ba kenan ya dawo gida jikin sa a sukwane, ko da ya shigo ya ci sa'a ta na falo ba ta shiga ɗakinta ba.

Sallama yayi ya shigo falon abinda bata taɓa jin yayi ba.

Liyana ya ajiye akan 2 sitter sannan ya ƙarasa three sitter ya zauna, jikinta na rawa ta ce "Yaya sannu da zuwa" da wani irin sauri ta ƙarasa kitchen ta ɗauko bottle water duk da tsohon cikin ta haka ta tsugunna agabansa wani kalar runtse idanunsa yayi ya miƙa hannunsa zai ƙarɓi ruwan already daman ta riga ta buɗe bottle ɗin, sai ruwan ya fallatsa masa ajiki.

"Yaya dan Allah kayi haƙuri wallahi i didn't do it intentionally." ta faɗa ta re da ɗaukan tissue jikinta na kakkarwa alamar tsoronsa ta ke ji.

"IKI" ya faɗa da kakkausar murya, runtse idanunta ta yi, saboda yanzu an doshi 10years da taji sunan nan a bakinsa, is she still dreaming?", ta tambayi kanta, because har yanzu ba ta yarda da abinda take ji kuma take gani in her present ba, not even her past life wan da daman kullum da imagination ɗin past life ɗinta take bacci take tashi sannan kuma take rayuwa.

"Ikimat am sorr..... Ka sa ƙarasawa yayi kawai ya ta shi daga wurin zuciyarsa na masa ɗaci.

Ha ka rayuwarta ta cigaba da tafiya a gidan Nabil har ta haifi yar cikinta wanda shima Cs aka mata, ta sha wahala sosai because mahaifarta ya sami matsala an juyar mata da shi , ta yi kuka ta godewa Allah, kamar maye sai da ya kira Rufaidhat ya sanar da ita.(Soo Sad□□)

Seven Years later □□

A kwana a tashi girman mutum ba wuya Liyana ta na Jss2 in da ɗayar yarinyar mai suna Maimuna amma ana ce mata Ilham ta ke primary 2 rayuwar su gwanin burgewa an ƙara renewing gidan nasu komai ya zama na zamani.

Zuwa yanzu kam driver ke kai Liyana da Ilham school wanda duk girmanta sai tayi kukan Abbih ne zai kaita.

Akwai shaƙuwa sosai tsakaninsa da Liya wanda ko a gaban waye ba ya ɓoyewa.

A school sai labari ake da LIYANA wacca kowa a class ɗinsu ke son mata magana da kuma son aga ta na hulda da kai saboda kuɗin Abbinta, yau friday ko da aka tashi ba ta wani ɓata lokaci ba ta nufi primary section ta ɗauko Ilham ta re da riƙe mata hannu suka fito daga school compound ɗin.

Hannunta sar ƙafe da na Ilham har wani motan da ta ke sa ran na Abbine ya iso wurin, ƙirar Mercedes Benz s class 2018 sai sheƙi ya ke a hasken rana, fitowa yayi daga motar yana murmushin sa mai kyau ta re da karɓan jakar hannunta...

Abbih" Sannu da zuwa" ta faɗa da siririyar muryarta, mai daɗin sauraro.

Nabil kam girma ya zo mai a tattare da shi amma baifi under 40s ɗin shi ya ke ba, wannan wankan da ƙwalisar na nan, fuskarsa da ya ke murtukewa kaɗai ne ba ya nan shi ma ban san ko dan babu Ikimat ba.

Sai dai fa su muke kira da saurayi magidanci, he's soo calm ƙarasa saukowa yayi daga motar da murmushi a fuskarsa ya ce "Yʻammatana! Yʻammatana"Liyana da sai kumbure kumbure take taƙi juyowa, Tana tsaye a wuri ɗaya tayi folding hannunta, Ilham da zafin rana ya dameta, cikin muryarta na yara ta ce "Abbih Dan Allah ka buɗe min ƙofa na shiga mota ni nagaji da tsayawa."

Nabil ne ya juyo ya ce "Hajiya mammahna am soo sorry karkiyi fushi, Oya shiga front seat mu tafi gida Ammi tayi mana fried rice, Liyana ba ta bari Ilham ta shiga ba tayi sauri ta shige.

"Abbih ka kalleta ko?."(My Maiduguri ppl 😂).

"Yi haƙuri baby of the house shiga back seat kinji habibty".

Tun da su ka shiga motar babu wanda yayi magana, sai arround 12:30 suka ƙaraso gidan, komai na gidan anyi renewing ga masu aiki da aka sama Ikimat (Likafa ta cigaba babu labari Ikimat 😂).

Komai na gidan smells rich and elegant, bayan yayi parking a wurin da motocinsa su ke kusan kala biyar gaba ɗaya Mercedes Benz ne sai kuma sauran duba da yanayin motar da ake yayi vibe ne kusan kala biyu, wanda ya sa motocin suka cika kala bakwai.

Bayan yayi parking motar da gudu Ilham ta ƙarasa shiga entrance ɗin gidan, sanyin Ac sai ƙara ratsa living room ɗin ya ke.

Wata ƴar matashiyyar mata ce wacca ba zata wuce early 30s ɗinta ba zaune cikin boyel ɗinki na alfarma, tayi kyau sosai kallo ɗaya za ka ma ta ka ga tsantsar jin daɗi da kwanciyar hankali da ke wanzuwa a fatar ta da ma fuskar ta ba ki ɗaya.

Ilham ce ta ƙaraso ɗakin tayi hugging ɗin ta tare da bata ƙarar Liyana, dariya kawai Ikimat wadda su ke kira da Ammi a halin yanzu ke yi.

Cikin siririyar muryarta ta yi sallama su ka shigo falon tare da Abbihnta, Ikimat na ganinsa ta tashi tsaye ta re da faɗin "Yaya sannu da zuwa". Murmushi ya ma ta kawai ta re da zama akan kujera.

Kallonta Liyana ta yi cikin muryarta mai sanyi ta ce "Ammi ina fried rice ɗin?." "Wanda ki ka bani ajiya?."Ammi ta faɗa, Juyowa ta yi ta ɓangaren Nabil ta ce "Abbihhhhh" ta ja Abbin sosai, Nabil dariya kawai ya ke, "Daughter kin yarda Ammi fried rice tayi?" Na gaya miki ne kawai saboda bazan iya stressing kaina ba yau, kuma laifin da nai bazai wuce driver ne ya kai ki school ba.

"Ki kawo min ɗaki." Daga haka yayi upstairs tare da faɗin "ku shirya za mu fita yawo yau ".

Ba yaran kaɗai ba har Ikimat murna ta ke saboda ta san bachirawa zasu je yau ɗin.

Ko da yamman da suka je bachirawa tsallaken gabas gidan a gyare mai kyau bayan sun sauko a motar wani tsoho fari kyakkyawa irin kyawawan shuwa Arab ke zaune a madaidaicin ƙofar gidan ko da Liyana ta fito tsokanarta ya shiga yi yana faɗin maman Liya ke ce yau a gidan namu."

"Alhaji ka daina ɓata min suna." Liya na faɗin haka ta shige gidan kakannin nata, ko da ta ƙarasa cikin gidan direct ɗakin Mama Maimu ta nufa.

Mama Maimu, mahaifiyyar Ikimat kenan, cikin Isa ta zauna akan kujerar da ke ƙaramar parlourn ta re da faɗin "Tsohuwar manya!, come forward na iso gidan tun da ke ba za ki zo ba." A hankali ta fito daga uwar ɗakinta, cikin sanyinta da yaranta suka gada daga wurinta ta ce " ja'i ra kin iso kenan?, ina uwar ta ki mara son zuminci???." " Gada tayi ai." Shine abinda Liyana ta faɗa mata.

This is just the beginning □□

Hausa Writter from Igala land □ □

NDA DUBDO □ □ THE NOBLE WRITTERS

Mun fara shigowa cikin labari ku bani goyon baya da cigaba da kawo muku updates yanca ya dace.

Readers are we together □ □

Readers duk wacca ta karanta ba tayi comment ko like ba Allah ya isa ban yafe ba.

And I mean it a lahira sai ta biyani ✍✍

> Shin duk cin zarafin da Rufaidhat ta mai a public ya na tare da ita?

> Ku biyo Pending Amarya ✍ dan jin yadda zata kaya ✍

> What comes arround goes arround □ □

> The Regret (Dana sani) ONLY ON PENDING AMARYA'S BOOK CORNER □ □

> Extra Ordinary Everyday □ □
□https://chat.whatsapp.com/DAqtxT35oDPJgXIGyih8qT?mode=r_c

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.□□

::

The Noble Writters □□□

Dedication is our strong □□□

THE REGRET □□□□□

when love meets temptation □ who survives?

Hausa Writter from Igala land □ □

Rayuwa ta kan zo da sauyi ko wani yanayi

Gwara ka riƙe ƙaddara kan ka shigewa tsautsayi

NIGERIA

For Pending Amarya ✍✍

NDA DUBDO

My Maiduguri ppl😂

Chapter 5: The present is calling

Mama Maimu, mahaifiyyar Ikimat kenan, cikin Isa ta zauna akan kujerar da ke ƙaramar parlourn ta re da faɗin "Tsohuwa manya!, come forward na iso gidan tun da ke baza ki zo ba." A hankali ta fito daga uwar ɗakin, cikin sanyinta da yaranta suka gada daga wurinta ta ce " ja'i da kin iso kenan?, ina uwar ta ki mara son zuminci???." " Gada tayi ai." Shine abinda Liyana ta faɗa mata....

Ko da su Ikimat da Ilham da Nabil suka shigo bayan sun gaisa, ta ƙara haɗa musu da nasiha sannan su ka bar gidan gidansu Nabil su ka wuce rijiyar zaki daga nan kuma su ka da wo gida.

Tafiya ta yi tafiya Su Liya na Senior Secondary School Grade 12(ss3) ita kuma ILI na Jss3, wani kalar shaƙuwa ke tsakanin Ilham da yayarta.

Ɓangaren Nabil da Ikimat kam sun doshi 10years yanzu babu wata matsala amma wannan shaƙuwar babu ita a tsakaninsu, in ta mai magana sai dai murmushi, sometimes ma abin ya kan motso shi yayi ma ta halin nasa amma ba duka kallo ɗaya ma in ya ma ta za ta sha jinin jikinta.

Let's start the Journey □□

Tafiya ta ke sannu a hankali trying all her best ta tsayar da hawayen da ke bin ƙuncinta, Ilham ce ta tawo da gudu ta na binta wanda alamu sun nuna da ga joint su ke, gudu ta ke sosai saboda ta cimma yayar tata, alamun girma sun bayyana ajikin ko wannensu, barimma Liyana da ke sanye cikin jump suit black color da farin tootle neck with white jersey Veil, shape ɗinta ya fito soo Ma Shaa Allah.

Wata Mercedes Benz ce ta fito daga wurin da su Liyana su ka fito da gudu, motar ce ta sha gaban Liyana, Abbin Liyana naga an rubuta a bayan motar wanda hakan ya tabbatar min da ce wa motar Nabil ce, fitowa yayi daga car ɗin ya ƙaraso kusa da Liyana, cikin kakkausar murya ya ce "Liya!, maganar da na miki ce ta ɓata miki rai?, ba za ki cika min burina ki zama doctor baa Liya?." Cikin muryar da ke haɗe da kuka ta ce "Abbihhhhh!." a sanyaye ta re da fashewa da kuka ta rungume shi ta cigaba da shashsheƙar kukanta.

"What's wrong with you daughter?, Mey akai miki?, kallon Ilham ya yi ya ce"Mammah kin yi mata wani abu ne ?.""Noo Abbih bayan mun yi waya da kai zaka zo ɗaukan mu then mukai yan ciye ciye da pictures, kana shigowa ita kuma ta fito ta na kuka shi ne nima na biyo ta, buh I have no idea akan kukan ta Abbih." " Okay" ka wai ya fa ɗa sannan ya ce su shiga mota daga haka suka wuce gida a mota ma juyin duniya ta yi magana ta ƙi sai kuka ta ke kamar an aiko ma ta da saƙon mutuwa.

Ko da suka je gidan ko abinci kasa ci ta yi Ammi ma ta zo ta yi ma ta magana juyin duniya ta ƙi bata amsa sai kukan da ta ke yi, daga ƙarshe ma Ammin tsawa ta daka ma ta sannan ta bar ɗakin.

Ko da akazo dinner ma ita ba ta fito ba shi ma kuma Abbih da bai ganta ba ɗakinsa ya wuce.

Bai jira cewar Neneh ba ya tashi ya bar gidan dan wani kalan zazzaɓi ke neman rufesa.

Ko da ya ƙarasa gida bai bi ta kan kowannensu ba flat ɗinsa ya shige tare da kwanciyyarsa.

Ɓangaren Liyana kuwa, tun da Abbhi ya dawo da ita gida kuka kawai take tun dawowarta, kallon pictures ɗinsu da Sultan kawai take tana kuka, Neneh ta zo ta mata magana har ta gaji sai dai ta ɗago ta dallawa Nenehn harara sannan ta kuma ɗauke kanta.

Ta yi kuka ta godewa Allahnta, ta kira Sultan amma fushi ya ke da ita yaƙi ya ɗaga for almost two weeks yanzu.

She has no choice than to give up ɗin da ta faɗawa Abbhin.

Komai ya cakuɗe mata.

Ta kira Lilian ita ma wayanta is not reachable, ta kira Ilham kuma network ba ya bari ta ji.

Haka ta fawwalawa Allah komai, first in history da ta ɗauki Kur'ani ta karanta saboda samun sassauci, because in dai karatu za ta yi sai dai ta karanta na ƙwaƙwalwanta bai fi aya ɗaya ba ta cigaba da jin waƙoƙinta.

Haka rayuwarta ta cigaba amma tsiwar nan na nan.

Amma ba ta cika fita ba kullum ta na gida sai dai fa ta yi suna sosai a Instagram kowa ya san yar gidan Nabil (Liya bae).

Kullum shi ma Abbhi ya na gidan bai cika fita aiki ba sai ya tabbatar ta ci ta ƙoshi ta na walwala sannan zai tafi office.

Bikin Liyana saura two weeks, next week za'a kawo lefenta which is idan biki ya rage one week, kuma suna ta tsara events sosai da ƙawayenta, kuma sun shirya da Sultan amma ba ta gaya masa bikin ba.

Yau dai kam she's in a good mood sosai, dan kallo ɗaya za ka mata ka ga hakan tattare da ita, ga wani gyaran jiki da ake mata, dan wata mata Mamin Hydar ta ɗauko all the way from Ethiopia, sai kuma Neneh ta ɗauko ta nan gida Maiduguri.

Wani kalan tsantsi fatar ta ta yi ga wani shegen ƙyalli da wani kafirin ƙamshi da ke tashi a jikinta.

Cikin shigarta na palazzo trousers da long sleeve shirt milk color with black stones ta sauko tare da shiga kitchen ta ɗebo fresh milk da yanzu ta zama kamar ruwan sha a wurin ta, dan ita yanzu ba ta da abincin da ya wuce fruit salads da fresh milk, sai kuma milky donut da strawberry hollandia yɗan amana dan suma ta cigaba da shan su.

Ta na zaune a falo Neneh ta sauko ta na ƙare mata kallo, cikin muryarta mai sanyi ta ce " amarya ba kya laifi dubi ga wani annuri da ke fita a tattare da ke."

" Kin ga dai dana sauko ban miki magana ba ko?, toh wallahi ban wuce da ke ba ki shiga hankalinki."

" Allah ya ba ki haƙuri yɗar nan mai ya yi zafi, kin ga daman Mansura ce da yaranta za su zo yau toh babbar yɗarta a ɗakin ki za ta sauka."

" Bana sharing."

" Kya ji da shi ai dalla gafara min can, tun da gidan na ubanki ne."

" Ai na kakanninki ne."

Ta faɗi hakan ta na cigaba da shan fruit salad ɗinta.

Ɓangaren Haidar kam tun da ya koma gidan zazzaɓi ya yi a tsai tsaye sannan ya ɗan warke, kusan kullum sai Mami ta tilasta masa ya zo wurin Liya, amma ya na fita ya ke shigewa flat ɗinsa.

Yau kam sai da ta ƙara masa magana akan ya je ya tambaye ta size na under wears ɗinta dan lefe su ke so su haɗa mata na gani na faɗa.

Yau ma bayan ta gama masa jawabin yaje ya sami Fatima, flat ɗinsa ya nufa tare da kwanciyyarsa ya kira Sultan.

Ring biyu ya ɗaga cikin muryarsa mai amo ya ce "Sultan." Shima Sultan a ɗayan ɓangaren ya ce "Yes Big Brother."

" Sultan ka na gida ne?."

" Noo bana ma Kano gaba ɗaya tun jiya ina Jigawa state."

" Okay."

Mai ya faru big brother."

" Nothing much, a dawo lafiya."

" Allah ya sa."

Katse wayar ya yi tare da dailing number Amir, sai da ya yi ring uku sannan ya ɗauka

" Hello Amir can you hear me."

" Eh I can hear you, what's wrong."

" Amir come over dan Allah , akwai matsala."

"Subhanallahi, mai ya faru?."

" Bana son shirme just come."

" Okay on my way."

After some hours Amir ya shigo ɗakin nasa.

Ajiyar zuciya ya sauke tare da ɗaukan wayarsa da ke gefensa ya miƙawa Amir.

List ɗin kayan lefe ne Mami ta tura masa almost 200 million dafe ƙirji Amir ya yi sannan ya ƙyaƙyala dariya ya ce " wallahi Mami ta min dai-dai, for almost 2 Weeks ana maganan ka kawo kuɗin lefe tun yana 100 million har sai da ta ƙara 100 million a kai, wallahi da ni za'a je ma." Ya faɗa tare da ƙara faɗaɗa dariyar na shi.

Tsaki Hydar ya ja tare da warce wayarsa daga hannunsa tare da faɗin " ni fa ba kuɗin ne damuwana ba, ka je ka biya kuɗi a yi lefe a ka wo maka wata albasa acikin gida (gajeriyya 😂😂). Buh idan ma sama da hakan suka yi requesting ai i can provide, and abin haushin ma bana son yarinyar, shi ne abin da ke bani haushi."

" Sai kaje ka ganta, dan Allah mai aka dafa am starving."

" Dalla ware can, ana maka magana mai ɓillewa kana kawo abinci, shiryawa za ka yi kaje ka tambaye ta, domin Mami ta riga ta yi booking gobe zata wuce Dubai, Please do this for me friend."

" Ba'a aikin banza a Kano nawa zaka bani,?."

" Is ten million okay for you?."

" That same 200 million is okay ai."

" Amir you're Mad."

Dariya ya kece da shi sannan ya ce su tafi tare, ko kallonsa Aliyu be yi ba ya yi hanyar toilet dan wanka ya ke son yi.

A hankali ya ƙwanƙwasa ƙofar gate ɗin gidan Neneh, bayan mai gadi ya buɗe masa ma , gaisawa kawai suka yi, sannan ya wuce cikin parlourn.

Neneh ya gani a parlour da wata matashiyyar budurwa, da take shan fruit salad ɗinta tare da daddanna wayarta, farace amma ba sosai ba, ƙarasa shigowa ya yi tare da zama akan kujera ya na gaida Nenehn.

Liyana da ke zaune cikin shigarta na kullum, da kuma normal hula ta ɗago da kanta ta kallesa sannan ta cigaba da operating wayarta because chatting ta ke da wata sabuwar ƙawar da ta yi a Instagram.

Sai da Neneh ta zolayesa sannan ya ke tambayar ina amaryar su.

Kallonsa ta yi sannan ta ce " ga ta ta na jin ka ai." Ita dai Liyana ba ta kallesu ba she countinues what she's doing with her waya.

Yarinyar ta mugun burgesa dan Amir akwai son ƙyale - ƙyale.

A hankali Neneh ta ce " Liyana kike ko Libiya, ta shi ki ɗebowa baƙo kayan motsa baki."

Ba ta yi magana ba ta shiga kitchen tare kawo masa abin da ya kamata tare da komawa wurin da ta ke ta zauna.

Shi kam Amir shape ɗinta kawai ya ke bi da look.

Dan yarinyar is damn beautiful.

Babu ƙarya Hydar ya yi dace.

Ruwa kawai ya sha tare da kallon Nenehn ya ce " wurin amaryarmu fa na zo."

" Toh ai shikenan, bari na baku wuri."

Bayan Neneh ta tafi kallon Liyana ya yi tare da faɗin " Amaryar mu."

For the first time ta ɗago ta kallesa sannan a hankali ta cigaba da danna wayarta tare da faɗin " call me Liya or Fatima."

" Am sorry."

" Never mind."

"Hydar ne ya aiko ni akan under wears sizes ɗinki."

" Mai ya hanasa zuwa da kansa? Tell him to come, ba wani ba."

Har ta tashi zata tafi sannan a hankali ya ce " baya gari ne and ni ne P.A ɗinsa, Kuma ba undies ɗin bane ba kaɗai ya kawo ni har da events da za kiyi."

A hankali ta dawo ta zauna tare da kallon ƙwayar idonsa ta gaya mai bra size and the rest. Sai kuma cikin sanyin muryarta ta ce " Akwai ladies party, Shuwa Arabi day, Al Qur'an day, Father's day, mother's day, sister's day, dinner, madrid lover's day,then after ɗaurin aure zamu je shan ice cream da friends ɗina."

"Your wish will be granted in shaa Allah, daga haka ya yi hanyar fita daga gidan.

Kuka Liyana ta fashe da shi dan yanzu wani kalar kewan kowa ta ke ji, abin da ya kawo ta gidan Nenehn ma ba ta yi ba an jogana mata aure.

Ta na cikin kukan Neneh ta ƙaraso ta ce " ke kullum cikin kuka, kamar zuma rock?."

" Tun da hawayen ki ne sai ki zo ki hana ni."

" Mara kunya."

" Naji."

Amir na zuwa gida ya wassafawa Hydar komai, cikin muryarsa ya ce " Alhaji ka gama dace, You see shape?, sai ka ganta, Man wallahi ka yi dace, ka ga wani command da ta bani, je ka turo sa ya zo da kansa, she's a boss lady ooo." ya faɗa tare da buɗe fridge tare da ƙara faɗin"Man wallahi tun da baka sonta ni ka barmin ita, sai ma ka kalli curved shape ɗinta anan zaka san defination of full option, wallahi su Mami ba zaka san sun maka gata ba sai nan gaba, wallahi ka hanzarta, ka tura kuɗin lefen nan, wallahi dan ko one billion ka tura a mata siyayya ba ka faɗi ba, kai kaga flat tumm....."

Bai barsa ya ƙarasa ba ya ce" Ya kuma ishe ka haka." " Buh I thought ka ce ba ka sonta?." " Dan Bana son nata ai yanzu ƙoƙarin zama matata take, suffanta ta ya yi haka."

" Allah ya baka haƙuri, daga ɗan magana, wallahi abin sai ka gani k..."

Tashi ya yi ya bar masa ɗakin ya koma parlour.

Binsa Amir ya yi ya ce " idan ka faɗa fa Man za'a yi iskanci." Danne - dannensa ya cigaba da yi, bai kallesa ba sai da Amir ya ɗan leƙo da kansa ya wani zare ido ya ce "Hydar dey fear God, yanzu baka son nata ka tura 500 million?, half of a billion fa kenan?."

" And so?." Daga haka ya tashi ya nufi flat ɗin Mami dan ya na ganin kiranta .....✍

> PENDING AMARYA AS USUAL FOLLOW FOR MORE

> PENDING AMARYA'S BOOK CORNER EXTRAORDINARY EVERYDAY POSTING LINK

https://whatsapp.com/channel/0029VbAyucH7j6g0IDCpPi2V

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.□

The Noble Writters □

Dedication is Our Strong □

Alhamdulillah The Regret Book Two Activated □

This page is dedicated to you My Rufy

Pending Queen Nigeria limited.

Ina yin ki ta Rafiƙ□😆

_ Pending Amarya 23 _

Not edited.

Binsa Amir ya yi ya ce " idan ka faɗa fa Man za'a yi iskanci." Danne - dannensa ya cigaba da yi, bai kallesa ba sai da Amir ya ɗan leƙo da kansa ya wani zare ido ya ce "Hydar dey fear God, yanzu baka son nata ka tura 500 million?, half of a billion fa kenan?."

" And so?." Daga haka ya tashi ya nufi flat ɗin Mami dan ya na ganin kiranta .....

Ko da ya ƙarasa Ɓangaren Mamin, kallonsa kawai take sannan a hankali ta ce ''Papa na ga alert, and you didn't tell me size na bra ɗinta, that's not even what we expect, Muna godiya.''

a hankali ya ɗago kansa tare da kallon Amir ya na mai alamar ya yi magana.

Amir ɗauke kansa ya yi kamar bai gansa ba ya ci gaba da yiwa Sultana magana ta kawo masa abincinsa.

Cikin inda-inda ya ce ''Mami i think ba zai wuce, 38 ba a yadda na gani.''

''So tell me da kaje ka ga yarinyar ka yiwa kanka adalci ba ta yi maka matsayin house wife ba fisabilillahi.''

''Mami ta yi.''

''Ba na zaɓin banza ai, nawa ma kace size ɗin nata?."

''38 Maa.''

''I got the right dimension kenan ma, da ni da Sakinat za muje, tun da yau sunday duk in da Friday take muna hanyar dawowa.''

Adawo lafiya suka yi mata sannan suka fita daga side ɗinta gaba ɗaya.

Side ɗin Liyana kuwa tun da Amir ya bar gidan take ta banka uwar tsaki, ko kallon Nenehn da keta waya da drivers aje a ɗauko mata baƙinta daga airport ba ta yi dan already yanzu yamma ya riga da ya yi, ko ina na gidan ya ɗauki ƙamshi mai daɗin gaske.

Arround seven o clock, su Aunty Mansura suka ƙaraso gidan ita da yaranta yammata biyu duk sa'annin Liyana, kyawawa ne sosai kuma kallo ɗaya zaka musu ka san da cewa money dey talk a tattare dasu wadda ke zaune kusa da Neneh, cikin shigarta na pencil jeens brush trousers sai orange polo da white viel ta kalli Nenehn cikin sanyin muryarta ta ce ''Neneh where's the bride, ina son ganinta, mu fara preparations na bikin since we are all ƙawayenta duk da is our first meet.''

Wadda ke kusa da Aunty Mansura ce ta ce ''Rashanda(Rashidat) kina da problem, we are the visitors here ya kamata ace ita zata zo ta gaida mu, bana son wannan halin shishshigin naki.''

''Oh mine Faridat, just understand something about life, ba shishshigi bane ba.''

''sai ki ci gaba ai.''

Liyana ce ta shigo cikin gidan dan tun ɗazu ta na garden, cikin shigarta na wani combat na mata da ya ƙarawa skin nata haske, wani big polo da saura kaɗan ya rufe combat ɗin ne ajikinta, sai kuma slippers ɗinta, dan yau bandana ta saka a kitson ƙanana da aka mata, ga ear plugs ɗinta manne a kunnenta.

Ba ta ma lura da mutane a living room ɗin ba ta na tafiya ta na jin waƙar Ayra star dai-dai wurin da ake faɗin _Me no get the time for the haters and bad energy, cus I mind on my money, make you dance like bracolli steady green like raccoli_.

Rashanda ce ta wani firfito da ido tare da faɗin ''Besty yar gidan Nabil.'' bata ma ji ana kiranta ba dan she's busy chatting with Sultan, ga kuma waƙan da take ji,

A dinning area taje ta yi zamanta wanda hakan ya bawa Salimah daman kawo mata strawberry hollandia ɗinta.

Ba ki kawai Mansura ta saki because bata taɓa tunanin abin har ya kai serious haka ba yadda Neneh ke gaya mata banbancin Liyana da Christian sallar asuba.

Ear plugs ɗin ta cire tare da shiga Instagram because she's chatting with Sandy rash sannan ta shigo cikin gidan ɗazu.

Message ɗinta ta karanta ''Mun sauka a Nigeria, gobe zan zo gidanku in shaa Allah.''

She smiled, sannan ta yi mata ya gajiya ta cigaba da karanta comments da mutane suke wa pictures ɗinta da tayi post ɗazu a garden.

''Fatima.''

A hankali ta juyo dan jin muryar Umma da tayi kusan shekara goma sha biyu ba ta ji ba sannan ba ta ganta ba.

Haɗa ido da suka yi da Umma Mansura shi ya ba ta daman wara ido tare da facali da kujerar dinning room ɗin ta shige jikin ummar da gudu.

''Umma Neneh ba ta gaya min za ki zo ba.''

''Amarya naji kar ki karya ni.'' ita duk shagalinta ba ta san ma da wasu a duniya ba.

Sai da ta gama rungumar Umman sannan ta ɗago ta kalli cikin falon.

Kurawa Rashidat ido ta yi sannan a hankali ta ce " Sandy is that you?. Murmushin ta mai kyau Sandy ta sakar mata sannan ta ce ''Yeah.'' ''Welcome then.'' tsakin da aka saki a falon shi ya bata daman ɗagowa ta kalli falon wata black beauty ke zaune cikin shigarta na abaya white and golden.

A hankali Liya ta ce ''Who's she?."

''Classy Reeda ta I.G ce.'' a taƙaice Rashida ta bata amsa.

''She's welcome then, buh next time a gaya mata gidan nan ba'a tsaki.''

Daga haka ta fice daga palon.

Da yamma arround nine o clock Abbhi ya kawo mata ice cream, ta sha sosai because a garden suka zauna yau ɗin.

Sai wurin ten O clock sannan ya koma gida.

Ko da ta shigo cikin gidan ko kallon Classy Reeda ba ta yi ba, da Sandy Rash ta takurata da wedding preparations kuwa ce mata ta yi kawai ta hau I.G suyi chat dan ba ta gayyatan ko wani local zuwa bikinta.

Classy ba ta tanka mata ba, kawai chat ɗinta take yi dan ta san yar gidan Nabil da rashin mutunci tun a media ma ba ragawa kowa take ba balle a reality.

Haka suka ci gaba da rayuwa agidan kullum Umma Mansura cikin ɗurawa Liyana magunguna take ga wanda masu gyaran jiki ke bata, kuma maganin na ɗan bata matsala sosai dan za'a iya cewa ya mata yawa a jiki.

After some days

Yau Mami ta dawo daga Dubai da ita da Sakinat, akwatuna ne na gani na faɗa babu wanda zai gani ya ce kuɗi bai yi magana ba.

On Wednesday su Mami suka dawo da daddare, sai washegarin ranar mutane suka zo kallon lefe kafin a kai gidan Nenehn.

Mutanen Ilorin ma da na ibadan danginsu Mami kenan tun ranar tuesday suka fara zuwa gidan, sai kuma dangin Alhaji Kyari mutanen Borno su ma sun ɗan fara zuwa , amma na Ilorin ɗin sun fi yawa.

A kwana a tashi asarar mai rai hausawa kan faɗa yau friday yau ne za'a kawo lefen Liyana tun safe ake ta gyare-gyaren gidan ga snacks kala kala, ginger juice, kunun aya abinci kala kala.

Ƙamshin turare kala kala na ta tashi ga su Ilham da classy Reeda da Sandy Rash har da Lilian sun yi kwalliya mai kyau ga jeran kumbo a ƙasan falon da duk an jera, ga wani traditional Decorations da yayi mugun kyau.

Suna zaune akan kumbon jikin su sanye da lifaya mai kyau ga kaskon turaren wuta shima a gabonsu.

Three o clock dai-dai a ka fara jin parking na motoci, langa Neneh ta sa aka ɗauko aka fara kiɗa ana waƙan Kanuri har ma da Shuwa Arabi Rufaidhat na nan Ikimat ma haka, sannan rabin yan uwansu na Maiduguri duk sun zo.

Kiɗa ake sosai, Sultana ce ta fara shigowa da wani akwati sannan sauran suka fara shigowa da shi, tun suna iya ƙirgawa har suka gaji suka daina.

Thirty six pieces of akwati designers babu fake.

Bayan an gama entertaining ɗinsu, sannan aka fara buɗe kaya.

Atamfofi kam sam babu na wasa atamfar holland ita ce mafi ƙanƙantar kuɗi a cikin su.

Atamfofi sai da aka ƙirga sama da two hundred pieces Dan kusan akwati goma suka yi occupying.

Less da materials kuwa luxury organza shine kaɗai mafi ƙanƙantar kuɗi a ciki shima ba da Naira ba da Euro.

Hand bags da takalma kuwa daga CHANNEL, DIOR, LV, VERSACE, GUCCI, BALENCIAGA. Duk babu na yardarwa.

Wata dalleliyyar Iphone wadda ta fi ko wacce tsada a duniya, FALCON SUPERNOVA PINK DIAMOND IPHONE, it's aka zaro dalleliya mai kyaun gaske.

Akwati guda ɗaya kuwa cike yake da palazzo trousers, dayan kuma different styles of tops ne a ciki.

Sai kuma wani akwati mai bin wani babban akwati dake cike da juweries, tun daga kan zicon, da golds sai diamonds sai kuma wasu beeds juweries da suka biya India aka siyo su ma tsadar su yayi over.

Kayan man shafawa kam babu wanda ba daga Oriflame ba tun daga turaruka roll on, face mask on, dama lipstick babu abinda babu.

Lefen Liyana ya gama haɗuwa over, Alhaji ƙwarya ta bi ƙwarya ya yi a rayuwa. Mai kuɗi ya auri mai kuɗi, talaka ya auri talaka, maraya ya auri marainiyyar Allah.

My sister no confuse your self.

An gama kallon lefen wanda shima ba duka a ka buɗe ba dan mayarwa wani yaƙi ne.

An bada tukwicin lefe twenty million naira cash not transfer.

Irinsu Sandy Rash da Classy Reeda sai posting ake for more followers. Ko ina ka shiga maganar lefen yar gidan Nabil ake, Arewa rich kids an ɗaura, Abis fulani ma ya fara sharhinsa akai.

An ci an sha an watse an gyara komai da dare kamar ba'a yi ba, kowa sai jinjina maganar lefen yake.

Bayan Abbhi ma yazo zama ya yi shi da mutanen gidan aka dasa hira. Liyana da ta fito fuskarta duk a kumbure wanda alamu ya nuna kuka ta sha.

Zama tayi kusa da Abhinta ta sa kanta a kafaɗarsa tana kallon videos ɗin da in less than two hours ya zama viral.

Neneh ce ta ɗago daga zaunen da take ta ce '' Yanzu dan Allah ki duba uban lefen da aka haɗa miki kamar za ki buɗe plaza, duk kuɗin plaza da ubanki ya ce ya buɗe ai bai kai kuɗin wannan ba.''

''Ni lefen ba su min ba ma yar tsohuwa.''

Kallonta kawai Neneh ta yi dan ba ta da ta cewa.

A hankali Abbhi ya shafa kanta tare da faɗin ''Babyn Abbhi kan ki ya tsufa da yawa kuma ke yanzu amarya ce ya kamata ace kin fara gyara kanki ko?."

''Abbhii.'' ''Naam yar Abbhinta.''

''Take me out please ina son naga gari it has been a while.''

''Okay, ba yau za ki kai ɗinki ba?."

" That's why I love you Abbhi, dan wallahi na manta.''

''It's alright muje na zaɓar miki, wanda za ki kai ɗin.''

Tashi tayi tare da barin wurin ta na bankawa Classy harara.

''Tsohuwar manya ina lefen nawa?."

" Gashi na ɗaure a kaina a jikin gashi na ya na lilo.''

''kya ji da shi, ai na kusa bar miki gidan ki cinye.''

''Lily, Sandy where are my stuffs.''

Cikin sanyin murya Sandy ta ce ''Suna wancan abandond room ɗin na ƙarƙashin stairs.''

Ko da ta shiga ɗakin zaɓo kayan da zata saka ranakun ta yi sannan ta ɗauko trolly a ɗakinta haɗe da wani trolly wan da ta daɗe da siyan anko's na ƙawayenta.

Sun yi murna sosai sannan suka wuce Abbhi na driving Liya a gaba, sai Lily da Ilham a baya, sai kuma Sandy da Classy duka suma duk a bayan.

A hanyan dawowa ma ta wani wurin shan ice cream suka biyo.

''Abbhi please ka tsaya anan.''

''Okay Maa.''

Sauka suka yi Abbhi na riƙe da hannunta suma sauran suka mara masu baya, bayan an bata ice cream ɗin ta babbawa kowannensu sannan ita ma aka bata nata, Abbhi ta ga ni ya bar kusa da ita ya na tsaye kusa da wani mutum dake tsaye da wasu yammata wanda alamu sun nuna gaisa yake da mutumin.

Ita kawai so ta ke ta nunawa Abbhin ta samu strawberry ice cream da ta daɗe bata sha ba wan da ba ta wani lura da mutanen dake ɗan cunkoso a wurin, wata

matashiyyar budurwa ce ta ɗan bige ta ta yi baya zata faɗi wanda hakan yasa ta rufe idanunta gamm, har ta sadaƙar zata faɗi sannan ta jita ajikin wani faffaɗen ƙirji, Ƙamshin turarensa na Armani Georgia haɗe da Valentino da Baccarat duk sun cika mata hanci wanda a hankali ta fara buɗe lumsassun idanunta tare da sauke su akanta.....''

Pending Amarya as usual muje zuwa.....

> KAR KUJI HAUSHI NA SABODA RASHIN UPDATE KOMAI A HANKALI NAKE BI BANA RUSHING😭😭

> PENDING AMARYA'S BOOK CORNER EXTRAORDINARY EVERYDAY

https://whatsapp.com/channel/0029VbAyucH7j6g0IDCpPi2V

THE REGRET

(Dana sani).

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.

The Noble Writters

Dedication is Our Strong

_ Pending Amarya 24 _

Ita kawai so ta ke ta nunawa Abbhin ta samu strawberry ice cream da ta daƈe bata sha ba wan da ba ta wani lura da mutanen dake ɗan cunkoso a wurin, wata matashiyyar budurwa ce ta ɗan bige ta ta yi baya zata faɗi wanda hakan yasa ta rufe idanunta gamm, har ta sadaƙar zata faɗi sannan ta jita ajikin wani faffaƈen ƙirji, Ƙamshin turarensa na Armani Georgia haƈe da Valentino da Baccarat duk sun cika mata hanci wanda a hankali ta fara buƈe lumsassun idanunta tare da sauke su akanta.....''

Wani kalar waro ido ta yi tare da ɗaure fuskar ta a lokaci ɗaya, shi ma ganinta da ya yi ba ƙaramin ɓata masa rai ya yi, sun kalli fuskar su na some seconds sannan a hankali ya sake ta ta faɗi a ƙasan wurin, wani ɗan ƙara ta saki wanda hakan ya sa attention na wasu daga cikin mutanen ya ɗan dawo kansu.

Ficewa ya yi daga wurin gaba ɗaya, Liyana kam a hankali ta tashi tare da kakkaɓe jikinta, Sandy ce ta zo kusa da ita tare da ce mata sannu tare da kamo hannunta.

Fincikewa ta yi tare da dalla musu harara, har ta ƙarasa wurin Abbhin.

Ta na ɗan ɗingisawa, sannan a hankali ta kamo hannunsa a cikin nata.

Juyowa ya yi tare da yin sallama da Dr Hafiz, hawayen da ya gani shaɓe shaɓe a kan kuncinta yake bi da kallon mamaki, sannan a hankali ya ce ''Day maker what's wrong?." Cikin Wani kalar marayan murya ta ce ''Abbhii.'' tare da fashewa da kuka dan daman a jogane take.

''Subhanallahi daughter mai aka miki?, wani acikin ku ya mata wani magana ne?." Ya faɗa tare da kallon su Ilham.

''Mun ganta a ƙasa mu bamu san mai ya faru ba ma.'' Classy Reeda ta faɗa tare da ƙafe Liyanar da eyes.

Abbhin bai ce komai ba kawai ya ɗauke ta suka mara mai baya sannan suka ɗauki hanyar gida.

A motar ma wani kalan kuka take wanda ita kaɗai ta san na menene.

Bayan sun zo gidan ma a ɗakin da yake masu yanzu ya ajiyeta.

Kallonsa ta yi tare da faɗin ''Abbhi ba zaka min tsifan ba?.'' ''Babyn Abbhi dare ya yi kiyi bacci da sassafe zan zo na miki tsifan sannan muje saloon ɗin da ake miki kitso kin ji?." Gyaɗa kanta ta yi kamar sokuwa, sannan a hankali taja duvet ta rufe iya ƙafarta ta na duba wani ɗan saƙo da Sultan ya turo mata wani ɗan video ne nasu a mota, ba zata manta ranar ba hijab ne jalibab a jikinta black color da ya amshi fatarta _"Did you remember this day."_ shi ne abin da ya rubuta a ƙasan videon .

A hankali ta yi clicking tare da fara kallo, wani biscuits ne a hannunsa chocolate biscuits mai tsada ne sosai, ta ce ya bata ya ƙi ba ta shi ne ta fara mai waƙan Fire boy Dml ta na faɗin _" if I leave you nah you I go run back to, I go run back to you, e sure for you baby am going no where, your love is true I know you will always be there, no one could love you like I do no body……_

Dariya ya yi sosai a videon sannan ya ce ''Na wash yaudara ne wallahi.''

Cikin muryarta na sakalci ta ce ''Kaiiiii."

''Toh ga shi kina faɗin No one could love me like you do, ina kika bar Mami da Abbuh?."

''Toh na ce ka yi comparing da wannan soyayyar ni dan Allah ka bani biscuits ɗin yawu na ya tsinke.''

''I No dey give.''

''Please.''

''za ki iya aure ki barni ita kuma Mami ba zata iya barina ba.''

''Kai kullum cikin negative vibes kake, why?." Ta ƙarashe maganar kamar zata yi kuka.

''That's the reality.''

''Toh ni bana son reality ɗin bani biscuits.''

Bai mata magana ba ya ci gaba da ci, a hankali ta fakaice shi ta wawushi na hannun sa ta lunƙume a baki, a haka sukai ta kokawa, then at the end she had her first kiss a wurinsa anan kuma videon ya yi cut.

Cilli ta yi da wayan tare da fashewa da kuka, why THE HEART BREAK this is BEYOND HEART BREAK wannan ya fi karayar zuciya.

ta raini son shi for almost 3years yanzu kuma ace wani zata aura, aranar dai Liyana kasa bacci ta yi tunanin Sultan yaƙi barin ƙwaƙwalwarta.

Tun su Ilham na rarrashi har suka tattara suka rabu da ita.

Washegarin ranar da ta tashi fuskarta a kumbure, ta yi jaa sosai, bayan sun gama breakfast Tun da kusan kowa na gidan dan su Ammi ma basu koma ba, arround 10 O'clock Abbhi ya zo bayan sun gaisa, ya zauna ya na yiwa Liyanar tsifa.

Wuraren biyu kuwa ya wuce office, Liyana ita dasu Sandy ne suka tafi aka yi mata washing and setting, sai yamma liƙis suka dawo gida, dan ba kitso zata yi ba.

Huge hair ɗinta a pake duk ana zaune a na ta hira.

Suna daga zazzunen suka ji sallama, cikin wani kalar siririyar murya, Rashanda da Classy Reeda suka ta shi a million, suna rungume wannan yar matashiyyar budurwar da ta shigo, tsayinsu zai zo ɗaya da Liyana amma tafi Liyana kawrin jiki.

''Hey cousin sisters karku karya ni manaaa.'' (shegen iyayi 😊😂).

''Babu maganar karyawa we really miss you mis chubie.'' duka suka haɗa baki wurin faɗa.

Cikin falon suka ƙarasa aka yi ta hira da ita ita ma Liyana ta ajiye girman kai aka fara hira da ita amma still ba ta gane wacece ba. A hankali ta ce ''Sandy please can I know her more.'' a hankali Sandy ta ce ''ai sunan mamanta kika ci gado yar yayan Uncle ce da ta rasu (Abbhi).

''Okay na gane Allah ya jiƙan musulmai.'' ''Ameen suka amsa gaba ɗaya.''

Washegari da sassafe suka kama hanyar zuwa legal dan acan za'a yi lallen lallen, Liyana ya yi maroon sosai sannan ya yi kyau dukkannin su yayi kyau amma na Liya yafi.

On monday za'a fara events, da ball za'a fara a _La Sultanah_ za'a yi events ɗin REAL MADRID LOVER'S.

Tun safiyar ranar aka fara shiri. Liyana kam wani dakakken Palazzo trousers jeens ta saka sai rigan Madrid, daga ganinsa zaka san mai mugun tsada ne all the way from Switzerland.

Sannan ta ɗaura wani black jacket mai ɗan laushi mai kama da water jacket akai an rubuta _The Bride_ sai kuma farin booth, sai kuma ta ɗauki wayarta ƙirar iphone fourteen promax.

Jersey veil ta yana tare da ɗaura wani butterfly sun shade mai mahaukacin kyau.

Dukknnin su kayan Madrid ne amma na Liyana ko a ido yafi tsada.

Lilian ma ta yi kyau sosai.

Sultana ce ta zo ƙanwar Aliyu da sauran cousins ɗin Aliyun suka nufi wurin taron arround six pm.

Suna kallon ball suna nishaɗi, sannan suma suka shigo cikin stadium ɗin suna ball suna rawa, wani waƙan Madrid fan na wannan mawaƙin _Elikia_ waƙar _Mentality_ .

She's very happy a ranar duk wani damuwarta nemansa ta yi ta rasa, saboda Liyana ba sai na faɗa ba gwana ce a wurin sharholiyya.

Sai ƙarfe goma suka dawo gidan, duk sun gaji wanka suka yi kawai suka kwanta bacci dan gobe shima akwai events.

Ɓangaren Hydar kuwa tun ranar da Maminsu ta dawo ma da aka nuna mai lefen bai wani react ba kawai ya dai yi murmushi sannan ya bar living room ɗin dake jibge da boxes ɗin.

Ya wani cire damuwa a ranshi ya sa business a gaba.

Da yanzu ma ya na China Abbuh ne ya hana sa.

Bayan an kai lefen ma sai da aka cajesa kuɗin ɗinki two million sannan hankalinsu ya kwanta.

Sam babu wanda ya damu da shi ba ga dangin Mami ba ba ga dangin Abbuhn ba.

Kullum ya kanje ya sha yawonsa kafin ya dawo gida, ranar ma wani tsautsayi ya sa shi ya ji yana sha'awar zuwa shawarma zone yaci shawarma with ice cream, ranar kam sai da ya haɗu da bad luck ɗinsa acewarsa Liyana is a bad luck to him.

Lamarin Amir kam wurin zolayarsa ƙara gaba take yi, kullum cikin maganar shape ɗin Liyana yake shi kam abin na mugun ɓata masa rai ba kaɗan ba.

Ranar Monday arround 11pm Sultana ta shigo ɗakinsa bayan sun dawo daga La Sultanah ta ce ''Yaya sannu da hutawa, wallahi your wife is very beautiful, Kai ka ganta kuwa santaleliyya wallahi ka iya zaɓe, ta yaya ma ka ganta har ka gayawa su Abbuh, abeg gist me, ni is like na taɓa ganin ta sau ɗaya a school.'' haka tai ta surutu.

Bai mata magana ba ya zaro slippers ɗin ƙafarsa sannan ya saita bakinta ji kake buff.

''Wayyo Yaya daga magana.''

Tashi ya yi tare da ajiye laptop ɗinsa ya sakar mata ranƙwashi, ''wayyo kaina.'' wani ya ƙara sakar mata, sannan ya ce ''Duk magana ɗaya idan kika ƙara sai kin gane kuren ki.''

''Am sorry Yaya.'' yatsunsa na tsakiyya da na ƙarshe ya haɗe su tare da ɓalle mata baki sannan ya ce ''Not even sorry, motsi kika yi yau sai kinga ribar gulma. ''Yaya buh k.....'' ɓalle mata baki ya sake yi.

Sultana kan data ga abin na zalunci ne yau da gudu ta tattara wandonta ta bar ɗakin.

Ajiyar zuciya ya sauke sannan a hankali ya cigaba da nazarin laptop ɗin da ke gabansa.

Amma tunanin yarinyar ya ƙi barin brain ɗinsa, wani iska mai zafi ta furzar haɗe da ajiye laptop ɗin yana focusing akan chatting ɗinsa da Amir.....

> GUYS SALO YA CANZA KUMA SAI KU CANZA ZAMA □□

THE REGRET

(Dana sani).

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.□

The Noble Writters □

Dedication is Our Strong □

_ Pending Amarya 25_

Ajiyar zuciya ya sauke sannan a hankali ya cigaba da nazarin laptop ɗin da ke gabansa.

Amma tunanin yarinyar ya ƙi barin brain ɗinsa, wani iska mai zafi ta furzar haɗe da ajiye laptop ɗin yana focusing akan chatting ɗinsa da Amir.....

Washegarin ranar za'a yi Lifaya day wato shuwa Arabi day, tun safe aka fara shiri, abinci kala kala babu wanda zaka nema ka rasa abin dai sai wanda ya gani.

Shima dai a Leena event center za'a yi, dan Jiddah ne ya ce baya son a tsawwalawa bidi'a da yawa albarka kawai ake nema.

Da yamma misalin ƙarfe shida aka fara harraman zuwa can wurin occasion ɗin.

Liyana ce cikin wani kalan dakakken lifaya da kuɗinsa kaɗai sai ya cire mutum daga talauci na wucin gadi.

Lifayar fari ne ƙal sai stones golden color da aka yi mai wani kalar classic design, sai wani kalar gucci hills da ya ƙarawa shigarta kyau, sai gashinta da aka yi mata kitson gaba ƙato gudan ɗaya, tun kafin ka iso kusa da ita zaka ji sanyayyar ƙamshin turaren nata ya fara maka marhaban.

A hankali wasu tsofi guda biyu suka kamata suka saka ta acikin motar da na musamman Abbhi ya siyo dan kai ta wurin events ɗin nata.

In ban da rawan Al ragaba (rawan wuya)babu abin da suke yi suna yi suna cilli da hannu, ga kuma turaren wuta a ɗayan hannun ya na tashi a hall ɗin.

Ko ina waƙan Roua Na'eem ke ta shi waƙar nan nata mai taken _Habibi_.

Anci an sha sannan aka dawo gida, shi ma duk jikanta a gajiye, da daddare misalin ƙarfe 11, yunwa ke nuƙurƙusan cikinta hakan ya bata daman fitowa kitchen dan samawa cikinta abin da zata ci.

Bayan ta shiga kitchen ɗin ma Pepe soup ɗin kan rago ta gani an ɗan buɗe shi ya sha iska Dan kar ya lalace, shi ta ɗiba tare da bread ɗin da ta gani saman toaster, ta shigo ɗakin ta na ci idanunta a lumshe saboda bacci take ji sosai.

Da haka har ta gama ci ta wuce ta kwanta a tsakiyar su Unaisa (mis chubie).

Washegari ma da sassafe, mutanen gidan suka fara hada -hada amma ita Liyana sai da ta korawa kowa jawabin kar wanda ya tashe ta.

Da yamma aka yi mother's day, Liyana cikin wani dakakken Abaya duk ya ji stones masu kyau sosai, mother's day ɗin dai a compound ɗin gidan akayi inda aka kira wannan mawaƙin boys kiddo ya waƙe Ammi da wannan waƙar na shi na Mama.

Haka Liyana da Ilham suka rungume Ammi suna ta kuka har aka tashi daga taron.

Da daddare ma hira suka ɗinga yi a tsakanin su, wanda Liyana babu zato babu tsammani ta fashe da kukan da bata san dalilin sa ba.

Su Classy Reeda da Sandy Rash da Mis chubie har da Lily suka yi ta bata baki har tayi shiru bacci ya kwashe ta.

Ko da Abbhi ya shigo da ya tambayi Liyanar cewa aka yi bacci take yi.

Bai sa an tashe ta ba ya wuce ya koma Hotoro.

Washegarin ranar aka yi Father's day, idan kaga Abbhi da Liyana sai ka rantse shi ne zai aureta, baƙin yard ya saka itama wani baƙin material da aka yi mata ɗinkin corset gown, da ya bi shape ɗinta ya lafe.

She looks hot sosai, haka suka yi ta rawa da ƙawayenta Abbhi na mata liƙi.

Ta yiwa Abbhi baitoci sosai sannan aka tashi daga event ɗin Abbhi ya maida ta gida sannan shima ya koma Hotoro.

Washegarin ranar aka yi sisters day duk sunyi kyau sosai cikin shigar su na abaya's, anyi games da dama.

Rana bata ƙarya yau ne kamu wanda aka gayyaci manya -manyan malaman Musulunci, irinsu sheik Tijjani Guruntum da ma sauran malamai irinsu sheik Gadon ƙaya.

Anyi wa Liyana wa'azi sosai akan haƙƙoƙin miji da ma sauransu, jikinta duk a sanyaye yake ta sha kuka bayan taro ya watse sosai, rayuwarta kawai take tunawa bayan auren nan ko ya zata kasance? Ko ya mijinta yake?. Wani kukan ta fashe da shi mai tsuma zuciya.

Tun jiya ma kiran Sultan take amma shegen yaƙi ɗagawa. Tsaki taja haɗe da yaye gadon data kwanta ta shige toilet haɗe da yin wanka da ruwan turarenta dan bacci take ji.

Ko ina kuma a social media maganar bikinta ake har jira ake aga ta hau online, shi yasa ma wayar ajiyesa tayi a gefe data ga zai takurata, dan yan comment section har izgili suke mata, har yau basu ga mijin Aunty Carrier ba. Dan a cikin followers ɗinta akwai masu ce mata Aunty Carrier. (Ko mai sa oho).

Rana bata ƙarya sai dai Uwar ɗiya taji kunya yau Sunday ranar da dumbum jama'a ke ƙoƙarin shaida wannan babban rana ga Fatima Nabil Aliyu Ibrahim Shuwa Arabi da kuma Aliyu Ahmad Qassim Kyari.

Ƙarfe goma dai-dai aka ɗaura aurensu akan Sadaki Naira Dubu ɗari biyar lakadan ba ajalan ba.

A take street ɗin ya ɗauki busawar Algaita, da kuma hayaniyar jama'a.

Amir ne kaɗai ke ta washe baki kamar shine angon.

Bayan labarin auren ma yaje masa ji ya ɗinga yi tamkar ya zunduma ihu.

Dan Amir yasa yaje ya masa leƙe, bayan auren kam, Sultan da Amir ne a parlourn Hydar suna ta kallon yadda yake ta huci kamar wani zaki.

Amir ne ya yi gyaran murya tare da faɗin ''dama tashi kayi ka shirya da ya fiye maka wannan fake emotions ɗin naka dan class mates ɗinmu babu wanda ban gayyato ba.''

Sultan ya amshe da faɗin ''Ko kai ma ka faɗa Amir, da ni ne ake min maganar anyi min mata ajiye wadda muke soyayya da ita zan yi a gefe in amsa hannu bibbiyu daga ƙarshe na ƙaro ta ana biyu.''

''Shege.'' Amir ya faɗa da ɗan barkwanci.

Bai ma kallesu ba balle su saka ran amsa ya cigaba da danna wayarsa.

Ɓangaren Amarya Liyana kuwa tun da taji an ɗaura zuciyarta ke duka uku³ ta rasa yadda zata yi.

Kuka zata yi ko dariya bata sani ba.

Wani mahaukacin shadda da ya lalace da ɗinki ta saka wanda alamun kayan ma kaɗai kasan ba ƙaramin shadda bane sannan ba ƙaramin tailor ne ya ɗinka sa ba.

Ɗinkin yafi kama da na ƙasar Gambia dan aɗinke yake a cikin lefenta.

Shaddar milk color ne sai aka yi design da coffee color thread, sai aka yi mai ruwan stones, sai kuma wani coffee heels dan sam bata sa ka zani ba kamar sauran amare.

Duk da ba kwalliya tayi ba, amma wannan hasken na amare ya karaɗe fuskarta, duk ɗakinta ayarin cousins ne and all of them are very classy.

Rashanda da Classy Reeda da Unaisa da Ilham sun saka kaya kala ɗaya har da Lily.

Farinciki a wurin Ammi baya misaltuwa, ta aurar da headache ɗinta a rayuwa.

Rufaidhat kam ranta a ɓace yake yadda ta ga kowa ya yi banza da ita.

Kamar mayu sai da suka je shan ice cream ɗin, dan Liyana ma bata ci komai ba sai ice cream ɗin data sha.

Misalin ƙarfe shida na yamma Aka yi mata wanka da ruwan lalle sai da aka ƙara dafa ta, sannan aka sa mata wani lifaya purple color da ratsin white color aka saka mata sai da aka turara mata jiki gaba ɗaya sannan aka kaita wurin Jiddah ya mata Nasiha, ita ma Neneh aka kai ta ta mata tare da faɗin ''Ni dai Fatima aure ne an riga an miki rashin kunya, da waƙe -waƙe sai ki ajiye tun da dai Davido ba ƙanin ubanki ba ne ba, in kunne ya ji jiki ya tsira daga azabar Allah, akai ta wurin Salamatu ta ja mata Aya.''

Sai da Liyana ta ɗage abin lifayar ta dallawa Nenehn harara, wadda ta cigaba da surutun ta.

Daman ta saba kiran Ammi da Salamatuh that's why kawai wurin Ammi aka kai Liyanar, ita dai Addu'a ta mata tare da mata fatan samun daidaito a rayuwarta ba ki ɗaya.

Daga haka aka kaita wurin Abbhi.

Rungume shi ta yi ta na kuka shima bai san lokacin da ya fashe da kukan ba dan har ga Allah ba zai iya zama bai ga ɗiyarsa ba ace har sai wani ya bata izni yanzu akansa.

''Don't worry dear every friday zan ɗinga zuwa ganin ki okay?." Gyaɗa kanta kawai ta yi sannan aka wuce da ita gidan su Mami sai da suka samu tarba mai kyau, itama Mamin ta mata nasiha sannan aka ɗauki hanyar sharaɗa da ita dan acan gidan Hydar ɗin yake.

Duk ƙawayenta da kuma yan uwanta na jiki sai bayan one week zasu koma gidan Neneh dan al'adar su ce hakan, wanda a yaren shuwa Arabi muke kiransa da Sabbayats.

Ko kaɗan bata daina kukan ba haka tai ta kukanta su Reeda da Unaisa na rarrashinta.

A haka har ta daina kukan.

Daga ƙarshe ma dai ta ware suka cigaba da hira tun suna jiran angwaye har suka kwanta bacci.

A haka har kwanaki bakwan da zasu yi ya ƙare.

Ranar da zasu ta fi babu kalar magiyyar da Liyana bata musu ba har diamond ɗaya ta ce zata basu da dubu ɗari biyar su ƙara sati ɗaya amma suka ce su basu san zancen ba gida zasu koma.

Itama Ilham ta ce zasu koma makaranta Lily kam ita ma preparations tace zata koma ga fara dan next week zasu koma.

Ta sha kuka sosai ahaka har suka gama shiri suka kama hanya suka ɓacewa ganinta.

Gidan wani kalar faɗi ne da shi na ban mamaki, dan gidane babba sosai, readers gidan Liyana sai a novel babu shi a reality, because ya gama haɗuwa komai na gidan looks luxurious.

Ga marble tiles kaca -kaca, gidan dai soo Ma sha Allah.

Haka ta yi ta rayuwarta ita kaɗai ta girka abin da take so taci.

Shi ma Abbhi yayi ƙokari sosai wurin haɗa mata gara domin har da Hollandia strawberry ya sa mata her favorite drink.

Kullum tana online ko Sultan ya mata magana bata basa amsa dan bata canza layinta ba.

Monday Morning

Yau ta kasance Monday yau kuma za'a koma makaranta tun safe ta shirya cikin shigarta na wani black abaya mai mugun kyau da tsada sannan ta sanya Gucci flat shoes ɗinta black color haɗe da saka wani ziconic leg chain mai mugun ƙyalli da stones ajiki green and red.

Ta yi mugun kyau sosai sam sam babu wani locality ajikin Liyana komai na ta mai kyau ne.

A hankali ta sanya hannu tare da ɗaukan one in town wayarta, da ta fara amfani da shi last week her pink iPhone , sai da ta gama pictures sannan ta shiga dakakkiyar motarta mai numfashi da Abbhi ya siya mata na gudumowar bikinta.

A hankali ta nufi wurin jeep ɗin nata da yake Black color mai ƙirar G_Box, ta masa wuta tare da barin cikin gidan gaba ɗaya.

Wasa wasa har ta kai one month a gidan bata taɓa ganin wanda ta aura ba

Zata ji fitarsa da dawowarsa duk a kunnenta amma basu taɓa clashing ba ko da wasa.

Yau dai basu da lectures, wani kalar yunwa ke nuƙurƙusan cikinta dan haka ta fito dan nemawa kanta abin da zata sa ma cikin ta.

Misalin ƙarfe biyu ne na rana, wani palazzo trousers ne mai kyau da kuma faɗi ajikin ta sai crop top black color mai ɓulallen ƙirji.

Ko da ta shiga kitchen tea ta haɗa tare da futowa living room ɗin, ganin wayanda ke falon ba zato babu tsammani mug ɗin tea ɗin da yake hannunta ya faɗi a ƙasa ji kake tassss.....

Let's meet tomorrow in page 26 muji yadda zata kaya.

Pending Amarya ce ✍

THE REGRET

(Dana sani).

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.

The Noble Writters

Dedication is Our Strong

_ Pending Amarya 26_

Ko da ta shiga kitchen tea ta haɗa tare da futowa living room ɗin, ganin wayanda ke falon ba zato babu tsammani mug ɗin tea ɗin da yake hannunta ya faɗi a ƙasa ji kake tassss.....

Cikin muryarta mai sanyi da kuma nuna tsantsar farincikin da take ciki ta ce " Ilham!, Farida, Rashidat,." ai da gudu ta ƙarasa wurinsu tare da rungumesu gaba ɗaya, tare da fashewa da kuka.

Rungumeta suka yi tare da sakin ta Reeda ta ce " ashe za ki iya missing namu har haka."

Tsaki Liyana taja tare da faɗin kaɗaici ne kawai buh na rasa wa zan yi missing sai ku? Is impossible ai, dan Allah ku tashi ku dafa min abinci am starving." Rashanda ce ta dalla mata harara tare da faɗin "Ily kaɗai kika girma anan ba mu ba."

"Ni na ce ke ne?."

"Kin ma isa."

Reeda dake zaune cikin wani paper less mai mugun kyau ce ta ce "zaku fara ko?."

A haka suka yi ta hira har sai yamma liƙis sannan suka kama hanyar zuwa gidan Neneh shima da ƙyar sannan ta barsu suka tafi.

Ɓangaren Hydar kam bai wani damu da ya ga what soo called wife ɗin da ake kirarin an masa ba shi dai kawai yana rayuwarsa, daga gidan Mami sai gidansu Amir da kullum cikin tsokanar sa yake da yayi fresh menene sirrin?.

Baya tanka masa balle ya sa ran answer.

Almost a month da bikinsu buh he didn't even bother ya ga wacece ko chanyar corridor ɗinta baya bi balle idonsa ya kai ƙofar da yake sa ran nata ne.

Yau tun safe ta shirya cikin wani up and down masu kyau sai tayi ɗaurinta na matar minister sannan ta saka gucci heels da kuma bag sai wani passion eye wear masu kyau, yau data yi waya da Neneh tace mata zata aiko mata Salimah tun da ba Salimah kaɗai bace ba yar aikin Nenehn.

Hollandia strawberry kawai ta kwankwaɗe tare da fita daga cikin flat ɗin, ta shige mota haɗe da zuge glasses ɗin motar ƙasa dan zata yiwa mai guard magana.

Bayan ta shige Jeep ɗin nata haɗe da sanya seat belt tare da yiwa motar key, kafin ta ƙaraso ma har ya buɗe gate ɗin.

Parker motar nata ta yi tare da yiwa mai guard ɗin magana, cikin muryarta mai sanyi ta ce " Malam mai aiki zata zo da anjima, ka buɗe mata gate, am I clear?, and....."

Bata kai ga ƙarasawa ba wani mota ƙirar Lexus RX ta kutso kai saura kaɗan motar ta shafi ta nata.

Bayan motar ta wuce sai da ta futo da kanta waje ta dallawa motar harara haɗe da kallon mai gadi tace " da maƙota a gidan nan ne?." "Hajiya ke kaɗai ce ai da Alhaji a gidan nan, kuma ina fatan har abada daga ke ba ƙari."

" Idan ya ƙaro sai ka fitar da ita ai, kaji bayanin dana maka?."

" Eh hajiya Allah ya bada sa'a."

" Tun da ance maka gasar kyau zanje ai."

" Allah ya ba ki haƙuri."

" Haƙuri kaya ne." Daga haka taja motar zuwa school.

Ko bayan ya dawo daga gym daya shigo gidan, idanunsa suka gane masa yarinyar da take cikin motar he was shocked to see her for the fourth time, buh how comes?, mai ya kawo ta gidan sa wa tazo nema? Ba dai ƙawar wannan j'airar aka aura ma sa ba.

Kwata -kwata zuciyarsa da ƙwaƙwalwarsa wani kalar tunani suke basa, ga zuciyarsa wani kalar tafarfasa yake, tunaninsa da hankalinsa sunƙi ba shi nutsuwa, haka nan kawai yaji ya tsinci kansa da shiga ɗakinta."

A hankali ya tura ƙofar ɗakin tare da shiga ciki, wani ƙamshin turare ne ya daki hancinsa a take ya ɗan lumshe idanunsa.

Ɗakin kaca - kaca yake, kwalin pizza na kan gado, sai kwalin hollandia, ga wani ɗan container kamar na milky donut shima akan gadon, sai kuma wani bra dake yashe a ƙasa wanda tun shigowarsa ɗakin shi ne abin da ya fara masa sallama, duk ɗakin kaca -kaca.

" Daman nasan tsaftar biri ne, just look at."

Ji yayi kamar amai zai taso masa har zai fita daga ɗakin, sai a hankali idanunsa suka sauka kan wani picture dake bedsides na Ilham, jalbab ɗin himar ke kanta har ƙasa, tayi folding hannunta tana murmushi dimple ɗinta ya loɓa.

Sai kuma ɗayan su biyu ne ita da Liyana, still dai hijab ne ajikinta, ita kuma Liyana palazzo trousers da corset top tayi alamun kiss da bakinta.

A hankali ya ijiye frames ɗin tare da faɗin "might be the one in hijab in shaa Allah."

Daga haka ya fita daga ɗakin.

Ko a mota sai da ta kira Salimah akan lallai idan taje gidan ta gyara mata ɗakin dan jinta take wani iri da ta bar ɗakinta kaca -kaca, dan abin da bata saba da shi ba kenan."

A school ma lecture ta ɗau daɗi, bayan sun fito sai da ta biya gidan Lily ta yi rayuwarta sannan ta kamo hanyar gidanta.

Gidan sai ƙamshi yake dan Salimah sai da ta mata girki ta gyara gidan tsaf ta saka mata turaren wuta.

"Aunty Liyana sannu da zuwa." " Yawwa Salima, mai kika dafa?." " Cous cous ne da sauce."

" Serve me please."

"Okay Aunty."

Daga haka ta shiga kitchen ta zubo mata abincin, sai da taci sannan ta haura sama, shima fess ko ina.

Kayan bacci ta saka tare da feshe jikinta da turare masu tsadar gaske, sannan ta fito dan taya Salimah hira.

Sai kusan Arround 10 O'clock sannan ta haura sama ita ma Salima ta shige ɗakinta na downstairs.

Arround twelve O clock ta tashi tana jin ƙishin ruwa wanda sai da ƙyar ta sauko downstairs dan tsoron gidan take ji, kitchen ɗin ta shige tare da kunna switch ɗin kitchen ɗin, wanda a take idanunta suka gane mata bayan wani faffaɗen mutum mai tsayi, jikinsa sanye da pyjamas white color wanda alamu sun nuna tea yake haɗawa.

Wani kalar razananniyyar ƙara ta saki dan a tunanin ta aljani ne ko ɓarawo.(Ɓarawo da haɗa tea😂□□).

Shi ma a kiɗime ya juyo dan ƙarar har kwanyar kansa ta ratsa, a hankali ya sauke idanunsa akan.....

Let's meet tomorrow

Thanks for reading □□□

THE REGRET

(Dana sani).

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.□

The Noble Writters □

Dedication is Our Strong □

_ Pending Amarya 27_

Arround one O clock ta tashi tana jin ƙishin ruwa wanda sai da ƙyar ta sauko downstairs dan tsoron gidan take ji, kitchen ɗin ta shige tare da kunna switch ɗin kitchen ɗin, wanda a take idanunta suka gane mata bayan wani faffaɗen mutun mai tsayi, jikinsa sanye da pyjamas white color wanda alamu sun nuna tea yake haɗawa.

Wani kalar razananniyyar ƙara ta saki dan a tunanin ta aljani ne ko ɓarawo.(Ɓarawo da haɗa tea😂□□).

Shi ma a kiɗime ya juyo dan ƙarar har kwanyar kansa ta ratsa, a hankali ya sauke idanunsa akan kyakkyawan shape ɗinta na baya data juya da gudu domin nemawa kanta mafita, dan wannan baya ma kama da mutum, bare ma ace ɓarawo ne ko what soo called her fucking husband.

Ko upstairs bata nufa ba ƙasan ɗakin Salimah ta bubbuga da ƙarfi, a firgice Salimah ta buɗe ƙofar ta na tambayarta mai ya faru?.

Ko kallonta Liyana ba tayi ba ta shige cikin bargon Salimahn ta kwanta tana maida numfashi.

''Aunty Liyana lafiya?."

Tsaki taja haɗe da faɗin ''Lafiya ce tayi sanadiyar shigowata ɗakin ki ai tun da penthouse ne ɗakin naki.'' ta ƙarashe maganar haɗe da shigewa cikin bargon.

''Allah ya ba ki haƙuri Aunty.''

Ko kallonta ba tayi ba ta kwanta wani wahallalen bacci ya kwasheta.

Da safe ma bata yarda ta fita ba komai Salimah ke zuwa ɗakinta ta ɗauko mata.

Dan yau babu school ɗin da zata iya zuwa.

Zama tayi a parlourn tare da da kallon Salimah da ta gama kwashe kwanukan da suka yi break fast ta ce '' Salimah ɗauko min hand bag daga sama please, sai ki haɗo min da veil black color, da kuma slippers.''

''Toh Aunty.''

Da sauri ta hau saman tare da ɗaukan abin da ta aiketa sannan ta dawo mata da su.

Shiryawa ta yi tsaf daman already jeens trouser da long sleeve shirt ne ajikinta black color amma wandon fari ne.

Sai kuma slippers baƙi, sai baƙin mayafi da jakarta ƙirar Gucci, chewing gum ɗin dake kan center table ta ɗauka haɗe da cilla shi a baki.

''Salimah shirya muje mu dawo.''

''Aunty kuma a haka za ki fita.''

''Bana son shishshigi, yaushe muka fara wannan dake, je ki ciki ki shirya mu wuce dallah.''

Sum- sum Salimah ta shirya ta saka wani zumbulelen hijab har ƙasa ta fito.

''Wa za ki bi a haka, nifa ba gidan mutuwa zanje ba kika wani saka hijab kamar za ki tafi musabaƙa.''

''Toh Aunty Liya ban da mayafi.''

Tsaki taja sannan ya kuma faɗin '' sai ki taho muje dan ba zan shiga sama ba.''

Daga haka ta wuce wurin dinning room ta ɗauki mukullin motar ta a inda ta bar shi jiya da ta ci abinci, dan tsarin gidansu kenan, idan kana goge - goge, ka ga abu ka bar shi a wurinsa.

Ta nufi jeep ɗinta, tare da sanya seat belt ɗinta. Taja motar ta bar gidan.

Bata zarce ko ina ba sai rijiyar zaki gidan Neneh.

Shigowarsu ma Neneh da fadila ne a zaune yɗar aikinta suna hira.

''Ni Ajiddeh matar Aliyu na ga abin da ya kai min wuya.''

Ko kallon Nenehn bata yi ba ta nufo falon tana ƙoƙarin zama a parlourn.

'' ke kam rainon Nabil bai miki kyau ba, mai wannan?, dubi ki ga yadda nake hango ƙasusuwa, duk kin bar Lami a buɗe.''

''Neneh ke ko missing mutum ba kya yi kya bari na zauna kafin ki fara halin naki ai.''

Matsowa ta yi sosai kusa da Liyanar tare da faɗin.

''Kin haɗu da Khairatu a waje ne?."

''Wace hakan?."

''Ashaa, Uwar mijinki mana.''

''Ni ina da mijina?, ko akwai wanda ku ka yi da shi zan aure sa?."

''Na yarda bayan tsalle tsalle harda shaye shaye a tattare dake, tun da Allah ya jeho ki sai ki zo muje can bachirawa wai Ummaru ba lafiya.''

''Subhanallahi, Tsohon manyan ne ba lafiya?."

''ni fa iyayinki ke haɗa ni dake, ba komai ba, kice Babi, kawai kin tsaya wani kalacen jaraba.''

''Ke ta shafa ai, ban tambayi mijina ba babu inda za na je.''

''Aatouh mai ruwan Neneh uban uwarki ne dai.''

''Ba ubanki ba.'' ta faɗa tare da murguɗa baki.

''Fatima ni kike zagi?."

''La Salimah kuji Neneh za ta min sharri fa, dan Allah wannan zagi ne?."

Neneh baƙin ciki ma ya hanata magana, sai can bayan some minutes sannan ta ce ''Dan kaza kazanki zo ki fitar min a gida.''

''Babu inda zani, Salimah ɗauko min Apple dan Allah.''

''Kizo ki fita ko na tuno miki ranar da Ikimat ke naƙudar ki a duniya.''

''Da naji daɗi.''

Sai misalin ƙarfe shida da yan canji Liyana ta bar gidan ta koma nata da ita da Salimah.

Aliyu kam tun da ya ga ta fita da gudu bai ma bi ta kanta ba dan shi a rayuwarsa idan aka ce menene dislikes ɗin da kake da shi a rayuwarka toh mutum mara

nutsuwa ne, he's an introvert sam wuri mai hayaniya yana nisantar kansa da shi ne, idan yaji ihu ko wani abu makamancin disturb, ya kan ɗan tsinci kansa da ciwon kai, shiyasa idan kana magana da yawa ma baya hulda da kai.

Bayan ya gama haɗa tea ɗinsa ya sha sannan ya yi sallah raka'a biyu haɗe da kwanciya.

Washegari ma da sassafe ya bar gidan ya tafi gidan Mami da kullum ba ta da magana sai na Liyana.

Shima Amir kullum cikin maganar zuwa yake shi da mamansa, amma kullum cikin hana shi yake duba da yadda ko sanin yanayin yarinyar bai yi ba balle a kai magana kan kawo manyan baƙi.

Ya maida hankali kan business ɗinsa sosai, dan ko da wasa ba zaka taɓa ganinsa wai da sunan he's not busy ba because shima ya san he's damn busy with his business, trying to achieve more goals, kuma babu laifi managers na yin abin da ya dace.

Dan a iya month, sai a samu riba fiye da five billion tun da shi ɗin akwai factory waɗanda su ne suke ƙerawa daga kan android, laptos tablets, fridge, etc sune suke samar da shi.

HYDAR na da mahaukatan kuɗi, idan yazo wurin spending ɗinsu he spends it roughly, because shi bai yarda da wannan al'adar ta Malam Bahaushe wai a tara musu ba, A'a idan sun fito sun zo duniya sun kai munzalin nema su nema su tara na kansu.

Shi a stage ɗin da yake yanzu mace da abin da ya shafe ta ba sa gabansa, he just want peace, like original peace of mind.

Idan yana son shakatawa ya kan fita shi da Amir, su zagaye Kano sometimes har da wajenta, amma still, ko budurwa ko wani abu he didn't care about them.

Saboda ɗaure fuskarsa ma ba kowacce kilaki bace ba ke kawo kanta da sunan seducing ko soyayya ba, noo he didn't do that.

Washegarin ranar ma Amir ya kira dan kansa wani mugun sarawa yake, tunda yayi sallahr subhi ma bai tashi a barci ba sai kiran Amir da yayi akan ya taya shi handling, kallon laptop ɗinsa, sannan yau zai yi conference video call da su saboda CEO ɗin Adafar Ventures Adam Ayan Muhammad Ali Humaish Al khaizaran (Beyond heart break). yazo all the way from Singapore akan wani sabon ac da suka ƙera za'a basa sari almost fifty thousand pieces, kuma akan hakan ne zasu yi magana.

Washegarin ranar ma da sassafe bayan ta shirya cikin shigarta na as usual, fruit salad kawai ta sha sannan tayi packaging milky donut, da kuma hollandia strawberry yourghurt ɗinta.

Bayan ta gama packaging komai ta zira slippers ɗinta ta nufo hanyar da zata sada ta da balcony ɗin da zaka shigo parlourn ta buge mutum dake sanye cikin jumper ox blood color da sauri ta ɗago ta kallesa sakamakon wayar da yake amfani da ita wanwar a ƙasan wurin.

Dubanta ta kai akan kyakkyawar fuskarsa wanda abin da idanunta suka gane mata suka girgiza dukkanin tunanin ta.....

Mu haɗu a next page

The regret na baku ginger kuwa😭

THE REGRET

(Dana sani).

PENDING AMARYA CE

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.□

Alhamdulillah it's Friday again □.

ALLAHUMMA SALLI ALA SAYYIDINA MUHAMMAD, WA ALA AHLI MUHAMMAD KAMA SALLAITA ALA IBRAHIM WA ALA AHLI IBRAHIM INNAKA HAMIDUN MAJEED.

ALLAHUMMA BARIK ALA MUHAMMAD WA ALA AHLI MUHAMMAD KAMA BARAKTA ALA IBRAHIM WA ALA AHLI IBRAHIM INNAKA HAMIDUN MAJEED □

The Noble Writters

Dedication is Our Strong

_ Pending Amarya 28_

Washegarin ranar ma Amir ya kira dan kansa wani mugun sarawa yake, tun da yayi sallahr subhi ma bai tashi a barci ba sai kiran Amir da ya yi akan ya taya shi handling, kallon laptop ɗinsa, sannan yau zai yi conference video call da su saboda CEO ɗin Adafar Ventures Adam Ayan Muhammad Ali Humaish Al khaizaran (Beyond heart break). yazo all the way from Singapore kuma akan hakan ne zasu yi magana.

Washegarin ranar ma da sassafe bayan ta shirya cikin shigarta na as usual, fruit salad kawai ta sha sannan ta yi packaging milky donut, da kuma hollandia strawberry yourghurt ɗinta.

Bayan ta gama packaging komai ta zira slippers ɗinta ta nufo hanyar da zata sada ta da balcony ɗin da zaka shigo parlourn, buge mutumin dake sanye cikin jumper ox blood color tayi wanda hakan ya sanya ta ɗago da sauri ta kallesa sakamakon wayar da yake amfani da ita wanwar a ƙasan wurin.

Dubanta ta kai akan kyakkyawar fuskarsa wanda abin da idanunta suka gane mata suka girgiza dukkanin tunanin ta....."

Cikin muryarta da yake breaking ta fara magana "SUL....TAAAN..... whaaaa..... What..... U ... Doing here..?."

Kallonta yayi da kyau sosai sannan ya ce " i will be the one asking you this, for almost 3 weeks you're not picking up my calls, na miki wani abu ne?." Ya faɗa tare da riƙe kafaɗunta, da sauri ta ƙwace jikinta daga hannunsa, sannan ta ƙara kallonsa cikin ido ta ce" ka amsa min tambayar mana." "Liyana i missed you, dan Allah babyn Abbhi ki daina ignoring ɗina, let me hug you ko na ji sanyi a rain....." Bai ƙarasa maganar ba wayar dake ƙasa ta fara ringing.

"Damn it." Ya faɗa a taƙaice sannan ya ɗaga wayar da ya kwankwatse a ƙasa ya ɗaga wayar a hankali tare da juya mata baya.

"Hello Big Brother, in the next ten minutes please." Sun kai kusan minti biyu suna magana da yayan nasa sannan ya katse wayar.

Juyowan da zai yi ya tarar har ta shige Jeep ɗinta gate man ya buɗe mata gate ɗin har ta fita da mugun gudu.

A cikin motar ma tunani take kala kala, ko dai Sultan ne mijinta?, ko abokin mijinta ne?, wata zuciyar tace " Nooo it can't be, and it will never be." Ta faɗa tare da dukan stiring motar.

"Ya Allah Have some mercy upon me, yah rabbi what's all this happening."

Ta faɗa tare da juya kan motar ta yi hanyar hotoro gidansu kenan.

Tana isowa gidan wani kalar horn ta danna mai shegen ƙarfin tsiya, bayan mai gadi ya buɗe mata motar ta shige gidan da mugun gudu.

Motar Abbih da na Ammi duk suna nan a parke alamun babu wanda ya fita cikin su, ko da ta shigo ɗin ma, cacar baki Rufaidhat da Ammi suke.

"Shegiyya farar karuwa, ai ke ɗin a tafin hannuna kike, uban waye bai san ba ki shigo gidanki da budurcinki ba, ko an gayamiki banda labari akai, shashasha kawai, kuma yar ta ki da kike ikirari da kin aurar, ina ne bata karaɗe ba hotels kala kala babu wanda bata sani b....."

Rufaidhat ba ta kai ga ƙarasawa ba Liya ta sauke mata mari zafafa guda biyu tare da ranƙwashi mai rai da lafiya.

"Idan kina tunanin mahaifiyyata ta na a tafin hannunki ni à ina kike tunanin zan saki, yar balaja'u."

"Ke kuma Ammi mai na biye mata bayan kin san yar ƙwayace, huh."

"Ke kuma Ilham mai kika tsaya yi, farar kura."

Liyana ta faɗa tana ƙafe Ily da ido.

"Liya Ammi ta ce nai shiru faa." Ta faɗa ta na ƙara sakin kuka.

"Ina Abbhina."

"Ya na ɗakinsa ciwon kai ke damunsa, since day before yesterday."

"What ?! and non of you call me, ku gaya min kuma mun yi waya da shi jiya bai gaya min ba."

Rufaidhat dake tsaye wajen stairs Liya ta hankaɗe tare da faɗin " Stupid hag."

Da gudu ta shige corridor ɗin ɗakin Abbhi wanda yanzu ta kai four months ba ta shigo shi ba tun ranar da ta bar gidan.

Ya na zaune akan Sofan bedroom ɗinsa yayi stretching ƙafarsa akan center table ya na shan lemon juice ta shigo ɗakin.

"Amarya." Abbhin ya faɗa tare da buɗe hannunsa da nufin tayi hug nasa.

Da gudu ta ƙaraso tare da rungumarsa nasa tana ƙarewa fuskarsa kallo.

"Amma ba kai kama da mai rashin lafiya ba."

"Rabu da su sun takura min da kawo ƙara ne wallahi, that's why kawai nace musu hakan na ɗan huta."

"Abbihhhhh."

"Naaaaam."

Ya kwaikwayeta.

"Buh ka sani cikin damuwa manaaaa."

"It's okay dear Am sorry dear, and yanzu ina za ki je ?."

"Am planning naje school akwai test yau buh na ma fasa, i wanna spend my time here with you."

Ta na faɗin haka tayi kwanciyarta anan kan coach ɗin.

"Ko za ki shirya muje Domino's Pizza?."

"Banda kaya ai anan Abbhina."

"Ina ta so daman ranar da zan zo gidanki na ba ki kayan da na siya miki amma tun da kin zo sai ki saka shi ai, ragowan kya tafi dasu."

"I love you wallahi Babana."

"Love you more."

Daga haka ya miƙe ya buɗe tankamemen press ɗinsa tare da ɗauko wani leda mai kyau.

"Na san palazzo trousers ne favorite dress ɗinki soo I picked them for you." Ya faɗa tare da zaro wasu tsala -tsalan palazzo trousers masu kyaun gaske.

Daga sama har ƙasan su wani kalar beeds ne ajikin su masu walƙiya sosai daga ganin kayan za ka san kuɗi sun yi kuka .

"Abbhina you're the best ever, Allah ya ƙara buɗi."

Bata jira amsar sa ba ta shige toilet ɗinsa dake ƙamshi mai daɗin gaske haɗe da canza shigarta zuwa kayan da Abbhin ya siya mata.

Ko da ta fito sai yabon kyaunta yake.

Take taji duk wani damuwarta na ganin Sultan a gidanta ya kau.

In less than ten minutes ta shirya cikin kayan da suka mata matsiyacin kyau.

Already daman slippers ne aƙafarta and her bag to is the same color with her slippers.

A hankali suka sauko shima Abbhi ya mayar da rigarsa na kaftan yadin nasa mai mugun kyau da tsada, sai car key ɗinsa dake hannunsa ta benz ɗinsa, hannunta acikin na Abbinta.

Ilham dai ita kam abaya ce ajikinta tana lunch tana daddanna wayarta dan chatting take da Sultan da sai magana yake mata akan changes ɗin Liyana da kuma ganinta da yayi yau buh he didn't tell her a inda ya ganta.

Ammi data fito da wani bowl ɗin fruit salad ce ta ce "Yallabai the lunch is ready." "Noo eatry muka nufa, yau ɗin, since babu wadda ta damu dani a cikin ku."

Sidda kanta kawai Ammi ta yi sannan ta ce " Gimbiya mai ya kawo ki yau ɗin."

Fuska ta yi kamar mai son yin kuka sannan ta ce "nazo naga Abbhina ne faa Ammi."

"Is alright Allah ya kyauta ya kuma tsare."

"Am sorry Ammi ke nazo gani faa."

"Nooo da maganar farko ake amfani ai."

"Nope Ammi an wuce generation ɗin fa."

Kafin ta gama surutan ta har Abbhi ya wuce ya fita.

Rufaidhat ce ta zauna a living room ɗin tare da faɗin "su fanko har za'a tafi kenan, har an gama barbaɗin."

Cikin wani kalar ɓacin rai Liya ta ce "Naji idan ma fankon da gaske ne ba ubana ne ya maida ni ba hakan wasu kuma faaa?." Ily ta caɓe da faɗin "karuwan gidane idan an gama da iya sai adawo kansu."

Wani kalar tsawa Ammi ta daka musu.

Taɓe baki Liya tayi tare da faɗin " wallahi Ammi shiyasa ta rainaki, dama nice matar Abbhina da kin daɗe da fita a gidan nan tsohuwar bazawwara."

Ajiye bowl ɗin Ammi ta yi tare da cire slippers ɗinta ta biyo Liyana, ai da gudu ta arce ta bar falon haɗe da ƙwalawa Abbihnta kira.

Rufaidhat kuwa ta cika famm kamar zata fashe.

Sannan idanunta suka kawo wani ƙwalla mai mugun zafi tana dana sanin, sanin Nabil da ƴaƴansa da tayi. Dama zamanta tayi a gidanta su cigaba da damawa da ita da Sufyan ɗinta.

Da gudu ta haura sama.

Koda ta shiga motar Abbih numfashi kawai take da sauri haɗe da dariya.

"Wallahi Abbhi matanka ba zasu kashe ni ba, muyi sauri ka ajiye ni a gidana."

Ta faɗa tare da rufe ƙofar motar.

A hanya ma kawai labarai suke ta yi, a hankali ta ce " Abbih ina ma muka nufa?."

"Wani sabon wurin shakatawa ne."

Bata bashi amsa ba ta cigaba da jin waƙar ta da ta jona da ear plugs ɗinta sabon waƙan da Davido ya saki _Un Available _.

Basu wani jima ba suka ƙaraso Hydar's palace and garden, dake a titin hanyar minjibir wurin ya mugun tafiya da tunaninta wurine dake cike da shuke shuke na ban mamaki na flowers mabanbanta tun daga gate tulip flowers ke shinfiɗe a ƙasa ga mutane nata basu ruwa.

The place is damn beautiful.

Kallon Abbhi ta yi tare da faɗin "i love it, promise me every friday za ka ɗinga kawo ni nan please."

"Pinky promise dear."

Fitowa suka yi daga motan bayan ya faka motar.

Wurin ƙarshe ne wurin kyau amma gaba ɗaya wurin is artificial, komai constructing nasa aka yi.

"Kaɗan kika gani idan kinje VIP ɗin za ki riƙe baki."

"Abbhi dan Allah?, toh kai ya aka yi ka san nan ma bayan kana office kullum ko dai za'a wa Ammi ta uku?."

ta faɗa tare da turo ɗan ƙaramin full lip ɗinta dake shafe da lipstick.

" Babyn Abbhi kina da matsala, oya let's goo."

Haka ta riƙe hannunsa suka wuce cikin wurin da ake biyan kuɗin.

Bayan sun shigo reception ɗin ma ce musu aka yi the boss is arround, ba zasu iya shiga VIP ɗin ba, indai kuma suna don shiga sai dai 500k each person.

A haka ta matsawa Abbhinata sai da ya biya suka shiga wurin da idan ka gansa zaka manta Nigeria ne. Kana ganin yanayin wurin ka san all the way from out side aka masa wannan aikin.

Dan wani kalan rafi aka yi a wurin sannan aka zuba yashin sahara, da duk idan kaga wurin za kayi tunanin ocean ne sai dai ocean is big and wider than what she's seeing right now.

Komai na wurin looks classy ga bishiyoyin kwakwa da suke a wurin just saboda passion.

She was like woow, wayarta ta ɗauko ta fara sakin reels in less than a minute ta samu like fiye da 1million because ta riga da ta tafi viral in everything akan social media sai dai fa ita bata facebook da tiktok.

Ko ina yayi kyau ga wasu boats dake ta yawo kan ruwan because sai da akayi ramin almost 20 kilometer sannan aka yi constructing rafin.

Ga wasu kujeru a wurin na shakatawa, turawa ɗaiɗaiku ne a wurin saboda is a VIP place sannan aNƙara zuƙa masa kuɗi duba da boss na nan.

Ɓangaren Mr. Ali namu kuwa tun safen da ya kira Amir bayan ya ɗaga suka yi magana ya kira Sultan domin ya duba masa abubuwan dan yana da buƙatar fresh air.

Bayan Sultan ɗin ma yazo jogana sa yayi da laptop ɗinsa suka fara meeting ɗin daya kamata da CEO ɗin Adafar Ventures Adam Ayan Muhammad Ali Alkhaizaran.

Combat ne ajikinsa sai wani white designer polo shirt sai ya saka Gucci slippers masu kyau haɗe da ɗaukan key ɗinsa suka wuce a motarsa.

Wurin shakatawar sa ya nufa domin ya samu bacci, dan baccin hotel da ban yake da na gida dan da akwai hotel a wurin shakatawar nasa.

Arround 10 O'clock ya ƙarasa cikin ƙantamemen luxury Joint ɗin nasa wanda daga gani kasan an narka wasu mahaukatan kuɗi a wurin gina shi.

Direct lift ya bi ya shiga dan idan yace ta ƙofofi zai bi QR code zasu masa wahalan snapping ga thumbprint ma zai ba shi wahala.

Danna bell ɗin da zai sada shi da réception ya yi.

Wanda a take suka kawo masa breakfast ɗinsa.

A ɗakin ma Amir cika mi shi kunne ya yi da surutai berekete babu kai da ƙafa, da dabara ya sa shi yaje wurin rafin domin ya shiga boat ya za ga wurare, ya yi race da polo with so many games dai arround 2 O clock zai sauko, dake Amir ɗan sharholiyya ne babu ruwan shi dan shi he's an extrovert kowa ba shi ne.

A take ya amince ya bar ɗakin nasa.

Bayan fitar Amir ɗinma wani bacci mai mugun daɗi ya wuce da shi, wanda kuma babu wani ɓata time ya basa haɗin kai.

Liyana kam daman tun da suka zo da ta ga one hour ne ya cisu zuwa nan tace masa after four zasu koma gida.

Arround one thirty ta fara jin yunwa ga Abbhi ya na can gefen rafin ya na amsa waya da business partners dan sabon engine na atamfa yake son siya.

Ga shi babu wani waiter dake wurin balle ta kira a kawo mata strawberry smoothie ta sha.

A hankali ta tashi daga kan kujerar dake wurin tare da fara tafiya a hankali towards Abbhi at the same time pressing her phone in a comfortable way.

Bigewa tayi da mutum ta yi baya kamar zata faɗi sannan ta dawo ta tsaya da ƙafafunta.

Sai da ya ƙarewa jikinta kallo, sannan ya kalli fuskarta dake sanye da farin glasses.

Ganin wanda ke tsaye gabanta ya mugun ɗaga mata hankali, amma sosai ta dake haɗe da murguɗa bakinta tare da faɗin "kai kullum duk inda zan je sai ka bi ni are you for real?." Ta faɗa tare da ƙara murkuɗa masa bakin.

Shanyayyun idanunsa dake nuna alamun basu daɗe da tashi a barci ba ya zuba mata su sosai wanda hakan ya sa cikin ta ya yi wani mugun kaɗawa....."

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

Allah ya haɗa mu ranar monday mu fara Posting steadily.😭

THE REGRET

(Dana sani).

~PENDING AMARYA CE~

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.□

The Noble Writters □

Dedication is Our Strong □

_ Pending Amarya 29_

Ganin wanda ke tsaye gabanta ya mugun ɗaga mata hankali, amma sosai ta dake haɗe da murguɗa bakinta tare da faɗin "kai kullum duk inda zan je sai ka bi ni ? are you for real?." Ta faɗa tare da ƙara murkuɗa masa bakin.

Shanyayyun idanunsa dake nuna alamun basu daɗe da tashi a barci ba ya zuba mata su sosai wanda hakan ya sa cikin ta ya yi wani mugun kaɗawa....."

A hankali ya buɗe bakinsa ya ce "I will be the one asking you this spoiled brat, duk inda naje kina sane da ni da rayuwata, kina yawan satar kallona, this should be the last time da zan ganki arround me, if not." Bai ƙarasa ba kawai ya yi ƙwafa.

"Karasa karta kashe ka."

" I don't have time ga wa'yannan kalan matan, for the last time don't you dare show your face again, get lost!."

Sakin baki ta yi dalala har ya ɓacewa ganinta bata sani ba, ga baƙin cikin ɓakar maganar da ya sakar mata, wai wa'yannan matan?.

Karuwa fa kenan yake nufi.

"Kam balasti."

Ta faɗa a fili kafin tayi wani harraman binsa har Abbhi ya iso inda take.

"Abbhi yunwa."

"Da ƙwandala ake cin abinci fa anan."

"Abbhi manaaa, Allah yunwa nake ji ba wasa nake ba."

" Sorry babyn Abbhi." daga haka yaja hannunta suka ƙarasa wajen wurin order abinci kafin suka fara ci.

Sai da ta shiga ruwa suka yi yawo sosai, sai ƙarfe goma sannan ta nufo hanyar gidanta dan sai da Abbhi ya ajiyeta a gidansu ta ɗauko kayan da Abbhin ya siya mata da motarta, shima Ammi kamar ta kasheta da faɗa.

Da wani mugun speed take sharara gudu a saman titin da babu kowa sosai sai manyan motoci haka tayi ta overtaking mutane.

Wani kalar birki taci sanadiyyar karon da suka yi da wani mota ƙirar Lexus LC 500.

Wani kalar matsiyacin duka ta kaiwa sitiyarin motar tare da daka wata uwar tsaki ta fito daga cikin motar ta.

Babu mutane sosai a unguwar, a hankali ta duba motarta tare da leƙa wanda suka ci karo.

Yana zaune ahakimce ya na ma waya.

Ganin hakan ne ya sanya ta komawa cikin motarta da niyar tada motarta ta ƙara gaba.

Still motar a buɗe ta barta dan sai ta gama tada mota sannan take kulle ƙofar ita haka tsarin ta yake.

"Kamar saukar aradu taji muryar mutum a kunnenta unexpectedly wanda saboda hakan ya sanya ta firgita a take dan Liyana akwai tsoro.

"Can't you say sorry?."

Dake babu wani haske a motar yasa bata ga fuskar ba buh the voice sounds familiar amma wannan ya na da sanyi not wanda ta saba jin sa a fusace.

A hankali ta fito daga cikin motar wanda hakan ya ɗan sa shi ya ɗan ja baya.

A nitse ta fara magana " You will be the one to kace min sorry ai, saboda kana waya kana tuƙi which is not allowed."

Ta faɗa tare da fara ƙoƙarin komawa cikin motarta.

"Wayarsa daya mayar gaban aljihunsa tun lokacin da ya gama waya ne ya fara kawo flash alamun kira.

Wanda hakan ya hasko masa fuskar wadda take cikin motar.

Sai da ya ɗan ja baya kaɗan sannan ya ce " at this time daman sai mata Irinku ke shawagi a titi."

"Whaaaat! How dare you?."

Ta faɗa tare da cire glasses ɗin ta.

"Don't you dare ki yi min magana son ranki."

A hankali tayi shiru tare da mayar da hankalinta kan gaban motarta tana kallon titin da babu kowa, sannan a hankali ta ƙara faɗin " ja gefe zan kulle motana."

Tsaye yayi bai motsa ba awurin.

"What's all this wai, ko kaine ka siya min motar?!."

Ta faɗa a hasale.

Ja yayi da baya yana ƙare mata kallo da kyau wani kalar matsiyacin kallo ta masa duk da duhun haɗe da tsaki sannan ta tayar da motar ta wuce.

Tun bayan da suka rabu da ita a joint ɗinsa sai da suka yi yawo sosai da Amir sannan ya kamo hanyarsa na dawowa gida domin ya huta, still a hanyarsa sai da ya haɗu da wannan shaiɗaniyyar yarinyar.

Har yanzu mamakin kalar iyayen da suka yi raising ɗinta yake.

Gaskiya sun yi sakaci da yawa.

To eleven ace yar ki bata dawo ba kuma ba zaki iya neman inda taje ba.

Dubi yadda take ta'amali da tsofaffi duk sugar daddies that girl is a fitina to society gaskiya.

Sai tsaki yake ta jaa, dan Hydar na da mita sosai.

Murza motarsa ya yi ya cigaba da tafiya har ya ƙaraso gidan.

Liyana kam ranta fess she didn't even care about rashin ɗan idon data masa duk da bai bata fuskar hakan ba.

Bayan ta dawo ɗinma sai da taci abinci ta yi wanka ta sauko parlour cikin shigarta na pyjamas wandon ya tsaya mata a dai-dai gwiwa.

Rigar ta lafe luf - luf a jikinta.

Duk da uban daren da ake tsalawa sai da ta kunna waƙa a TV haɗe da ƙure volume.

Ga home theater da sai amsa kiɗan suke.

Koda ya dawo cikin gidan ma tun a parking lot yake jin kiɗa na tashi na ban mamaki.

Shigowarsa keda wuya ya tarar da ita tana tweking kamar wadda take a club.

Waƙar Ayra Starr Bloody Samaritan ce ke tashi a living room ɗin.

With all her body take girgiza ko ina na jikinta ko ina ta na malƙwayashi haɗe da lanƙwasa shi dai-dai da salon kiɗan.

Baki sake ya tsaya kallon wadda yafi tunanin cewa ita ce matar tasa sannan a hankali ya ƙaraso living room ɗin haɗe da ɗaukan remote ɗin Tvn ya na mai kashe tvn.

A tunaninta ko Saleemah ce hakan ya sa ta juyowa a fusace wanda hakan ya yi sanadiyar haɗa idanunsu a daidai inda ya duƙa zai maida remote ɗin mazauninsa....."

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

THE REGRET

(Dana sani).

~PENDING AMARYA CE~

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.

THE NOBLE WRITTERS TEAM.

Dedication is Our Strong

_ Pending Amarya 30_

A tunaninta ko Saleemah ce hakan ya sa ta juyowa a fusace wanda hakan ya yi sanadiyar haɗa idanunsu a daidai inda ya duƙa zai maida remote ɗin mazauninsa....."

Da wani kalar speed ta ja baya sannan ta ƙara matsowa sosai haɗe da murza idanunta ko gizo suke gane ma ta, da ta ga dai da gaske idanun na ta ba su mata ƙarya ba hakan yasa ta daddage ta runtuma wani uban ihu wanda duk wani na kusa da ita idan ya ji zai ji shi ne har dodon kunnensa.

''Salimah! Salimah! Na yi gamo da aljani, innalillahi wa inna ilaihir rajiun!."

Jikinta sai rawa yake dan ganinsa da ta yi ya yi mugun ɗaga mata hankali.

Kwalama Salimah kira take amma babu alamun zata fito ma, kuma mutumin sai ƙara dosota yake, itama ta na matsawa baya.

A hankali ta tafi tare da zurawa a guje zata haura saman stairs teddy slippers ɗinta ya faɗar da ita a ƙasa.

A hankali ta ƙara yunƙurawa ta tashi daga ƙasan haɗe da tsayawa ta na ƙare masa kallo.

Salimah dake kwance ta na waya da boyfriend ɗinta ce ta fito a kiɗime jin kiran da Liyanar ke kwaɗa mata, "Aunty Liyana what's wrong?."

Idonta ne ya sauka akan Hydar dake tsaye ya ƙafe Liyanar da eyes ɗinsa.

''Laa Ya Hydar sannu da zuwa.''

''Yawwa!, Sannu!, who's she!?." Ya amsa gaisuwar nata haɗe da jefo mata tambaya akan Liyanar da itama ta ƙuresa da firgitattun idanunta.

Sai da ta tsaya yi musu kallon mamaki sannan a hankali kuma ta ce ''Matar ka ce mana Yaya.''

''You can go.''

''Toh Yaya.''

A hankali ya fara ta ko ƙafafunsa zuwa inda take tsaye a fusace ta ce ''Kar ka matso kusa dani ko da wasa!.''

Bai kula ta ba ya cigaba da matsowa kusa da ita.

''Don't you dare come closer, you dog!."

Jikinsa har wani ƙalar huci yake, idanunsa na canza kala dan ya sha faɗa ya tsani mace mara tarbiyya da kuma mara kunya a rayuwarsa.

Da sassarfa ya ƙaraso wurin da take haɗe da ɗauke ta da wanni kalar gigitattcen mari sannan a hankali ya ce ''wannan na ranar da kika faɗar min da waya ne, kin tuna ranar?, nasan ba za ki tuna ba.''

wani marin ya ƙara mata wannan karon sai da ta ga stars kalar na duniyar mars (😂😂).

'' Wannan na ranar da kika bige min mota ne.'' sannan ya ƙara mata wasu twins ɗin mari making four ''wannan na marin da kika min ne saboda lack of tarbiyya da iyayenki suka ba ki.''

Hannu ya ɗaga zai ƙara sakar mata wani marin wanda bai kai ga marin ba ta bangaje hannun nasa tare da hawan kan stairs da gudu cikin shashsheƙar kuka ta fara magana ''Ai ba jaka aka kawo maka ba da tun safiyar Allah kake marina mugu kawai, lack of tarbiyya kuma wannan kai za'a kira da shi, banza kawai mai dukan mata lusari!.''

Da gudu ya biyo ta zai dake ta wanda hakan ya saka ta arce a guje.

Ko da ta shiga ɗakinta ma faɗawa ta yi akan gadonta ta fashe da wani sabon kuka, a haka har bacci ya kwasheta.

Ɓangaren HYDAR kam marin da ya mata ma a ganinsa bai huce ba, dan laifukan ta sun fi yadda ya lissafo, ga yawo da samari da aurensa akanta, ai wannan ma sam - sam ba matar aure bace, ya sha ganinta a joints kala - kala, musamman da ya ke gina joint ɗin shi da yake duba kalar wa'yanda ake da su anan kano ɗin.

Kwafa ya yi tare da faɗin ''kaɗan kika gani, zaman gidan nan ma sai ya gagare ki.''

Daga haka ya shige toilet domin watsa ruwa sannan ya sanya kayan baccinsa tare da kwanciyarsa, sai da ya ɗan duba laptop sannan ya gyara kwanciyarsa bacci mai daɗi ya kwashesa.

Washegarin ranar ma Liyana ko da wasa ba ta fito ba rayuwarta kawai take a sama Salimah na kawo mata abin da take so.

Shi HYDAR ma ko ta kanta bai bi ba, duk da ya ga abinci jere kan dinning buh he prepared ya ci na siyarwa because shi yanzu komai na gidan ya fice masa a kai, ga tsanar yarinyar na ƙara fizgarsa.

Fitarsa ke da wuya a gidan wayarsa ta fara ringing ko da ya duba ma Abbuh ne ke kiransa a wayar ajiyar zuciya ya sauke sannan a hankali ya ɗaga.

''Assalamu alaikum Abbuh.''

''Wassalam, har ka fita ne?."

''Eh Abbuh.''

''Kana ina toh yanzun?."

''Ina hanyar zuwa gida ne."

''Gidanka?."

''A'a Abbuh gidanmu, naka kai da Mami toh.''

''Yayi maka kyau, ka zo ka sameni a office yanzun nan.''

''Wanne a ciki?."

''Na takalma.''

''Toh sai na iso Abbuh.''

"Okay, alright.''

Ajiye wayar ya yi haɗe da fuzgar da iska a bakin sa sannan ya juyar da kan motar tasa zuwa can office ɗin.

Liyana sai da taji fitar motarsa sannan ta fito falon fuskarta duk shatin mari dan har lokacin shatin na nan.

''Munafuki.'' shine kalmar da ta faɗa haɗe da zama akan kujerar dinning ɗin ta fara cin abincin da ta ganshi a jere a kan dinning ɗin.

Salimah ce ta fito daga cikin ɗakinta fuskarta da dan damuwa tazo wurin Liyanar ''Aunty Liyana, kin tashi lafiya?.'' ajiye spoon ɗin hannunta ta yi tare da faɗin ''lafiyar ce ta saka kika ganni da shatin mari à fuskata algunguma!.'' ta ƙara jan tsaki haɗe da kwaikwayon Salimahn.

''Laa Yaa Hydar sannu da zuwa baka sani ba matarka ce ai.'' ta ƙarashe maganar da tsaki tare da faɗin ''Rubbish.''

Sannan ta cigaba da cin abincin ta .

Har Salimah ta fara kwashe warmers ɗin Liyana ta ƙara faɗin ''Shi ko menene sunan da kika kira ma, ko a ina kuka haɗa dangi har ya zama yayan naki oho.''

''Aunty Liyana dan Allah ni kiyi haƙuri, ki barni haka.''

''Ni kauce min a hanya, mtsww laa ya hydar.''

Ta faɗa sannan ta ƙarasa up stairs da gudu.

Miss call ɗin Lily ta gani hakan ya saka ta bi wayar.

Ring biyu ta ɗaga a hankali suka fara magana because test ɗin jiya shine jigon exam ɗinsu na first semester a level 400.

''Lily yaushe za ki zo?."

''Bae i think next week zan zo buh kinsan ni wallahi am not good a zuwa gidan friends unless idan zamu haɗu a Hydar's palace and garden.''

''Ai sai dai kar mu haɗu wallahi.''

Haka suka cigaba da hira har ƙarfe biyu sannan ta yi sallah.

Bayan ta idar ma fitowa dinning room ta yi domin cin abincin rana.

''Aunty Liyana kin fasa zuwa Saloon ɗin ne?."

''Kin saka an yi min damaging fuskar zan fita a hakan?."

Parking ɗin mota Liyana taji a compound wanda a take ta saki spoon ɗin hannunta haɗe da arcewa da mugun gudu.

Salimah kawai da idanu ta bita.

''Assalamu alaikum jama'a.''

Muryar Neneh ta daki kunnen Liyana da saura ƙiris ta ƙarasa buɗe ɗakinta.

Juyowa ta kuma yi a million ta fara saukowa da gudu jikinta daman tun mini skirt ɗin yau da safe ne ba ta yi wani wankan ba.

Sai wani crop top mai kyau milk color ƙafarta kuma sanye da slippers ɗin Gucci.

Kanta ba kitso tayi parking a tsakiya santala santalan cinyoyinta na ta sheƙi kamar kullum.

''Sannu da zuwa my Neneh.''

''Subhanallahi, Fatima ko fitina? , maza dallah je ki saka tufafi kin bar su lantana a buɗe haka?."

Ɗago kanta tayi a ta kai dubanta wurin Neneh, amma idonta bai sauka kan kowa ba sai wanda ke sanye cikin shigar manyan kaya kansa na sanye da hular nan ta zanna bukar.....

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

THE REGRET

(Dana sani).

~PENDING AMARYA CE~

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.

THE NOBLE WRITER'S TEAM

Our strength lies in Dedication

Am back to who I'm

A baya nayi sanya amma yanzu na ajiye son jiki agefe, akan kawo ƙarshen wani abu domin fara sabon abu.

Dan haka na kawo karshen sanyin jikina domin cimma nasarata.

Kafin na cimma nasarata sai na ajiye son jiki agefe.

Am Soo sorry everyone.

Pending Amarya as usual But not like before

_ Pending Amarya 31_

Parking ɗin mota Liyana taji a compound wanda a take ta saki spoon ɗin hannunta haɗe da arcewa da mugun gudu.

Salimah kawai da idanu ta bita.

''Assalamu alaikum jama'a.''

Muryar Neneh ta daki kunnen Liyana da saura ƙiris ta ƙarasa buɗe ɗakinta.

Juyowa ta kuma yi a million ta fara saukowa da gudu jikinta daman tun mini skirt ɗin yau da safe ne ba ta yi wani wankan ba.

Sai wani crop top mai kyau milk color ƙafarta kuma sanye da slippers ɗin Gucci.

Kanta ba kitso tayi parking a tsakiya santala santalan cinyoyinta na ta sheƙi kamar kullum.

''Sannu da zuwa my Neneh.''

''Subhanallahi, Fatima ko fitina? , maza dallah je ki saka tufafi kin bar su lantana a buɗe haka?."

Ɗago kanta tayi a ta kai dubanta wurin Neneh, amma idonta bai sauka kan kowa ba sai wanda ke sanye cikin shigar manyan kaya kansa na sanye da hular nan ta zanna bukar.....

Ta ma rasa mai ke mata daɗi, tana tsaye ta kasa gaba ta kasa baya.

Neneh dai neman wuri ta yi ta zauna tare da faɗin ''Mai kike wani gwaggwale ido kamar kin yi wa sarki ƙarya.''

Duba wurin da Sultan ke tsaye Neneh ta yi, ta ga babu alamar sa, kallon Liyana ta yi tare da ƙara faɗin ''Kin aike sa ne naga baya nan.''

Shiru Liyana ta yi sannan kuma cikin sassanyar muryarta ta ce ''waye shi Neneh?."

''Ke nifa ba tambaya nazo ki min ba, zuwa na yi na sanar miki Umaru ya mutu murus, yanzu daga wurin gaisuwa muke zanje kwaso kaya na na koma can ɗin, Ita kuma Maimu yɑr daƈi miji ta na can tana,suma ita ala dole mijinta ya mutu.''

''Innalillahi wa inna ilaihir rajiun!, Neneh kiji tsoron Allah.''

''Toh yo tsoron ki zanji, ku zubo min abin da ku ka dafa in ci,abinci ko wahala?, abicin gidan rasuwan duk yaji sai kace a gidan yarabawa, toh ina fama da gyanbon ciki ina Ajiddeh da cin fara da mai.''

Liyana ba ta tsaya jin shirmenta ba ta haura ɗakinta haƌe da sanya simple abaya mara kwalliya haƌe da himar sannan ta zira slippers tare da ɗaukan car key.

Ta sauko da ɗan gudunta.

''Ke dai Fatima ba ki da imani, a sanar dake mutuwa amma ko ɗigon hawaye babu balle kuka.''

''Dan kin sanar dani mutuwa sai na kama birgima a ƙasa tun da sunana Ruth?."

''Kar ki zagen.''

''Kyaji da shi kuma.''

Daga haka ta fice daga falon tare da faɗin. ''Salimah ki kula da gidan, ke kuma Neneh idan kin taho ki haɗo min da kayana.''

''Ba ni aka kawo miki yar aiki ba ai.''

Bayan fitar Liyanar kallon Salimah ta yi sannan ta ce ''Wai Salimah da ta tafi da izinin wa ta fita?."

''Neneh dai tare muke anan fa."

''Allah ya kyauta kowa dai fitsararre ne.''

Ko da Hydar yaje office ɗin Abbuhn ma tare suka je gidan rasuwar.

Sannan Abbuh ya ce masa ya kula da harkar komai na office ɗin tun da Sultan ke na Hydar ɗin.

Gidan ya yi maƙil da jama'a saboda Alhaji Umaru mai son jama'a ne sosai.

HYDAR bai iya zama gidan rasuwar ba saboda tausayi matan dake kuka ke basa, ga matarsa sai suma take tun da ya zo aka nufi hospital da ita, amma da rana zai dawo ɗaukan Abbuh.

Liyana kam gudu kawai take shararawa a titi har ta ƙarasa bachirawan, ko ina shiru a unguwar a hankali ta sauko daga motar idanunta duk ƙwalla babu wani alamar tsiwa a tattare da ita, a hankali ta tako har cikin gidan.

Ko ina maƙil yake da yan uwa da abokan arziki, kowa nata jimami Ammi na zaune kusa da Fatima yayarta da suke da uba ɗaya tare da yarta Yusrah, ƙarasawa tayi kusa da Ammin tare da faɗin ''Ammi ya haƙurin mu?."

''Da godiya.'' ta bata amsa a taƙaice.

''Ammi ina Ilham da Mama Maimu?."

''Ke wacce kaliyar sha³ ce da ba ki da hankali sannan kuma ba ki da tunani?, kina ganin halin da suke ciki za ki wani kama tambayar banza da wani wofi.'' inji cewar Yusrah dake zaune kusa da mahaifiyyarta y'ar gidan yayar Ammi ɗin her half cousin sister.

''Karki saki ki ƙara zagina tun da dai ba uwarki na tambaya ba!."

''Bara uba uwata kika zaga?!."

Kallonta Ammi tayi tare da faɗin ''Fatima kar na sake jin bakin ki anan.''

''Ba zan sake magana ba Ammi amma wallahi ta zagan sai na rama.''

Dariya Yusrah ta yi tare da faɗin '' banza kawai mara tarbiyya.''

''Da ni dake idan makaho ya shafa ya san mai tarbiyya da mara tarbiyyar ai, tsohuwar kilaki.''

''Ni kike kira da karuwa?."

Tashi Liyana ta yi haɗe da cire himar ɗinta sannan ta ce ''An kira ki ɗin, ki yi duk uban da za kiyi, ko zan daku ne?."

''Liyana I said ki daina cacar bakin nan ko?." Inji cewar Ammi.

''Ammi can't you see ita ta fara takalata ko uwar ta bata gani da zata hanata faɗe.''

Ammi bata ƙara kallonta ba ta cigaba da lazumin ta.

Yusrah ce ta kawo wa Liyana mari ita kuma ta sa hannu ta kare, kamar ba gidan rasuwa ba haka suka fara dambe a tsakaninsu kamar wasu karnuka.

Yusrah ce ta samu nasarar kama gashin Liyana hakan ya sa ta saki ƙara.

Sannan a hankali Liyana ta gartsa mata cizo, Mama Fatu ce ta zo ta fincike yʻar tata tare da faɗin ''Ke ba kida hankali da za ki biyewa wannan.'' ta faɗa haɗe da fincike Yusrah a hannun Liyana, tun da gaba ɗaya a bedroom na yaran gidan suke.

''Kar ki sake wallahi Mama Fatu ki ƙara zagina, karki ƙara cemin wannan.''

''Kull cire Maman nan kira ni Fatuh mara ɗaha kawai mai suffan shegu.''

''Suffar shegu kam kina ganin yʻar ki kinsan ta fi ni suffar shegu har da na shaiɗanu ba ki ɗaya, ki kalle ni daga sama har ƙasa ban yi ƙari da komai ita kuma yʻar ki fa?."

Ƙanƙance idanunta Mama Fatuh ta yi tare da faɗin ''Ke da aka aurar dake saboda kuɗi fa?.''

''Da kema za ki samu ki aurar da ɗiyarki saboda kuɗi da kin fi kowa murna.'' Liyana ta ƙarashe maganar da tsirawa Mama Fatuh ido.

''Ba dai aure ba?, mu zuba mu gani.''

''Shege ka fasa, in fitsari banza ce kaza ma ta yi mu gani, yʻa ta gama ruɓewa kin zo kina wage wawwaran bakin ki duk kin hanani sukunin."

''LIYAANAA!." Ammi ta faɗa da ƙarfi.

''Ammi ki ƙyale ni.'' ta faɗa haɗe da cuno baki.

''Ikimat a gaban ki yʻar ki ke zagina haka ba ki ce komai ba.'' ta faɗa tana kallon Ammi.

''Ahh wallahi da sauran tarbiyya ta ni bake na zaga ba, aatoh kar ki kaini inda Allah bai kaini ba.''

Jiddah ne da yaji hayaniya ya fara yawa har matan dake waje sun fara shelantawa a tsakaninsu, hakan ya sa shi shigowa cikin ɗakin tare da yiwa Liyanar magana ''Ya Zahra mai kuke yi haka?, ko kun manta wurin rasuwa ne nan ɗin?."

Sassauta muryarta ta yi haɗe da basa haƙuri.

''Toh kar akuma."

''In shaa Allah jiddah.''

Daga haka ya futa daga ɗakin.

Sai data fakaici idon Ammi da Mama Fatuh data ajiye kanta kamar ta Allah, daman Yusrah nada kumatu manya manyan nan, hakan ya sa ta kwaɓe mata fuska haɗe da faɗin ''Shegiyya.''

A fusace ta ɗago kanta saboda yadda masifa ke cinta wayarta ƙirar iphone fourteen promax ta cillawa Liyanar wanda hakan ya sa wayar ta fashe tare da yin blank.

''Wa ya gaya miki ana nufan yʻar gidan Nabil da sharri a wanye lafiya, U la la.'' ta ƙarashe maganar da gwalo da kuma dariya mai cin rai sannan ta fice daga ɗakin.

Ammi ta ma rasa bakin magana ta rasa ya zata yi da lamarin Liyana, ta san wace Mama Fatuh ta san mai za ta iya aikatawa ba ta ƙi ta lalata rayuwar Liya ba .

Tunani sun mata yawa akai berekete, ga mahaifiyyarsu bata farka ba har yanzu Neneh ma shiru bata dawo ba.

Gasu Fati ƙarama har yanzu daga kai order kayan sadakan uku basu dawo ba da ita da ƙanwar Mama Fatuh, Mansura ma bata iso ba (Fati ƙarama ƙanwarta da suke uwa ɗaya uba ɗaya, su biyu mamansu ta haifa).

''Yaro bai san wuta ba sai ya taka.'' jiin kalmar da Mama Fatuhn ta furta shi ya dawo da ita daga dogon tunanin data lula.

Liyana kuwa ko da ta fito daga cikin ɗakin a compound ta yi zamanta tana ƙwalla dan yanzu wani kalar taƙaicin biye wa Yusrah take.

Ga wani tuna marigayi da ta yi, Idan ya na mata wasa tana masa shan ƙamshi idan yana kiranta matarsa ashe dai ba zasu gana ba.

Ta takura kanta wuri ɗaya tana kukanta.

Sallamar da aka yi ta amsa tare da ɗago kanta tana kallon Unaisa da ta janyo wani ɗan trolly fuskarta duk hawaye sakin trollyn tayi tare da rungume Liyanar ta na faɗin ''Papi is gone!.'' haka suka yi ta raira kukan sannan suka kai kayan nasu ɗakin jikoki dake gidan.

''Ina Mama Maimu?." Unaisah ta tambayi Liyanar.

''She fainted kusan sau biyu, because a hannunta wai ya mutu.''

''Allah sarki ya rabbi I need this kind of love.''

Tsaki kawai Liyana taja tare da faɗin ''Zo ki raka ni gidana dan Allah.''

''Awwn kaga masu gida.''

''Y'ar iccar kawai.''

''na kai ki?."

Duk da suna cikin jimami hakan bai hanasu murmusawa ba.

Daga nan suka tashi tare da ɗaukan wayarta da car key ɗinta suka yo waje.

Ko da suka isa ƙofar gidan ma Sultan ke tsaye da Ilham wacce ke sanye da hijaby lemon green da ya haska mata fata.

Kallo ɗaya ta yi musu sai taji ba zata iya tafiya ba hakan yasa ta bawa Unaisah car key ɗin haɗe da nufar wurin da suke tsaye.

Cikin takunta na slay queens in hijaby (😂😂). Ta iso wurin da suke tare da faɗin ''Ilham mai kike a anan.''

''Yaya Liyana tambayarki yake fa, yawwa Yaya Sultan here she is, amma fa as I said she's married, na barku lafiya.''

Kallonta ya yi sosai haɗe da barin jinginar da ya yi wa motar ya dawo yana bawa gidan baya ita kuma ta jingina da motar tare da folding hannunta haɗe da kallon sa da kyau sannan ta ce '' faɗi mai ke tafe da kai am all ears.''

''Liyana how could you?....."

'' How Could I what?....huh.""

Ta faɗa tana hura iska a fingers ɗinta haɗe da ɗage girarta guda ɗaya.

" Got married without telling me?."

Murmushi ta yi mai sauti sannan kuma ta tsuke fuska kafin a hankali ta kuma faɗin ''As you be my papa?."

Ta ƙarashe maganar da murmushi akan fuskarta wanda hakan yayi dai - dai da fitowar Hydar tare da Abbuh saboda bayan yaje office ɗin ya dawo gidan rasuwar da rana saboda mayar da Abbuh wurin aiki.....

To be countinue tomorrow in shaa Allah!!. babu sanya al'amarin pending amarya yanzu 😩□□

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

THE REGRET

(Dana sani).

~PENDING AMARYA CE~

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION✍

(J.W.A)

Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi.✏

With strong passion, we change pain into strength,and dreams into stories. We are Jajirtattu Writers born to share powerful words.

THE NOBLE WRITER'S TEAM

Our strength lies in Dedication

_ Pending Amarya 32_

Ta ƙarashe maganar da murmushi akan fuskarta wanda hakan yayi dai - dai da fitowar Hydar tare da Abbuh saboda bayan yaje office ɗin ya dawo gidan rasuwar da rana saboda mayar da Abbuh wurin aiki.....

Wani kalar kallo ya watsa mata sannan ya kalli Abbuhn da bai ma lura da wa'yanda ke tsaye ba suka wuce cikin motar nasa.

Hararan gefen ido ta wurga masa sannan ta cigaba da magana da Sultan ɗin dake ta faman yi mata magana, amma tasa kanta gefe guda tana wasa da zara-zaran fingers ɗinta.

''Ka gama?, nace ka gama?, ban hanya na wuce.''

Daga haka ta bi ta gefen sa haɗe da shigewa cikin jeep ɗinta.

Acikin motar ma kasa driving ta yi ta rasa mai ke mata daɗi kawai Unaisah ta bawa car key ɗin domin taja motar dan a halin yanzu babu abin da take tunawa kalar rayuwar ta da Sultan and she ended up marrying his elder brother.

''Ya subhanallah.'' ta faɗa a fili.

Sannan ta jinginar da kanta a jikin kujerar motar, kawai tunanin yadda suke soyayya take, the kisses, the hugs, yanzu ai da kunya ta buɗi ido ta ganshi a matsayin ƙanin wanda take aure.

NOTE.

Yʻan mata masu sakarwa samari ragamar jikinsu ku bi a hankali because baku san ya ƙaddara zata kasance da ku ba.

Za ta ji nauyin zuwa gidan surikanta ma bama Sultan ɗin kaɗai ba, Allah yasa ma surutu irin na Sultan ɗin babu wanda ya faɗawa kalar haukan da take yi da shi.

Har Unaisah ta iso gidan bata sani ba sai da ta yi horn, sannan horn ɗin ya fargar da ita daga nisan tunanin da ta lula.

Ko ina na gidan tsaff Salima ta gama gyara ko ina dan yanzu har wajen 4 ta gauta.

Kʻamshin turare ya gauraye ko ina ga wani sanyi da ɗakin ya ɗauka.

Salimah na zaune cikin falon jikinta sanye da hijaby tana wayarta hankali kwance.

Shigowar Liyanar ne ya sa ta katse wayar tare da faɗin ''Aunty Liya sannu da zuwa.''

''Yawwa, mai kika girka?."

''Dambun jollof ne.''

''An bar miki kayan ki, dafa mana pasta kafin mu fito please.''

''Toh Aunty.''

Daga haka suka bar falon ita kuma Salimah ta shiga kitchen domin dafa musu pasta ɗin.

Shigarsu saman ma komai tsaf - tsaf da shi sai ƙamshi yake mai bada nutsuwa.

Sai a lokacin ta kunna wayarta haɗe da faɗawa Lily rasuwar da aka yi musu.

''Hello lily.''

''Bae what's app nah.''

''Wallahi normal.''

''Bae tun safe ake cigiyar ki a online, wai first in history yar Nabil tayi offline for 2 hours.''

''Wallahi My Grandpa just japa recent.''

''Jehooovaaaa, how comes wetin come happen?."

''Person no go die again?."

''Dalla bae am surprised ne ai ta ya Jiddah zai mutu haka?."

''Thunder go fire you, bastard."

''Ahh bae mai na yi kuma?."

''Ba Jiddah ba fa papi.''

sun daƈe suna hirar sannan ta katse wayar.

Kaya kusan kala goma ta ɗiba da hijjabai biyar sai slippers biyu, sai laptop da kuma charger da brush da soson wanka da sabulanta da kuma mayukanta na jiki.

''Wannan kayan fa hajiyata.'' Unaisah ta faƈa tana ƙafe Liyanar da eyes.

''Na gidan rasuwa ne mana.''

A daidai nan Salimah ta yi sallama haƈe da shigo da pasta ɗin daya ci crab fish da gasasshen kaji, sai ƙamshi yake.

''Ga abincin nan.''

''Godiya muke hajja Salimah.'' Liyanar ta faɗa tare da janyo plate ɗin.

Salimah bata ce komai ba ta fita daga ɗakin.

Abincin suke ci hankali kwance suna hirar su gwanin burgewa.

A haka har suka gama cin abincin sannan ta shiga toilet ta yi wanka haɗe da shiryawa cikin simple dress mara hayaniya.

Ta yi kyau sosai ga yamma ta yi dan an fara kiran magriba.

Key ɗin ta ɗauka haɗe da trolly ɗinta sannan ta fito parlourn Salima na zaune ta na kallo.

''Mai kike yi tun ɗazu haka a zaune ba ki shirya ba?."

''Aw!, wai Aunty da ni za ki tafi.''

''Malama ba zan tsaya dogon turanci ba, taho mu tafi.''

''Toh.''

Daga haka Salimah ta shiga ɗakin ta in less than two minutes ta fito da wani ɗan kit.

daga haka suka fita daga falon tare da nufar motar Liyanar.

Wani kalar gudu take shararawa wanda ba'a jima ba suka iso ƙofar gidansu Ammin dai-dai kiran sallar isha.

Gidan kowa dai shiru babu mai tankawa kowa Unaisah da Salimah ne suka kamo mata trolly ɗinta suka kawo mata shi har cikin ɗakin.

Sannan ita ma ta mara musu baya.

Yusrah ce zaune kan gadon dake ɗakin Sandy Rash da Classy Reeda na zaune kusa da ita duk suna hira sama- sama.

Shigowar Unaisah da Liyana ne ya sa su farinciki haɗe da baƙin ciki duk a lokaci ɗaya.

Sannan kuma suka fara hira.

ILY ce ta ƙaraso cikin ɗakin haɗe da ajiyewa kowa abincin sa sannan kuma ta zauna tare da ƙurawa Liyana ido.

''Aunty Liya ko ki neme ni.''

''Sannu Ikimat, ko nace sannu Nabil.''

Matsowa ta yi kusa da Liyanar ta ɗan dake ta sau uku a ƙirji tare da faɗin ''Blood.''

''Sai dai period ba blood ba.''

''Ke dai da bak'ar magana, ance ki je ki ɗauki abincin ki.''

''Wa ya dafa?.

''Mama Fatuh ce.''

''Ill!, never!."

''Mai kike nufi?."

''Ba zan ci ba wallahi.''

Yusrah da tun lokacin da Liya ta shigo take jin wani kalar baƙin ciki na lulluɓe ta ne ta ce ''za ki ci kaza kazanki.''

''Toh mai kike ci na baka ba falling down.'' Liya ta faɗa haɗe da murmusawa.

''Uwarki za'a kwaɗan ta min naci.''

''Ahh wallahi kin yi kala da mayu daman, ni nafi ƙarfin na yi dake sai dai nayi da uwarki, dan haka ki aiko min ita da ita zan yi.''

''Bara uba.....''

To be countinue tomorrow in shaa Allah!!. babu sanya al'amarin pending amarya yanzu 🙏🏻

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

THE REGRET

(Dana sani).

~PENDING AMARYA CE~

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

THE NOBLE WRITER'S TEAM□

This page is dedicated to UNAISAH (Miss chubie)□○

Barka da jummah my lovely fans □□

•°•°• Pending Amarya ce 33 •°•°•

''Ahh wallahi kin yi kala da mayu daman, ni nafi ƙarfin na yi dake sai dai nayi da uwarki, dan haka ki aiko min ita da ita zan yi.''

"Bara uba....."

''Bara uba, dani kike?."

''Ba ki ji mai nace ba da uwarki nake.''

Kafin Yusrah ta ƙara wani maganar su Rashanda da Unaisah suka fara bada haƙuri da haka dai kowa ya yi shiru.

Sai tsaki dake tashi a ɗakin different types of sounds.

Hayaniyya ke ta tashi a tsakar gidan wanda ke nuna alamun wani ne ya ƙara zuwa a cikin dangin.

Kowa ya shirya cikin kayan baccinsa, banda Liya kaɗai dake zaune ta na aikin chatting da wata ƴar class ɗinsu ta secondary school da suka haɗu ta IG (Instagram).

Sai da ta ga 11 ta ɗan gauta sannan ta kama cire kayanta haɗe da ɗaura towel ɗinta domin ta ɗan watsa ruwa.

Cikin ƙanƙanin lokaci ta fito ɗaure da towel haɗe da goge jikinta tare da sanya kayan baccinta, haɗe shafe jikinta da turarenta na Almiski wanda ta saba shafawa.

Ko da ta kai dubanta kan gadon ma har kowa ya yi occupying wurin kwanciyyar, duk sun fara bacci amma ban da Unaisah da take latsa laptop ɗinta ta na haɗa wani rahoto da zata bayar a gobe.

''Toh ni à ina zan kwanta?." Ta faɗi hakan tare da kai dubanta zuwa wurin Yusrah data baje a kan gadon.

Unaisah ce ta gyara zaman glasses ɗinta sannan ta kalli Liyanar haɗe da faɗin ''Ki ce musu su gyara kwanciyyarsu because ni ina gamawa a ƙasa zan kwanta ke kuma naga you're not a fan of kwanciyar ƙasa.''

''Ba zan iya kwanciyya a ƙasa ba just tell this girl to shift for me, duk ta cinye wurin.''

''Ni fa Liya karki ce za ki yi faɗa da daddaren nan idan ma falo ne kije ki kwanta a coach ɗin palo ko ki kira mijinki ya zo ya ɗauke ki ki koma gidanki.''

''Babu wanda zan kira a ɗakin nan zan kwana no matter what wallahi.''

''Ai shikenan.'' daga haka ta cigaba da danna laptop ɗinta.

Fincike filon da Yusrar ke kwance ta yi wanda ba shiri ta tashi daga barcin, wanda hakan ya saka faɗa a tsakaninsu, Neneh ce ta shigo cikin ɗakin tare da mutan gidan, su Rashidat da Faridat duk sun tashi daga barcin, Ilham kuma daman a wurin su Ammi ta kwanta duk tare suke da su Nenehn.

''Mai ya faru haka da ba zaku bari muyi bacci ba shima Umaru ya samu salama a inda yake kwance eh?."

Yusrah ce ta doka wani ɗan banzan tsaki haɗe da hararar Nenehn.

''Ai ba dake nake ba cangali tsone, da jiƙata nake.''

Rashidat ce ta yi wiƙi - wiƙi da ido tana kallon Nenehn sannan kuma a hankali ta buɗi baki ta ce ''Neneh bacci muke hayaniyar su ce ta tashe mu.''

''Duk yadda aka yi Ikimat kin ci zabi da cikin yar nan, taho muje can ɗakin Maimun ki kwanta acan ki ƙyale wannan kayan wankin mana.''

Liyana ce ta kalli Nenehn haɗe da faɗin ''Wallahi Neneh babu inda zani, kuce mata ta matsa min na kwanta tun da ba na ubanta bane.''

Yusrah ce takalli mutanen ɗakin kafin kuma ta murmusa tare da faɗin ''A gaban ku dai take zagina kuna ji kuna gani ko?."

Ilham da tun ɗazu abin ke sosa mata rai ne ta fincike Liyanar daga ɗakin.

''Ily ki cika ni kafin na wanka miki mari.''

Ko kallonta Ily ba ta yi ba ta shigar da ita ɗakin nasu, sannan a hankali ta fara magana ''Wai ke ba za ki nutsu ba fisabilillahi, kullum akan ki Ammi ke kukawa, ki

tsaya mana ki duba lamarin nan, ke idan ta miki magana ko ta tsokane ki ba za ki iya over looking ba kawai ki barta, dole sai kin shiga harkokin ta?, haka jiya da yamma Sultan na waje kuka yi ta dambe haka maƙota ke ta yayatawa, just ki barta please.''

Ta ƙarashe maganar haƌe da miƙa mata ruwan sanyi domin ta sha.

Nannauyen ajiyar zuciya ta sauke sannan ta ce ''Naji amma wallahi aka min sai na rama.''

Daga haka suka kwanta haƌe da yin bacci.

Washegari da safe ma ko kallonta bata yi ba kuma Mama Fatuhn ce ke raba abincin safen fankaso da kunu, bata bi kan abincin ba ta sa Salimah komawa can gidan ta yo mata girki ita da su Unaisah suka ci kafin ta tafi aiki.

Ko ina na gidan shiru dan Liya baccinta ta ɗinga shararawa.

A haka rayuwa ta cigaba kewar Alhaji Umaru na yaƌewa a zukatan su yayin da yau ake sadakar bakwai na marigayin.

Tun safiyar yau Jiddah da Abbhi ke zuwa gidan marayu da talakawa marasa ƙarfi ake ta rarraba musu kayan abinci haƌe da tallafawa masallatai.

Gidan ruwa da ake siyarwa da masu ga-ruwa ruwa sai da suka rarraba musu kuɗi sosai domin al'ummar musulmi su amfana a kuma raba musu shi kyauta.

Sosai suka kashe kuɗi akan sadakar bakwai ɗin yau.

Mama Maimu kuwa a hospital results sun nuna da cewa hawan jininta ne ya yi mugun tashi, domin sai yau ta farfaɗo.

Tun da ta farfaɗo ɗinma kuka kawai take Neneh na bata haƙuri, amma sai ya ɗan ƙara warware wa zata dawo gidan.

Mr Ali namu kuwa shima wurin bada nashi gudunmawa ba'a barshi baya ba dan sosai ya turawa Jiddah kuɗi a account ɗinsa.

Ga kullum Mami sai ta takurasa akan ya kawo mata Liyanar yanzu almost wata uku da auren basu zo ba in banda shi da yake sintiri, idan Sultana ta ce za taje kuma sai ya ce zai karya ta idan ta taka zuwa gidan.

Yau dai kam su Liyana sai ƙasa ƙasa ake da kai dan su Mami da Abbuh zasu zo gaisuwa har ma da Hydar ɗin.

Ita wani kalar kunya take har addu'a take Allah ya sa kar azo da Sultan.

Ammi ce keta bawa Salimah da Ily order su ɗan dafa abinci saboda baƙin da za'a ɗan yi.

A hakan dai har suka gama girkin.

Ƙarfe sha biyu dai-dai su Mami da Abbuh da Hydar da Assultanah suka hallaro.

Gidan da ɗan hayaniya amma ba sosai ba.

A haka har suka shigo cikin gidan, palon Umaru ɗin da ake tarban baƙi.

Basu wani jima ba Ammi da Neneh suka shigo haɗe da gaisawa dasu Mamin, shi dai tun da ya kalli Ammi sau ɗaya ya siddar da kansa a ƙasa, bai yarda ya sake ɗagowa ba.

Ita ma ta lura da hakan yasa suna gama gaisawa ta ce musu zata aiko musu Liyanar sannan ta yi ficewarta.

Neneh kam in banda bada labarin rasuwar Umaru ba abin da take yi.

A haka har ta shigo cikin parlourn cikin siririyar muryarta mai kama da busawar sarewa tare da yin sallama wanda ya amsa ilahirin ɗakin.

''Yawwa yɗar halal ta ƙi ambato.''

Neneh ta faɗa haɗe da kallon Liyanar.

Aƙasa ta durƙusa haɗe da gaida su Mami da Abbuh ɗin.

Amsawa suka yi haɗe da shi mata Albarka sannan suka yi mata ya haƙuri.

babu abin da suka ci a abin da aka kawo musu.

Bayan shiru ya ɗan ratsa falon, kanta aƙasa tana wasa da diamond ring ɗin hannunta, shikam Hydar ko kallonta bai yi ba ya na ta operating wayarsa ne kawai.

Cikin sanyin murya Sultanah ta ce ''Aunty you're soo beautiful Ma shaa Allah.''

''Thanks little.'' Liyana ta amsa mata a taƙaice.

Gyaran murya Mami ta yi tare da faɗin ''yanzu daughter yaushe za ki zo mana?."

Murmushi kawai ta yi mai sanyi ba ta amsawa Mamin ba.

Neneh ce ta amshe da faɗin ''dake ake mai farin fuska kike ta nannoƙewa kamar ta Allah.''

Hararar gefen ido ta sakarwa Nenehn akan idon Hydar da ya ɗan gyara zaman sa.

Sannan kuma a hankali ta ce ''Mami shi ya hanani zuwa.''

ɗago kansa ya yi tar- tar akan kyakkyawar fuskar ta sannan kuma ya ɗauke kan nasa daga kanta.

''Nasan za'a rina ai.'' Mamin ta faɗa, shi dai bai tanka musu ba a haka har suka shi musu albarka, haɗe da ficewa a ɗakin har da Neneh.

Mamin da Sultana cikin gidan suka ƙarasa, shi kuma Abbuh cikin yan makoki ya shige abinsa.

Gajiya ta yi da zaman hakan yasa ta tattara hijab ɗinta ta tashi da niyar fita daga parlourn.

Cikin Muryarsa mai amo da daɗin sauraro ya ce ''Da izinin wa kika fita?." Turo ɗan ƙaramin full lip ɗinta ta yi tare da faɗin ''Oho."

Daman a wajen ƙarshen kujera yake ta wajen ƙofa, hakan ya sa ya saka mata ƙafa ta yi tuntuɓe haɗe da faɗuwa a ƙasan.

Wani kalar ƙara ta saki tare da yarfa hannunta.

Manunin hannunsa ya saka akan bakinsa alamar ta yi masa shiru, sannan ya rage tsayinsa haɗe da tsugunnawa har suna iya jiyo numfashin junansu.

''Bayan yawace -yawacen ki harda iya haɗa ɗa da mahaifanshi kika iya ko?."

Kanta ta matsar gefe haɗe da murkuɗa masa baki.

Hannunsa na tsakiya da na ƙarshe ya sa tare da ɓalle mata baki, wani ƙaran ta saki tare da yunƙurawa za ta tashi hijab ɗinta ya ƙara faɗar da ita a ƙasa.

Shi dai bai ƙara mata magana ba ya ɗauki wayoyinsa haɗe da fita tsakar gidan da hayaniya ke ta tashi an ɗaukewa Mama Fatuh kuɗinta har dubu ɗari biyu da hamsin, hakan ya sa take ta zage - zage kamar ta ari baki.

Shi dai Hydar kallo ɗaya ya mata ya ɗauke kansa haɗe da sa kanshi ya fice daga gidan gaba ɗaya.

Da ƙyar ta tashi daga ƙasan haɗe da fitowa tsakar gidan da akwatin ta yake a yashe a tsakar gidan duk an mata fatali da kayanta.

Ilham ta tafi school Unaisah na aiki, su kuma su Reeda da Sandy sun tafi siyayyan komawarsu.

Umma Mansura kuma da Ammi na tsaye cirko -cirko yayin da Neneh ta tafi raka su Mami domin tafiya dan bata san wainar da ake toyawa ba.

Wani kalar mari Mama Fatuhn ta ɗauke ta da shi haɗe da faɗa mata suna ɓarauniya da kuma baƙaƙen maganganu ita ma Yusrah suka haɗe suna ta zagin Liyanar, har Umma Mansura zata shigo Ammi ta yi saurin girgiza mata kai.

Wani kalar mari Neneh da shigowarta kenan ta wankawa Mama Fatuhn tare da faɗin ''Ke kinsan waye mahaifinta wurin kuɗi, kin san kakanta wurin kuɗi, haka zalika kin san mijin da ta aura ba kaɗan bane ba a wurin kuɗi kowa anan zai shaida Alhaji Ahmed Qasim Kyari, ke da kallo ɗaya za'a miki a gane talauci gaba da baya sha ³ , so so so mai kama da biri.''

Baƙin ciki ma ya hana Liyanar magana sannan a hankali kuma ta cire himar ɗinta haɗe da jacking ɗin Mama Fatuhn ta kanainayeta kamar macijiya.

Kowa sai dukan hannun Liyana yake amma taƙi sakin Mama Fatuhn ta wani kalar shaƙe mata wuya.

Idanun Liyanar ya yi wani kalar ja.

Jikin Neneh wani kalar rawa yake dan ita a tunaninta Liyana jinnu ta tayar.

Duk da hammatan Mama Fatuhn ta hana ta sakat amma haka ta cigaba da naniƙe mata.

Hydar da zuwan sa gida kenan daga mayar da su Abbuh gida ya ji wayarsa na ringing wani kalar tsaki yaja dan atunaninsa Amir ne ko Sultan hakan ya sa shi yaƙi ɗagawa, sai da ya ga wayan na ƙara sosai hakan ya sa shi ɗaukan wayan amma sai kuma ya ga sunan Neneh ajiki.

Bayan ya ɗaga a kiɗime ta fara magana ''maza ka juyo ka dawo gidan nan, fitinar matarka zai sa ta yi kisa.''

Kalmar kisan da yaji ne ya sa shi ajiye wayar haɗe da ɗaukan key ɗin motarsa ya fara tuƙi a million.

Ko lokacin da ya iso har an samu nasarar ɓanɓareta daga jikinta dan Mama Fatuh sai da ta suma dan wahala.

Liyana na zaune sai huci take.

Abbhi ne ya zo ya zauna a kusa da ita wanda hakan yasa hawaye zuba daga cikin idanunta haɗe da rungumesa.

''Abbhinaaa ni ka kira min lawyer na, wallahi sai na kai wannan maganar ƙara, mai zan yi da 250k, let her check my account balance kuɗina 2 million za'a ƙara ya zama 20 million, Abbhi 250k is a chicken change a wurina wallahi."

''Is Okay, duk wanda ya taɓa min ke nayi alƙawarin bi miki haƙƙin ki daman ko waye shi, i don't care about the closeness, zata fuskanci hukunci, dai-dai gwargwadon abin da ta aikata miki kinji.''

Gyaɗa kanta kawai ta yi ba tare da ta kalli wa'yanda ke wurin ba.....

To be countinue on Monday in shaa Allah!!. babu sanya al'amarin pending amarya yanzu 😩□□

Durrah Hydar.✍

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

THE REGRET

(Dana sani).

~PENDING AMARYA CE~

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION✍

(J.W.A)

THE NOBLE WRITER'S TEAM

Pending Amarya 34

''Abbhinaaa ni ka kira min lawyer na, wallahi sai na kai wannan maganar ƙara, mai zan yi da 250k, let her check my account balance kuɗina 200k (last page na samu typing error ban lura ba). za'a ƙara ya zama 20 million, Abbhi 250k is a chicken change a wurina wallahi."

''Is Okay, duk wanda ya taɓa min ke nayi alƙawarin bi miki haƙƙin ki daman ko waye shi, i don't care about the closeness, zata fuskanci hukunci, dai-dai gwargwadon abin da ta aikata miki kinji.''

Gyaɗa kanta kawai ta yi ba tare da ta kalli wa'yanda ke wurin ba.....

Neneh da sai yanzu jininta ya ɗan sauko ce ta ce ''Alhamdulillah ga Hydar ɗin ma ya ƙaraso, sai ka zo ka ɗauki wannan fitinanniyyar matar ta ka, wallahi tun da Ummaru ya mutu, Liyana ba ta bar shi ya ji daɗin mutuwarsa ba kullum cikin fitina take, ai wannan ba Fatima ba ce ba fitina ce wallahi.'' ta ƙarashe maganar tare da direwa Hydar ɗin trolly ɗinta.

Murmushi kawai ya yi sannan ya durƙusa ya na mai gaishar da Abbhi dake kusa da Liyanar.

Babu yabo babu fallasa ya amsa haɗe da tambayarsa ya aikin.

Bayan sun gama gaisawar ya ɗauki trolly ɗin haɗe da sawa acikin booth, ko da ya dawo cikin gidan Neneh na ce mata ta tashi ta bi mijinta ƙi tayi, wai ita alankatafir ba zata bi shi ba.

Sai da Abbhi ya lallashe ta haɗe da tura mata 5 million a account ɗinta sannan ta tashi jiki a saɓule, haɗe da bangaje Mama Fatuhn da ta miƙe daga sumanta da ta farfaɗo, duk a gaban Hydar ɗin.

Bayan motar Hydar ɗin taje ta zaga ta zauna duk su Abbhi da Neneh suna kallonta, shi ma Hydar ɗin bai yi magana ba ya shige gaban motar haɗe da yi masa key.

Sai da suka fita daga unguwar sannan ya juyo da fuskarsa zuwa inda take zaune ta na hawaye.

Parker motar ya yi cikin muryarsa mai amo ya ce ''Uban waye driver ɗin ki?."

Ko kallonsa ba ta yi ba ta cigaba da goge hawayenta da hanky ɗin da Abbhi ya bata.

''Ba kya ji ne?."

''Leave me alone tun da dai da na shigo motar nan ban maka magana ba.''

''Zan bubbuge miki baki idan ki ƙara min magana without a bit of respect, dawo front sit kafin na ba ki correct slaps.''

Tsaki ta daka sannan ta buɗe motar haɗe da shigewa front sit ɗin.

Shiru ne ya ratsa cikin motar sannan a hankali ya juyo da kansa ya kai duban sa gareta tare da faɗin ''Amma wallahi ba ki da kunya, yanzu saboda rashin ɗan ido da mahaifiyyar ki kike faɗa harda bangaza?, see the way she's shouting time ɗin da muka shigo, wallahi ina ganinta na san ita ce mamanki, ashe dai tsotsa ki kayi a nono.'' ya ƙarashe maganar haɗe da fuskewa kamar ba shi ya yi ba.

Juyowa ta yi ta kallesa haɗe da haɗiye miyau sannan ta ƙara mayar da kanta gefe.

''Mai sa ba za kiyi magana ba?, sosai that lady deserve to be your Mom, gaskiya aje ayi DNA TEST because albasa ba tayo halin ruwa ba, Dan dai kar nayi saɓo da nace samun ki a matsayin ya' da Ammi ta yi shi ne jarabtar ta.''

''Ya kuma ishe ka haka."

''Shut up while I'm talking joor, sai shegen iyayi, kamar kina da wani wayewa bayan kaff arewa babu mai daƙiƙanci kamar ke.''

''Ka na kai ni bango fa?."

''Kin manta ƙarshen duniya nake kaiki.''

''Hmm.'' ta faɗa haɗe da cije lips ɗinta sannan ta cigaba da girgiza ƙafafunta, alamar masifa na cinta.

Daga ƙarshe shiru ne ya ratsa motar fuskar kowa a tamke barimma na Hydar.

Ko da suka isa gidanma komai neat kamar suna gidan, sai a lokacin take tunawa da wata Salimah.

Tsaki taja tare da hawa stairs ɗin ta bar shi a falon.

Remote ya ɗauka haɗe da furta ''Ƙazama.''

Liyana bayan ta ƙarasa ciki ma wayarta ta ɗauka haɗe da kiran Salimah akan ta dawo gidan.

Wanka ta shiga, ta daɗe a toilet ɗin sannan ta fito haɗe da goge jikinta da towel sannan ta fara shiryawa cikin mini skirt da kuma wani polo top.

Polo ɗin babba ne sosai dan kar ya takurata hakan ya sa ta tattara shi haɗe da kulle top ɗin sai ya tsaya a dai-dai cibiyarta. Wanda ya ƙara fito da farin shafaffen tummy ɗinta.

Slippers ta saka white color, haɗe da ɗaura normal hula akanta.

Shigar ya mugun yi mata kyau sosai, sannan ta cilla mint chewing gum ɗinta a bakinta da ya sha lipstick mai ƙamshin pineapple.

Neman wuri ta yi ta kwanta ta na daddana wayar hannunta dan yunwa take ji amma ta rasa ta ya za ta shiga kitchen ɗin ko noodles ta dafa.

Gashi har an fara kiran sallahr asar.

Ganin zamanta haka yunwa zai hallakata ya sa ta tashi daga kwancen da take haɗe da fita parlourn.

Ko da ta fita ma baya falon hakan ya saka ta shigo da ɗan gudunta cikin kitchen ɗin.

Tsaye ya ke ya ɗaura noodles a transparent glass pot ɗin dake kan standing gas, ya yi folding ɗin hannunyensa ya ɗan jingina da kitchen island ya na mai ƙurawa tukunyar ido.

Kallonsa ta yi daga sama har ƙasa, ba kayan safe bane ba ajikinsa, wannan karon combat ne ajikinsa sai t shirt milk color a gaban rigar an rubuta _NEVER STOP ROMANCE._ da black ink.

Kallon fuskarsa ta yi tare da ɗan ƙure sa da manyan idanunta, gaskiya guy ɗin ya haɗu ya na da pointed nose, ga gemunsa baƙi siɗik, idanunsa manya ne sosai, ga wani ɗan baƙi yale - yale dake wurin idanunsa da suka ƙara masa kyau.

Lips ɗinsa pink ne sosai musamman na ƙasa.

''What are you staring at?."

''Mai za'a kalla anan ɗin?."

Tana faɗin haka ta buɗe fridge haɗe da ɗaukan hollandia strawberry yourghurt ɗinta.....

Na gaji mu ƙarasa gobe in shaa Allah please

To be countinue on tomorrow in shaa Allah!!. babu sanya al'amarin pending amarya yanzu 😩□□

Durrah Hydar.✍

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

THE REGRET

(Dana sani).

~PENDING AMARYA CE~

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

THE NOBLE WRITER'S TEAM□

Pending Amarya 35

Kallonsa ta yi daga sama har ƙasa, ba kayan safe bane ba ajikinsa, wannan karon combat ne ajikinsa sai t shirt milk color a gaban rigar an rubuta _NEVER STOP ROMANCE._ da black ink.

Kallon fuskarsa ta yi tare da ɗan ƙure sa da manyan idanunta, gaskiya guy ɗin ya haɗu ya na da pointed nose, ga gemunsa baƙi siɗik, idanunsa manya ne sosai, ga wani ɗan baƙi yale - yale dake wurin idanunsa da suka ƙara masa kyau.

Lips ɗinsa pink ne sosai musamman na ƙasa.

''What are you staring at?."

''Mai za'a kalla anan ɗin?."

Tana faɗin haka ta buɗe fridge haɗe da ɗaukan hollandia strawberry yourghurt ɗinta.

''Leave my presence.'' ya faɗa cikin Muryarsa mai amo.

''Nifa da na shigo ban maka magana ba, yadda ka shigo girki nima girkin zan yi.''

''I said leave!." Ya ce tare da ƙafe ta da idanunsa.

''Buh I did nothing.''

Ta faɗa ta na marairaice face ɗinta dan ita yanzu har ga Allah guy ɗin burgeta yake.

Bai ƙara tanka mata ba ya nufi wurin dish rack haɗe da ɗaukan plate tare da juye noodles ɗin aciki.

Stool ɗin mini dinning table ɗin dake kitchen ɗin ya janyo haɗe da fara cin noodles ɗin sa hankali kwance.

Bata ƙara kallonsa ba itama ta ɗaura na ta abincin, ta yi shi da romo sosai ga yaji da ta zuba mai shiga maƙogwaro dan shi ma dakewa ya yi kawai ya zauna.

Juye noodles ɗin ta yi cikin ceremic plate da sai swimming suke kamar kifaye acikin red sea, sannan ta zo ta wuce ta bayansa daman da hannu ɗaya ta riƙe plate ɗin ga shi ceremic ne ya ɗauki zafi sosai zafin ne ya rinjaye hannunta hakan ya sa plate

ɗin ya suɓce mata sai ga romon noodles da shi kansa plate da abin da ya ke cikinsa a bayan Hydar.

Ƙara ta saki haɗe da kallonsa sosai, sai kuma ta ɗauke kanta haɗe da tsallake noodles ɗin da niyar fita daga kitchen ɗin.

Cikin muryarsa mai amo da taushi tare da ɓacin rai ya ce ''You did it deliberately right?."

Juyowa ta yi ta ƙafe shi da idanunta sannan kuma ta cigaba da tafiya.

''Ko da wasa kika saki kika fita a kitchen ɗin nan sai jikin ki ya faɗa miki.''

''Toh ni mai na maka?."

''Gidanku kika min, za ki zo ki kwashe wannan abin da kika zubar ko saina illata ki da yamman nan.''

''Toh ba kai ne ka tsaya a hanya ba, shi yasa na na juye maka.'' ta ƙarashe maganar haɗe da yin ƙat - ƙat - ƙat da chewing gum ɗin bakinta.

HYDAR da yajin ke ta masa nasiha a jiki ne ya ta shi daga zaunen da yake, tashin da ya yi ne ya sa ta arce da mugun gudu tare da yin up stairs.

Wani kalar tsaki ya ja tare da yin ɓangarensa, cire kayan jikinsa ya yi da duk yaji ya gama zagaye ko wani angles na bayansa.

Yana cire kayan ya na tsaki sannan cikin wata kaliyar shaƙaƙƙiyyar murya wadda ba ta fita sosai ya ce '' Wallahi this girl no go make heaven at all, just take a look at.'' ya ƙarashe maganar ya na duba bayansa a madubi haɗe da yin tsaki a karo na ba adadi.

Da ruwan sanyi ya yi wanka haɗe da kwanciyarsa because already ya yi sallar Asr.

For almost hour ya na kwance ba bacci ya ke ba, wayarsa da ke kusa da shi ta ɗauki ringing.

Ɗaga wayar ya yi sannan ya amsa sallamar da Amir ke yi masa.

''Man ga mu a street ɗin gidanka ni da Ummi.''

''Okay.''

kawai ya amsa a taƙaice.

Ta shi ya yi haɗe da zira jallabiyarsa maroon color haɗe da saka normal Muslim cap, tare da zira slippers ɗinsa ya nufi downstairs.

As usual ko ina ƙamshi buh the living room is more neater than some hours ago.

Kamshi yake ji na fita daga kitchen ɗin, very classic aroma.

Just mind ɗinsa ya bashi cewa Salimah ce ta dawo.

Kiran sallar da ake a masallacin street ɗin ne ya sanya sa nufar compound ɗin ya yi alwala haɗe da fita masallacin street ɗin.

Bayan ta shiga ɗakinta ma ranta fess, dan ita yanzu duk abin da zai janyo mata hankalinsa shi take so a yanzu, dan all of the sudden son yaron nan ya gama da ita, she can feel it sosai a yanzun.

Wanka ta ƙara yi bayan shigarta ɗakin sannan ta ƙara shiryawa cikin shigarta na kullum wato palazzo trousers da long sleeve shirt white color.

Zira slippers ɗinta kawai ta yi sannan ta fara gyara cikin gidan, sai da ko ina ya ɗauki ƙamshi sannan ta shiga kitchen ta fara ɗaura abinci mara nauyi.

Chips ne ta soya sannan ta haɗa da miyar Sauce, sannan ta nufi dinning room ta jera komai kan dinning ɗin dan hakan nan kawai yau take son gyara gidan.

Ta na gama jerawa ta nufi hanyar ɗakinta ta ƙarayin wankan haɗe da yin sallar magrib sannan ta saka wani Classic Egyptian abaya da ya gaji da haɗuwa black color.

Wanda ya ƙara haskaka fatar ta.

Lipstick mai ƙamshin pineapple ta shafa a saman tsararren laɓɓanta, sannan ta ɗaura mayafin rigar haɗe da saka slippers tare da ɗaukan phones ɗinta ta nufi hanyar falo.

Zama ta yi haɗe da kunna tashar Aljazeera dan yanzu kewar gidan rasuwar ma take dan da yanzu suna ta kwasar cacar baki da wannan lutiyar matar, mai siffar gorilla.

Sallamarsa ce ta katse mata tunaninta, wani jaka ne a hannunsa wanda dukkanin alamu sun nuna na mace ne , macan ma Uwa.

''Welcome to my home Ummi.'' kalmar da ya sake faɗa ne bayan sallamar ya dawo da ita daga tunaninta.

Muryar matar ne dake cike da sanyi ta ce ''Ma shaa Allah Son gida ya yi kyau sosai.''

Ɗago kanta ta yi suka haɗa ido da matar dake sanye da lifaya masu kyau, hakan ya sa ta tsugunnawa haɗe da gaisheta cikin girmamawa haɗe da amsar jakar dake hannun Hydar ɗin.

Wani kalar harara da ya watsa mata ne ya sanya ta ja gefe haɗe da ƙara yiwa Ummin sannu da zuwa, sannan ta nufi hanyar kitchen.

Cikin mintuna ƙalilan t a haɗa komai cikin wani resin tray sannan ta ɓito falon haɗe da ajiye tray ɗin sannan ta ƙara musu sannu da zuwa.

Ummi kallonta kawai take haɗe da yi mata zallar murmushi.

Dan wannan karon harda Amir ta tarar a falon ya na ta washe mata baki.

''Follow me.'' shi ne abin da ya faɗa haɗe da yin upstairs.

A hankali itama ta bi shi, adaidai corridor ɗin ɗakinsa ya tsaya sannan ya ce '' mai Salimar ta dafa?."

''Salimah ba ta dawo ba ni na dafa.''

''Mai kika dafa ɗin?."

''Abinci mana.''

''Okay!, kin ga matar dake falo?."....

Bai ƙarasa ba ta ce ''Na ganta mana.''

''Toh Maman Amir ce, also my Mom, Soo ki shiga kitchen ki dafa mata abinci, Heavy food nake nufi.''

''Buh ko thirty minutes ba'a yi ba da na gama wancan abincin and it's tastes good.''

''I don't care about the good, just do as I said.''

Har ya juya zai ta fi ta ce ''Ni ba zan iya ba, ko a gidanmu ba na girki, wannan ɗin ma dan kar na kashe kaina da yunwa shiyasa nayi.'' ta ƙarashe maganar ta na wasa da diamond ring ɗin dake sanye da ring finger ɗinta dan wayarta a falo ta bar shi.

''Ba shakka ai a maganar ki dan kin ce ba kya yi a gidan ku, kin ga yadda nake cikin fushin nan idan ba kiyi abin da na saki ba wallahi sai na lahira ya fi ki jin daɗi.''

''Wai kai ba ka san wasa ba.'' ta faɗa haɗe da tattare abayarta tayi hanyar fita daga corridor ɗin.

Har ta sha kwana sannan ta kuma dawowa.

''Toh amma kuma babu nama.''

''Ke ba mace ba ce?."

''Sai aka ce na saida nama?.....''

Kwana biyu kun ji ni shiru 😩Temu ne ya tiso ni gaba.

Durrah Hydar.✍

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

THE REGRET

(Dana sani).

~PENDING AMARYA CE~

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

THE NOBLE WRITER'S TEAM□

Pending Amarya 36.

''Buh ko thirty minutes ba'a yi ba da na gama wancan abincin and it's tastes good.''

''I don't care about the good, just do as I said.''

Har ya juya zai ta fi ta ce ''Ni ba zan iya ba, ko a gidanmu ba na girki, wannan ɗin ma dan kar na kashe kaina da yunwa shiyasa nayi.'' ta ƙarashe maganar ta na wasa da diamond ring ɗin dake sanye da ring finger ɗinta dan wayarta a falo ta bar shi.

''Ba shakka ai a maganar ki dan kin ce ba kya yi a gidan ku, kin ga yadda nake cikin fushin nan idan ba kiyi abin da na saki ba wallahi sai na lahira ya fi ki jin daɗi.''

''Wai kai ba ka san wasa ba.'' ta faɗa haɗe da tattare abayarta tayi hanyar fita daga corridor ɗin.

Har ta sha kwana sannan ta kuma dawowa.

''Toh amma kuma babu nama.''

''Ke ba mace ba ce?."

''Sai aka ce na saida nama?.....''

Kallonta kawai yayi haƈe da ƈauke kansa tare da shigewa ƈakinsa dan canja kayan jikinsa.

Ko da ta fito matar da Amir na zaune kan cushion ƈin falon.

''Sannu Maa.''

''Yawwa sannu daughter, Allah ya miki albarka.''

Murmusawa Liya ta yi tare da faƈin ''Amin Maa.''

Ɗaukar wayarta ta yi daga wurin haƈe da shiga kitchen tsayuwar mota ta ji a compound ba ta damu da ta leƙa da ta ga su waye ba, sai da ta ji sallamarsu Unaisah, Reedah, Sandy, da kuma Ily har da kuma Salimah.

Ta dai ji suna gaisawa da su Amir sannan anyi directing ƈinsu zuwa wajen da da take.

''Yaya, ya kike naji wai inji Ammi ba ki da lafiya.''

''Don't worry yourself I'm okay ai yanzun.''

Idanunta ne suka sauka kan Salimah da take ta danne dariyarta, Liyana wani kallo ta wurga mata haƈi da faƈin ''Almura, sai ki zo ki dafawa baƙi tuwo da miyar zogale, kina ganin na taho ba za ki iya taran napep su kawo ki gida ba, za ki gani a kwanon ki ai.''

Sannan ta kuma harar su Reedah tare da faƈin ''ku gafara min na wuce abeg.''

Unaisha ce ta gyara zaman glasses ɗinta sannan ta ce ''Calm down kina da baƙi a waje, You better respect your self Hajiyata.''

Furzar da iska Liya ta yi sannan cikin sassanyar muryarta ta ce ''ya ce na yi wa Mamin abokinsa girki buh I don't know how to do it.'' ta ƙarashe maganar kamar za ta yi hawaye.

Murmusawa Ily ta yi tare da faɗin ''Time.''

''What do you mean?." Liya ta faɗa haɗe da ɗage girarta guda ɗaya.

''Nothing much, kije ki ta ya matar hira i will handle it.''

''Salimar fa?."

''Itama yau ta huta.''

''Ki tabbatar kin yi mai daɗi please.''

''Allah sai na bar ki da kayan ki.''

''Sorry little sis.''

Daga haka suka bar Ily suka fito daga cikin kitchen ɗin.

Ko da ta fito ma matar har ta fara harraman tafiyya, cikin muryarta mai sanyi ta ce ''Ummi ba dai tafiya ba na ɗaura miki girki.''

''Noo daughter na gode da karramawa, ai abin sha ɗin ma kaɗai ya yi, and besides am in a hurry Abbanku ya dawo, kar ya ga na daɗe.''

''Toh Ummi yaushe za ki zo ki kwanar min?."

Murmushi Ummin ta yi tare da kallon zallar yarintar Liyanar, sannan kuma cikin muryarta mai nuna ƙaunar Liyanar ta ce ''Don't worry daughter ai sai dai ki zo ki kwanar min, zan sa shi ya kawo min ke okay.''

Murmushi Liyana ta yi mai kyau sannan ta ce ''Okay Maa my regards to Abba.''

''In shaa Allah dear.''

Daga haka Hydar da tun ɗazu ya sauko ya ɗauki jakarta.

Jakar dake ƙasa Ummin ta bata haɗe da faɗin ''Ga wannan ba yawa.''

''Mai yawan kenan Ummi, na gode sosai.''

Bai kallesu ba ya yi gaba haɗe da riƙe jakar na ta.

Sai da ta rako Ummi bakin mota sannan ta koma cikin gidan.

Ummu ce ta yi murmushi mai faɗi sannan ta ce ''Aliyyu.''

''Yes Maa.''

''Ka yi sa'ar mace wallahi, ka riƙe ta hannu bibbiyu, she's very socialize, I think you have won the trophy, ba ka da wani damuwa a yanzu.

Ga sanin ya kamata, ga kyau ga sura mai kyau ga hali mai kyau.''

Aliyyu ji yake kamar ya nutse a ƙasa dan kunya, dan sura mai kyau ɗin nan ji yayi kamar ya koma gida.

Daman kuwa bai yi nisa da Gidansa ba ya yi parking motar tare da faɗin ''Ummi Amir ya ja ki i forgot something at home, gobe sai na zo wurin Abban.''

''Is Okay Son je ka wurin matar ka duk da naga ta yi baƙin dare.''

Amir kam banda dariya babu abin da yake.

Bai kula sa ba ya fice a motar tare da sosa ƙeyarsa, Amir ya dawo wajen mazaunin driver, sai da ya yi wa Amir kallon warning sannan ya wuce ya kama hanyar gidansa.

Bayan Liyana ta dawo ma sa wa tayi Ily ta kashe gas sannan suka fara hira har da Salimah.

Ƙamshin turarensa ne ya fara sanar da ita wanda zai iso wurin, hakan ya saka ta ɗan lumshe idanunta na y'an daƙiƙu tare da sauke su akan kyakkyawar fuskar sa.

Wani kalar murmushi ne ya suɓuce mata wanda ba ta yi aune ba.

Gaisuwan da yake amsawa ne ya dawo da ita daga duniyar da ta lula.

Kallon wadda ya sanya aiki zaune ta na hira da ya'n uwanta yayi.

Wani kallo ya watsa mata haɗe da faɗin ''Ina abin da na sanya ki?.''

Turo lips ɗinta ta yi tare da kai dubanta wurin da yake tsaye tare da faɗin ''Ai Ummin ta tafi.''

Sai da ya kalli fuskan ya'n falon sannan ya ce ''Biyo ni."

''Ina ɗin zan biyo ka?."

Bai kulata ba ya cigaba da tafiyarsa.

Kallon su Reedah ta yi tare da faɗin ''Wai ƙarfe nawa za ku tafi ne?."

''Anan za mu kwana.'' Rashidat ta faɗa ta na kallon fuskan ya'n uwanta.

''Cabɓ, tun da kuka zo ya ƙafe ku da idanuwa, wallahi ku taso ku kama hanyar zuwa gidan Abbhi, haka kawai, akwai fa aure tsakanin ku.''

''Kaji Liyana da wani zance, Allah na tuba, gaskiya wannan maganar ta ki ta ɓata min rai ainun.''

Unaisah ta faɗi hakan tare da cire glasses ɗinta.

''Ai wallahi sai mun kwana, Ilham kunna mana TV abeg.'' Faridat ta faɗa haɗe da shingiɗewa akan kujerar parlourn.

Tsaki ta ja tare da barin wurin.

Tsaye yake a wajen corridor ɗin ɗakinsa tsawon minti biyar ya na ta jiranta, cikin muryarta da yake jinsa har brain ɗinsa ta ce ''Gani.''

''Saboda iskanci kin wani shanya mutum kamar mai jiran zuwan sarki, ko kin fara hauka ne.''

''Ni ka daina kira na mahaukaciya tun da ba a bola ka tsince ni ba.''

''Are you talking to me.''

''Allah ni ba da kai nake ba.'' ta faɗa tare da niyyar arcewa aguje.

Fizgota ya yi tare da haɗe ta da jikin bango, hannunsa ɗaya ya dafa a bangon da'yan kuma ya na mai riƙe haɓarta da shi.

Mutsu - mutsu ta shiga yi da bakinta da har lokacin lipstick ɗin bai goge ba.

Tsirawa bakin ido ya yi tare da matsowa da fuskarsa gab da nata lumshe idanunta ta yi sosai ta na Allah Allah ya sa sumbatar ta zai yi.

Hydar da mutsu - mutsun da take da bakinta ke ƙara birgesa hakan ya sa ya ƙara matso da face na sa.

Hannunsa na tsakiya da kuma na ƙarshe ya haɗe tare da balle mata lips ɗin har sau biyu.

Liyana dake tsammanin jin lips ɗinsa ne taji wani kalar azaba ba ta san time ɗin da ta buɗe ido ba ta ware su akansa haɗe da riƙe bakin nata.

Ranƙwashi ya ƙara sakar mata haɗe da faɗin ''You're expecting me to kiss you right?, toh Allah ya tsare bakina.''

Liyana saboda zugin da bakinta ke yi har ta fara ƙwalla.

Tsaki ya yi tare da faɗin ''Spoiled brat.'' sannan ya shige ɗakinsa haɗe da kulle ƙofar da ƙarfin tsiya.

Fashewa ta yi da kuka haɗe da durƙushewa a wurin.

Su Ily kam da suka gaji da zama tashi suka yi suka fita a gidan tare da tafiya gidan Ammi.

Daga ƙarshe dai Liyana sai da ta kusa hour ɗaya a wajen ta na gunjin kuka, sai da ta ji alamun kamar zai buɗe ƙofa sannan ta shige corridor ɗin ɗakinta tare da shigewa ɗakin gaba ɗaya.

Can ɓangaren Hydar hakan nan yake jin wani kalar mix feelings a tattare da yarinyar. He dislikes her habits, not her, amama wani ɓangare na zuciyarsa gaba ɗaya yake ƙinta.

Safa da marwa ya shiga yi tsakanin falo da master room ɗinsa, shi haka kurum yake son ya yi punishing ɗinta.

Ace matar da ya aura babu kalar club da gidan nanaye da ba ta sani ba.

He always wants kamilalliyyar mace for his self, the one with Deen, ƙarshen zance kuma wacca idan ba Hijab ta saka ba she will feel that the whole world ita suke kallo.

Saɓanin wannan da su Mami suka zaɓa masa, wadda ko da lingerie za ta iya zuwa duk wata duniya da ta ga dama ba tare da ta ji ko ɗar ba, ba ya jin ta iya karatun Alkur'ani mai girma, kullum cikin waƙa take kamar jiƙar Bob Marley.

Idan ya ce an cuce sa a wannan haɗin bai yi ƙarya ba.

Dubi mahaifiyyarta mutuniyyar arziƙi he can remember ranar da ta basu 5, 5k shi da Amir.

Very cheerful giver, uwa uba hankali, shi ma Dad ɗinta is something similar with the girl.

Wani kalar tsaki ya ja tare da shigewa toilet ya ɗauro alwala tare da gabatar da shafa'i da wuturi haɗe da kwanciyarsa amma still baccin is no where to be found tunanin Liyana ya masa kane - kane a rai.

Ɓangaren Liyana kam tun da ta shiga ɗaki recalling ɗin haɗuwarsu da shi take tun lokacin da suke 100lvl.

Da akwai ranar da suka fita da Ily da aurensu ya na jingine da jikin mota ta sheƙar da ruwa a jikinsa da gangan, and that day ma a maimakon ta ba shi haƙuri sai ma gwalo da ta masa tare da faɗa masa ta ga uban da ya tsaya masa.

Haka tai ta tariyo duk wani abubuwan da ta ɗinga masa wanda sai da suka saka ta kuka.

Duk da yanzu almost 2 Weeks da saninsa a matsayin mijinta, buh that guy is very dangerous, he can squeeze her a lokaci ɗaya a manta da babin ta ''Ya rabb have mercy upon me.''

Ta faɗa haɗe ƙanƙame jikinta, sannan a hankali ta shige toilet haɗe da yin wanka ta fito ɗaure da wani white towel.

Drying ɗin gashinta ta yi tare da zira kayanka da take Sallah da shi, bayan ta idar da sallar ma sai da ta ɗan roƙawa kanta tsari sannan ta kwanta bacci dan gobe za ta fita school.

Su Ilham kuwa tun da suka baro gidan Liya kowa ransa yake a ɓace, barimma Unaisah da Rashanda.

Ammi dai tun ta na tambayar na su har ta daina, Rufaidhat kuwa daman ko gidan rasuwa ba ta je ba , a cewar ta da iyayenta suka mutu Ikimat ɗin ba ta zo ma ta ba.

Ɓangaren gidan rasuwa kam bayan fitar Liyanar da Hydar Abbhi sai da ya tayar da maganar, haɗe da ƙoƙarin kiran police, amma da Jiddah ya tsawatar masa sai ya bawa police ɗin haƙuri haɗe da faɗa musu is a family issue.

Mama Fatuh da Yusrah kan sun gama ƙullace - ƙullacensu sannan suka koma can gida Niger, Maraɗi inda acan Mama Fatuhn ke da aure.

A taƙaice dai gidan ya watse daga Mama Maimu sai Mama Lantana mahaifiyarsu Mama Fatuh.

Sai dai mu ce Allah ya jiƙan Ummaru da gafara.

Washegari da sassafe kafin ta tashi har Salimah ta tanadar mata emergency ɗinta dan wani kalar ciwo da jikinta ke yi saboda aikin da ta sha jiya.

Zaune take akan dinning table ta na cin milky donut ɗinta da strawberry hollandia ɗinta hankali kwance ta na ci ta na lumshe idanunta haɗe da chatting da Lily.

Ƙamshin turarensa ne ya fara ziyartarta haɗe da dagule lissafinta ta dabarbarce lokaci ɗaya.

Cikin shigarsa na gym ya shigo hannunsa ɗauke da bottle water da kuma hanky.

Kallonsa ya kai wajen dinning ɗin take zaune cikin wani faux fur v neck jacket black color sai wani crystal jeens palazzo trousers shima black color kanta ɗaure da wannan ɗan kwalin nata na martar minista.

Ƙafafunta sanye da wani classy crystal boots white color designers mai shegen kyau da tsada.

Sai kuma wani gucci bag white color akan table ɗin dinning ɗin.

Sai idanunta dake sanye da wani glasses mai form ɗin medical glasses Wanda ta saba sawa.

Tun da ya shigo kanta yake a tsugunne, jin idanunsa na yawo akanta hakan ya sanya ta fara ɗagowa a hankali tare da sauke idanun ta akan nasa for the second time.

A dabarce ta ce ''Goo.... Good.....mor.....ning.....Yaya Alih.''

''Morning.'' ya amsa a taƙaice tare da shigewa cikin kitchen ɗin dake bayan ta.

Wani sassanyar ajiyar zuciya ta sauke haɗe da shigewa kitchen ɗin itama dan ta ɗauki package ɗinta ta wuce school.....

Durrah Hydar.✍

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

THE REGRET

(Dana sani).

~PENDING AMARYA CE~

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

THE NOBLE WRITER'S TEAM

This page is dedicated to you my favorite brother.

Yaya Sa'id dinaa

Allah ya shiga lamarin ka Alhajina.

Burin kowace y'a mace.

May Allah's blessings always be with you Fav miii

Iganya miii

_ Pending Amarya 37_

Tun da ya shigo kanta yake a tsugunne, jin idanunsa na yawo akanta hakan ya sanya ta fara ɗagowa a hankali tare da sauke idanun ta akan nasa for the second time.

A dabarce ta ce ''Goo.... Good.....mor.....ning.....Yaya Alih.''

''Morning.'' ya amsa a taƙaice tare da shigewa cikin kitchen ɗin dake bayan ta.

Wani sassanyar ajiyar zuciya ta sauke haɗe da shigewa kitchen ɗin itama dan ta ɗauki package ɗinta ta wuce school.

★_____★

Ko da ta shigo kitchen ɗin ya na tsaye a gaban coffee maker ya na ƙoƙarin juye coffee ɗin a cikin mug, a hankali ta iddasa shigowa haɗe da nufar kan kitchen island ɗin ta ɗauki abin da Salimah ta mata packaging, ''Where did you think za ki je by this time.'' ya ƙarashe maganar ya na mai juya milk a cikin coffee ɗin, kallonsa ta yi da kyau sannan kuma ta juya da niyyar ficewa daga kitchen ɗin.

''One step kika ƙara sai kin gane shayi ruwa ne.''

''Toh ni dan Allah mai na maka?." Ta yi maganar kamar za ta fashe da kuka.

''Ba za ki fita daga gidannan da wannan kayan ba, find something better to wear, otherwise babu inda za kije.''

''Amma ai a haka nake fita daga cikin gidan nan for almost 4-5 months, and besides wannan shigar nake tun ina gidanmu har a gidan kakanni na.''

''Ba na magana biyu, find something else to put on, leave my presence.''

''Yaya Alih.''

''Ba ni da ƙanwa irinki.'' daga haka ya zo zai wuce ta gabanta, da sauri ta riƙe rigarsa tare da faɗin ''Pleaseee.''

''Kyale min riga na ko na zuba miki ragowan abin da ke hannuna.''

''Dan Allah ka yi haƙuri, ai kayan ma a lefe aka saka min wallahi.''

''Cika min riga ta na wuce, wai yaushe ma na fara wasa dake to this extent.''

''Allah ni ba zan cika maka rigar ba , You have to say yes, an.....''

Bai bar ta ta ƙarasa maganar ba ya watsa mata ragowan coffee ɗin ba ki ɗaya haɗe da sakar mata ranƙwashi a kai.

Ba zato ba tsammani Liyana ta ji saukar coffee mai zafin gaske a fuskarta, a gigice ta saki ihu haɗe da riƙe fuskan na ta.

''You think that ba zan iya ba right?." Ya na faɗin hakan ya ja tsaki haɗe da ficewa a kitchen ɗin.

School ɗin da bata je ba kenan.

Da ƙyar ta lalubo hanya ta wanke fuskarta a sink ɗin dake kitchen, jacket ɗinta duk ya ɓace da coffee ɗin, ji ta yi kawai kuka ta zo mata babu zato babu tsammani kawai ta haura sama da gudu.

Ɗauraye jikinta ta yi sannan ta ƙara saka wani polo shirt da kuma palazzo trousers, wani ƙaramin akwati mai kyau ta ɗauka tare da zuba kayanta aciki.

Har ta gama loda kayan ta na ta hawayenta sai kuma ta koma a hankali ta zauna haɗe da fashewa da kuka ta na faɗin ''Ba abin ka je gida ba Ammi ta ce ba haka ba, ka kama hanya kaje gidan Neneh kuma gorin duniya ta haɗa ta yi maka shi.''

Goge hawayenta ta yi tare da ɗaukan wayarta ta na mai kiran Abbhi amma bai ɗaga ba.

Cilli ta yi da wayar akan gadon bacci ɓarawo ya sace ta.

Arround ƙarfe biyun rana Salimah ta shigo kawo mata lunch, ko kallonta ba ta yi ba ta shige toilet haɗe da yin alwala.

Bayan ta gabatar da sallar ma kiran Abbhi ne ya shigo wayarta haka suka cigaba da hira har sai wajen uku sannan ta shige toilet ta yi wanka haɗe da alwala domin miƙa sallar Asr. Hakan nan ta tsinci kanta da yin shiru akan abin da Aliyu ya mata ya da safe.

Bayan ƙarfe shida na yamma ta sauko cikin shigarta na boomb short da kuma wani polo da ta ɗan ɗage shi kunnen ta sanye da ear pods ta na jin waƙar _Ayra Starr_, kan ta ba ɗan kwali amma gashinta a tufke yake, sai wani lipstick mai kyau dake ƙyalli a leɓenta.

Zaune yake akan kujerar parlourn ya na kallon tashar Spotlight ya na kallon wani wasan Madrid, sai tapping ya ke da hannu ya na faɗin ''Mbappe pass the ball.''duk da she's a fan of Madrid amma Allah, Allah take ɣan Liverpool su cinye wannan ball ɗin.

Wani kalar dribbling M Salah ya kai wa Belingum da Mbappe ya yi wa passing ball ɗin wan da atake ƙwalon ya shige cikin ragar Madrid.

Wani kalar tsaki Hydar ya ja ya na faɗin ''Ohh God, damn it, ci biyar at thesame time.'' dariyar da yake ji ana yi ne ƙasa- ƙasa ya sa shi juyawa ya na kallon side ɗin da yake jin dariyar na futowa, dan shi har ga Allah bai ga shigowarta ba.

Haɗa idon da suka yi da shi ne ya sanya ta ƙwarewa ta fara tari sosai, nufuto ya fara yi hakan ya sa ta fara janye jikinta ta na matsawa baya.

Daman tun da can a jogane yake zaune a falon tun cin farko da aka musu, Amir ya kira shi yake ta masa dariya.

A zafafe ya ƙaraso wurin tare da faɗin ''You're laughing saboda an ci mu wasa right?."

''Noo wallahi am coughing ba dariya nake ba.''

''Za ki gane kurenki ne yanzu.''

''Dan Allah kayi haƙuri wallahi, fuskata kaɗan ya rage fatar wajen bai ɗaye ba dan zafi, please Yaya Alih.''

''Stop calling me with that stupid name da kike ƙoƙarin kakaɓa min.''

Sosai Liyana ta tsorata da lamarin Hydar.

Wani kalar ɓaci ransa ke ƙara yi, yadda take ba shi haƙuri at the same time take wani kalar murmushi, abin da ya tsani Sultana ta yi.

Zuciya ce ta ɗibe shi hakan nan kawai ya zare belt ɗin jikinsa ya shiga lafta ma ta kamar an aiko shi.

Dukanta kawai yake babu ji babu gani, Salimah da ta ji ihunta ta fito bawa Hydaar ɗin haƙuri, guda ɗaya da Ya shauɗa mata a baya ba ta san time ɗin da ta shige ɗakinta ba haɗe da saka key.

Ga shi jikinta daman babu kayan arziƙi duk cinyarta sai da ya yi masa dukan lilis.

''Frog jump.'' ya faɗa a zafafe haɗe da cillar da belt ɗin hannunsa tare da shafa gemunsa.

''Ba ki ji abin da na faɗa bane!." Ya faɗa a tsawace.

Ta na layi ta tashi haɗe da faɗin '' Ni ban san yadda ake frog jump ba.'' ta ƙarashe maganar tare da fashewa da kuka.

''Kin ga already Sallah ake kira, kafin na dawo daga masjid ki tabbatar kin fara frog jump ɗinnan, if not za ki ga the worst side of me.''

Ya ƙarashe maganar tare da yin ƙwafa ya wuce masallaci da kayan jikin nasa.

Liyana cinyoyinta kawai take bi da kallo haɗe da yin da na sanin fitowar da ta yi, indai wannan ne aure wallahi da ba ta yi ba, sanin miji ko iftila'i'.

Fashewa ta ƙarayi da kuka mai tsuma zuciya.

Ƙarar buɗe ƙofar falon da ta ji ne ya sanyata tashi da sauri ta na sharɓar majina haɗe da yin frog jump ɗin.

Shigowa ya ƙarasa yi cikin takunsa na ƙasaita haɗe da faɗin ''Make sure kin zagaye falon nan sau uku.''

A tunaninta ko wucewa sama zai yi sai ta ga ya ma jawo ragowan fresh milk ɗinsa ya na sha.

Sai da ta zagaye falon sau biyu sannan ta ji ƙarar buɗe ƙofar ɗakin Salimah.

''Salimah ina za kije?." ''Yaya Hydar girki zan yi na ga dare ya fara yi.''

''Je ki huta yau ita za ta yi girkin, You over there."

Juyowa ta yi ta ƙafe shi da manyan idanunta.

''Ma za ki tashi ki shiga kitchen ki dafa min abatcha, Salimah akwai fresh cassava da na kawo yau a ina kika ajiye?."

''Store ɗin ajiye potatoes yaya.''

''Mai kuma abatcha ɗin?." Ta faɗa ta na gwale idanunta.

Bai ma bi ta kanta ba ya wuce ya fara tafiya towards kitchen ɗin.

A hankali ta tashi dan ba ta son jikinta ya ƙara tsami hakan nan ta na ji ta na gani.

A hankali ta shiga ɗingisawa tare da bin shi a baya har suka ƙaraso cikin kitchen ɗin.

Bai zame ko ina ba sai store ɗin potatoes da doya, wasu manyan cassava's ya ɗebo guda uku tare da ajiye mata su akan kitchen island.

''Start.''

''Wallahi ban san mai ne abatcha ba, please karka dake ni.'' ta faɗa haɗe da fashewa da kuka haɗe da matsar da kanta gefe ta na mai gaucewa marin da yake shirin kai mata.

''Shut up.'' shiru ta yi tare da faɗin ''Toh ya zan yi?."

''Bare rogon tukunna.''

A hankali ta shiga ɓarewa slight mistake idan ta yi kuwa sai ya ranƙwasheta ko ya ɓalle ta da harara.

Wani bowl ne ya zame a hannunta, still ba ta damu ba ta cigaba da gurza cassava's ɗin.

Ranƙwashi ya sakar mata hakan ya sa ta ce '' zan kwashe idan na gama.''

''Who care's idan yaso ki fasa gaba ɗaya kayan kitchen ɗin in dai tiles ɗin ba zai samu karcewa ba am okay, c'mon do something fast.''

''Yi nake faaa.'' ta faɗa hawaye na zubar ma ta, ta sa hannu ta goge.

Haka ya yi ta monitoring ɗinta a kitchen ɗin har abatcha ɗin ya zama done, wani ɗan wood plate ta ɗauko ta zuba masa abatcha ɗin.

Bayan ya ga ta juye acikin plate kamar yadda ya umarce ta, wucewa ya yi ya zauna akan kujerar dinning dake cikin kitchen.

A hankali ta shiga jan ƙafar har ta tako zuwa wajen da yake, ajiye plate ɗin ta yi a hankali sannan ta fara ƙoƙarin barin wajen.

''Ina za kije?."

''Hutawa nake son yi kafin nayi sallah.''

''A ina za ki huta ɗin?, not when I'm arround.'' ya yi maganar haɗe da kai spoon ɗin abincin bakinsa, da sauri ya furzar haɗe da faɗin ''haka nace kiyi?, ko kin haukace ne da za ki zabga uban gishiri acikin abinci haka?."

''I use the measurement da ka ba ni." Ta faɗa haɗe da ƙoƙarin buɗe baki za tayi kuka.

''Ko da wasa naji kin ɓare wannan bakin naki mai kama da na ɓeraye sai kin gane kurenki da daddaren nan.'' da sauri ta kame bakinta haɗe da gyaɗa kanta ta na ƙara waro idanunta akansa.

''Salimah!, Salimah." Ya na mai ƙwala ma Salimah kira, Salimah dake rakuɓe afalo tun ɗazu ta shigo haɗe da kallon Aliyun.

''Bayan waɗannan kayan kitchen ɗin da akwai wasu ne ko su kenan?."

Salimah ba tayi tunanin komai ba ta ce ''Eh yaya akwai wasu a storage.''

''kina wanke waɗan nan da waɗancan ne ko kuma ba kya wanke su?."

''way'anda ake amfani da su kullum, kullum ake wanke su, su kuma na cikin cabinet sai every month ending ake wanke wa, su kuma na store ɗin are still new.''

''Okay nagane shiga ki kwaso min.'' har Salimah ta yi hanyar store ɗin da aka ajiye sauran kitchen utensils ɗin sannan Hydar ya ƙara faɗin ''Noo Salimah just leave it you can go, ba sai kin kwaso ba.''

''Okay Sir.'' daga haka ta fice daga kitchen ɗin ta na tausayawa Aunty Liyana. (Liyana nima kin bani tausayi a swear 😂).

Kallonsa kawai take babu ko ƙyaftawa, she can't believe this guy na juya ta fiye da yadda ya juya stearyn mota a rayuwarta.

Muryarsa ce ta katse ta daga tunanin da ta tafi, ''Kina jira ne na kwaso miki kwanukan?."

''Mai zanyi da su toh?."

''A kaina za ki juye, je ki kwaso kwanukan ki wanke su yanzu ba sai gobe ba, sannan ba na son maimaita kaina, am I clear?."

''Yess.'' ta faɗa a raunane.

''Good.'' da ga haka ya fice daga kitchen ɗin domin ɗauko wayarsa da car key ɗinsa ya siyo fruits ya dawo.

''Mugu kawai azzalumi, kuma Allah sai ya saka min, darajar ka ɗaya wallahi ina sonka da gidan sai ya mana kaɗan wajen yaƙi.'' ta faɗa ta na sharɓe majinarta.

Muryarta har ta fara dashewa, ta kusa mintuna goma ta na kwaso kayan amma still ba su ƙare ba.

A lokacin har kusan ƙarfe goma na dare ta gota, wanke kwanukan ta fara yi amma tsantsi yake mata dan kusan plate uku sun fashe daga farawarta.

Ganin ya yi kusan minti biyar da fita da motarsa ya sanya ta kwaso wasu daga cikin kwalayen warmers ɗin ta fara ƙoƙarin haurawa dasu saman ɗakinta.

Ta na yi ta na waigen entrance ɗin falon a haka har ta kai kusan kwalaye shida dukkanninsu da warmers aciki.

Ana bakwan ne taji shigowar motarsa cikin compound ɗin da gudu ta dawo domin komawa kitchen ɗin sai dai kashh ta na zuwa dai- dai tsakiyar falo, ya buɗe ƙofar ɗakin haɗe da ƙafeta da idanunsa masu rikitarwa.....

Durrah Hydar.✍

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

Not edited □□

THE REGRET

(Dana sani).

~PENDING AMARYA CE~

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION□ ✍

(J.W.A)

THE NOBLE WRITER'S TEAM□

Pending Amarya 38

Ana bakwan ne taji shigowar motarsa cikin compound ɗin da gudu ta dawo domin komawa kitchen ɗin sai dai kashh ta na zuwa dai- dai tsakiyar falo, ya buɗe ƙofar ɗakin haɗe da ƙafeta da idanunsa masu rikitarwa.....

''What are you trying to do?." Ya tambaye ta da muryarsa mai amo.

Cikin inda-inda ta fara magana ''Ai..... Ai..... Daman ba su kaɗai bane kayan kitchen ɗin nawa ba akwai wasu a ɗakina.''

''Su kenan?." Ya ƙara jefo mata wani tambayar, ''Yee....yeeaah, i think gaba ɗaya na kwaso.'' ta ƙarasa maganar ta na sosa goshinta, da gumi ya ɗan ƃata, alamun dai rashin gaskiya.

''Kin gama wanke wanken?." Ya yi tambaye ta haɗe da matsowa sosai wajen da take, komawa baya ya yi kaɗan haɗe da kallon cikin idonsa ta ce ''A'a.''

Ƙarar saƙo ne ya shigo cikin wayarta dake yashe a ƙasar Turkish carpet ɗin falo, hakan yasa idanunsa sauka kan saƙon dake ɗauke da Instagram icon, da ya fito cikin jerin notifications.

A hankali ya tako zuwa wurin da wayar take haɗe da ɗaukar wayar, wani kalar runtse idanunta ta yi haɗe da juyar da kanta gefe ta kalli ɗayan gefen, Allah Allah kawai take Allah ya sa ba Nifraz bane ba ya tura ma ta saƙon.

''Mufti menk has shared a reel.'' shi ne abin da ya gani rubuce akan fuskar wayar, cikin muryarsa mai daɗi ya ce ''Unlock the phone.'' ya yi maganar ya na mai ƙafeta da idanunsa.

''Buh that's my private life, mai za ka yi da wayata?." Ta faɗi maganar kamar za ta fashe da kuka.

''Don't let me repeat myself, I said unlock this phone!." Ya yi maganar a ɗan tsawace.

Amsar wayar ta yi haɗe da buɗe masa wayar, daman kuma ba ta fita daga chat ɗinta da lily ba a IG ɗin, soo kawai scrolling ya yi tayi ya na komawa can bayan chats ɗin, yadda ka san ta fizge wayar daga hannunsa haka take ji, dan ko Ammi idan ta amshi wayarta ta na dubawa zuwa take ta haɗa ta da Abbhi ya ƙwato mata ballantana wannan hallittan.

Cikin wata kaliyar shaƙaƙkiyyar murya ya ce ''Get lost.'' ''To where?, ina zanje babu wayata, ko kai ka siya min, wadda aka samin ma alefe ba gane kanta nake ba, idan ma ka ɗauka ita ce just gimme my pho....'' ba ta ƙarashe maganar ba ya bata mari lafiyayye a fuska haɗe da nuna mata hanyar kitchen.

Jiki a sanyaye ta bar wajen hawaye na zuba a fuskarta, bayan ta ƙarasa kitchen ɗin ma kuka kawai take haɗe da faɗin ''Ni anya wannan hanyar da Lily ta ce in bi ba barinsa zan yi ba, haka kawai a maida martani ayi ta saka jikina tsami, da yarinta na, za'a maida ni tsohuwa, ni dai Neneh sai da Allah ya ishe min.'' ta ƙarashe maganar ta na goge hawayenta.

Sai wajen ƙarfe 12 na dare Liya ta kwanta bacci ba tare da ta hau online ba.

******

Ɓangaren Yaya Alih kuwa, tun bayan da ya saka ta wuce kitchen yake ta faman karanta chat ɗinta da lily, abin na basa nishaɗi, the Lady we call Lily is soo simple buh her fake life pass her power, sometimes su kan faɗi kalan guy ɗin da suke so with some naughty talks, he can even say those girls are yan iska girls.

Wani voice ɗin Lily ya kunna wan da take bawa Liyana shawarar, ta ɗan ɗinga saka sexy wears, da kuma yawan yawo arround in da yake, duk abin da zai mata ta maida shi wasa, he will fall for her, idan kuma wannan hanyar bai ɓille ba sai abi ta wata hanyar.

He just smiled dan ganin wawtan yɤan matan biyu da ya gani, wai shi za'a yi seducing, yarinyar da ko shape ɗin arziki ba ta da shi, jikinta kamar na ƙwailayen shekara 14 , ita take cewa zata yi seducing ɗinsa, that girl most be in a mental health sannan ta gudo.

Tsaki yaja haɗe da faɗin ''Filthy thing.''

Kallon agogon ya yi ya na mai ganin ƙarfe 1na dare har ya wuce, hakan ya sanya sa wucewa toilet ya yi wanka haɗe da yin alwala tare da saka kayan baccinsa, sai da ya yi sallah sannan ya saka sleep mask ɗinsa ba tare da ya bi ta kan wayar ba kuma.

Arround ƙarfe 4 na asuba ya ji wayarsa ya na ringing ta shi ya yi daga barcin haɗe da ɗaga wayar dake kan bedsides ya na mai karawa a kunnensa.

Muryar Abbhi ya ji mahaifin Liyana ''Assalamu alaikum Son.''

''Wassalamu alaykum Abbhi.''

''Son sorry na tashe ku a bacci, ina daughter na take?."

''Tana nan lafiya Abbhi.''

''Okay shikenan, dama tun jiya nake ta ma ta magana a online she didn't reply, kuma i called her, almost 20 missed call she didn't respond, ko bacci na kasa yi shi ne na sanya Ilham ta bani number ka.''

Sai da ya ɗan ja tsaki ƙasa - ƙasa, sannan ya ce ''Wallahi Abbhi ta na lafiya kawai dai da yamman nan ne ba ta ji daɗin jikinta ba, shi yasa, dan har hospital muka je sai arround 10 muka dawo na dare, ta ce na gaya maka ma na ce kar a gaya dan kar a ɗaga muku hankali.''

''Ma shaa Allah, amma jikin da sauƙi ko?." ''Eh Abbhi yanzu ma bacci take da na tashe ta.''

''Just leave her ka ji, Allah ya yi albarka.''

''Amin a kwana lafiya.''

Ilham, Ammi har da Rufaidhat duk suna falon dan babu wadda ya sanya ta rintsa a cikinsu, dan different types of taught ke zuwa cikin kansa, ko ta yi hatsari ta na hospital, ko ta mutu a ɗaki ba'a sani ba.

''mtsww akan wannan ka sa muka kasa runtsa idanu, toh wallahi, Allah ya ishe min baccin da aka ƙi sani yi kuma, ƙilan ta ma club taje tayi tatil sannan ta yi dare, shi ma mijinta dake ɗan nanaye ne, ya rufa mata asiri.''

''Rufaidhat watch your tongues when it comes to my daughter, kowa yaje ya kwanta.''

Daga haka ya haura saman side ɗinsa.

Ita ma Rufy ta tashi haɗe da hararar Ammi tare da faɗin ''Babu arabi ba boko, kin ga kinje kin haifi fitina a maimakon Fatimah.''

''Ai abin sa'a ne taɓa nonon sirika, ke kici sa'a ma ki haifi ya' har ta zama fitinar.'' Ily ta faɗi hakan ta wuce nasu ɗakin dan ita ma ta san maganar akwai nauyi.

_____*

Ɓangaren Liya kam ji take kamar za ta mutu saboda ciwon jiki ga wani sara ma ta da kanta ke yi kamar zai cire, sallar asubar ma a daddafe ta yi shi da misalin shida na safe, sosai ta ke jin rashin samun kuzari a jikinta, barimma Kwankwason ta da take ji kamar an cire ma ta spinal cord ɗinta, da ƙyar ta samu ta yi wanka da ruwan zafi sannan ta shirya cikin wani plane abaya mara kwalliya, ko gashinta ba ta busar ba ta koma kan gadon haɗe da jan bargo domin wani kalan bacci ke fuzgarta.

Ko mintuna biyu ba ta yi ba da daddaɗen baccin da ya ɗauketa ba ta ji ana ƙwanƙwasa ma ta ƙofar ɗakinta, wani ɗan guntun tsaki ta ja haɗe da faɗin ''Waye!." Ta ɗan faɗa a tsawace, wanda ke bugun ya cigaba da ƙwanƙwasawa countinuesly ba tare da ya gaji ba, "wai Salimah wannan wani kalar karuwanci ne haka da safiyar Allah kina tashin mutum daga bacci , da wani ɗan iskan bugu."

Wani knocking aka ƙara mai shegen ƙarfin da ya fi na baya, hakan ya sata tasowa afusace haɗe da murɗa handle ɗin ƙofar da ƙarfin tsiya, saboda masifar da take cinta har rufe idanuwa take, " wai ke Salimah, wannan wani kalar iskanci ne mara license da za kina min a cikin gida dan kut....."

Ba ta ƙarasa ba idanunta suka sauka kan Hydar dake tsaye da kayan gym, hannunsa riƙe da wayarta ya na ta scrolling, " countinue what you doing, ki ƙarashe zagin." Ya yi maganar ya na ɗago manyan idanunsa haɗe da sauke ma ta su akai, sosa wuyanta haɗe da sauke idanunta aƙasa dan har ƙwalla ta fara zubar ma ta a idanunta tun kafin ya fara mazgarta.

" Welcome." Ta yi maganar a sanyaye haɗe da fara wasa da fingers ɗinta, " Your Dad wants to talk to you." Ya yi maganar tare da miƙa mata wayar.

" Allah sarki Abbhina." Ta yi maganar wani ɗan guntun ƙwalla ya ƙarasa sauko ma ta, tare da fara ƙoƙarin juyawa ta shige cikin ɗakin nata.

" Ina zaki je ?."

" Ɗakina zan shiga na yi wayar."

" Tsaya anan ki yi ki miƙo min."

Kamar ta zunduma ihu haka take ji, a nan ta tsaya sannan ta yi dailing number Abbhinata, line busy Abbhin ya danna ma ta sannan cikin second biyar aka biyo kiran.

" Hello dear."

Abbin ya faɗa a sanyaye, fashewa ta yi da kuka haɗe da faɗin " Abbhina I missed you, da kowa ma gaba ɗaya, please ka ce masa ya kawo ni yau naga fuskokin ku abeg."

Ta yi maganar ta na jan majina a kiɗime Abbhin ya ce ''Is anything wrong over there?."

Satar kallon Hydar ɗin ta yi sannan ta kalli wayar dake handsfree duk conversation ɗinsu ya na jinsu, a hankali ta ce ''Nooe just wanna say hi to you guys, ina ɗan zazzaɓin dare yɾan kwanan nan.''

''Okay well, amma kwana za ki yi, muje shan ice cream, idan ƙasar za mu bari ma duk you're okay, ni dai farin cikin ki shi ne nawa daughter, you're the only one for me, soo kar ki yi zazzaɓin da zai sa Abbhi ya ji kamar ya rasa ki okay?."

Ajiyar zuciya ta sauke sannan ta ce ''Toh Abbhina, sai na zo.''

''Okay bye dear, kar ido na ya bushe fa in ta sa rai.''

''Kar ka ji komai my rock.''

Daga haka suka yi dariya gaba ɗaya, sannan ta katse wayar, dan har ga Allah ta ɗan ji sanyi a ranta.

Wani kalar harara ya watsa ma ta sannan ya amshi wayar da ta miƙo ma sa ''Ke ko kunya ba ki ji ba mahaifinki ya kira ki ba ki gaida shi ba kin fara koro bayani, ke ba ki yarda ba ubanki ne ƙawarki ko?."

''Amma wannan ai zagi ne.''

'' Shut up while I'm talking joor, kafin na buge miki bakin nan na ki mai kama da na jaɓa.'' daga haka ya zura wayarta a aljihunsa tare da ƙara faɗin ''I need custard, with fried plantain for my breakfast, now!." Daga haka ya barta a wajen baki sake.

Juyawa ta yi ta kalli wall clock ɗin ɗakin ta ga 6:06 na safe, by this time ai bacci take mai daɗin gaske a lokacin da take gidan Neneh, dan ko gidan Ammi ma ba kullum take barinta ta yi bacci ba.

''Which kind wahala be this one nah, ni yaushe na iya ma wani dama custard da za'a ce na dama.''

Ta yi maganar ta na goge gumin da ya keto ma ta, ganin ba ta da mai amsa mata ne ya sanyata nufar kitchen ɗin da har Salimah ta gyara shi dan jiya babu wani gyara shi da ta yi.

Store ɗin ta shige haɗe da ɗauko plantain ɗin ta fara ɓarewa a cikin bowl haɗe da yanka shi kalar yankan da ake masa, ruwan zafi ta ɗaura akan gas sai da ya ta fasa ta ɗauko garin custard ba tare da kwaɓa shi ya zama kamar gasara ba ta dama shi cikin ceramic bowl ɗin da suke haɗa fruits salad, wani kalar gudaji ya yi duk babu kyaun gani, kafin ta juyo daga dama custard ɗimma har plantain ɗin ya fara ƙonewa, da sauri ta kwashe haɗe da zuba su acikin plate, ganin custard ɗin ya yi wani iri ya sanyata zubar da shi haɗe da wanke bowl ɗin, gashi wayarta na hannunsa balle ta kira Ily, jin muryarsa kamar ya na waya ya sanyata saurin zuba custard ɗin haɗe da zuba masa ruwan sanyi sannan ta yi sauri ta dama duk da ya yi ruwa bai yi wani kaurin na muzo mu gani ba.

Wani jar ta gani jere guda biyu a waje ɗaya hannunta kawai ta kai ga na farko ba tare da ta wani duba menene a ciki ba ta juye haɗe da stiring ɗinsa ba tare da kuma ta damu da taji taste ɗinsa ba.

_____

Zaune yake akan kujerar dinning ya na kallon laptop ɗinsa yadda ya saba duba factory ɗinsa na China, hannunsa na dama kuwa na manne da kunnansa ya na magana a waya, yadda yake amsa wayar ne ya bata tabbacin cewa Amir ne ke ma sa magana kuma kusan ma akanta ne idan za ta iya zama judgmental, wani kalar murmushi ya saki tare da faɗin ''Amir ba na son ƙorafi, I've made it clearly to you

babu inda zanje da wannan yarinyar, yadda ba ta jin magana, ta zo ta yi abin da zai sa a koro ni daga can, Amir ka riƙe advice naka please.''

Daga haka ya kashe wayar, haɗe da kulle laptop ɗin, A hankali ta tako har inda yake tare da ajiye tray ɗin akan dinning ɗin, wani banzan kallo ya wurga ma ta dan yanzu wani kalar tsanarta ya ji ya na masa yawo a kogon zuciya.

Bayan ta ajiye breakfast ɗin a hankali ya ɗauki tea spoon haɗe da shan custard ɗin, a million ya furzar haɗe ƙafeta da wani shegen kallo ''Dan ubanki uban mai ya kawo gishiri cikin wannan custard ɗin!." Ya faɗa a tsawace shiru ta yi ƙwalla na zuba a idanunta a zafafe ya ƙara faɗin ''Ba magana nake miki ba."

Muryarta na shaking ta ce ''Dan Allah ka yi haƙuri wallahi ban iya ba Salimah ce ke yin komai ba ni ba.'' ta ƙarashe maganar idanunta na zubdar da hawaye.

''Salimah!.'' Salimah ce ta fito jikinta na ɓari dan tun tuni ta na jikin ƙofa saboda wani kalar tausayin Liya da take ji, so take ta faki idonsa ta shiga kitchen ɗin amma ta kasa saboda ya na zaune a falon.(TOH Salimah mun ji uzurinki koma gefe 😮).

Kallon Salimah ya yi sannan ya cillo ma ta dubu goman da yake aljihunsa tare da faɗin ''Ki koma gidan Neneh za ta cigaba da aikace-aikacen gidan nan, ko kuma shirya kayan ki kawai zan sauke ki.''

''Toh yaya.'' Salimah ta faɗa haɗe da wucewa cikin ɗakin domin kwashe kayanta.

Wayarsa ya ɗauko tare da kiran mutane kusan huɗu, cikin ƙanƙanin lokaci wani dattijo da samari uku suka ƙaraso cikin falon, ''Alhaji barka da safiya.'' suka haɗa baki wurin faɗa.

Kallon ko wannensu ya yi sannan ya ce ''Barka dai Baba, daman ina son na sallame ku ne na yan watanni amma akowani wata za'a saka muku kuɗin aikin ku, za ku iya tafiya.''

''Toh mun gode Alhaji Allah ya ƙara buɗi, ɗan shuwa jikan shuwa.''

Bayan sun fita juyowa ya yi ya ga har a lokacin kuka take ''From today babu baccin banza a cikin gidan nan, girki, buɗe gate, bawa flowers ruwa, wanki, guga, komai ke za ki yi, tun da aure kika zo yi ba hutu ba, am I clear?."

Bai jira amsar ta ba ya yi ma ta pointing kan kujerar dinning ɗin a sanyaye ta zaune sannan ya turo ma ta tray ɗin abincin tare da faɗin ''Cinye abincin nan, tun da ba akuya aka kawo miki ba da za ki kawo min kalar wannan abincin.''

A hankali take cin abincin ba tare da ta ɗago ta kalli fuskar shi ba, cokalin custard ɗin da take sha ne ya faɗi aƙasan tiles wanda hakan ya sa ya ba ta wani kalar dirty slap, wanda sai da jinta ya ɗauke na wucen gadi.

A daddafe ta gama cin abincin da ya tilasta ma ta, sannan ta shige banɗaki ta yi wanka haɗe da shiryawa cikin wani abaya, shiru shiru ta ji har kusan ƙarfe shida na yamma ba taji ya ce ta fito ta tafi gidan Ammin ba , sannan kuma bai ba ta wayarta ba.

_____*

Tsaye ta ke a jikin ƙarfen balcony ɗin dake compound jikinta sanye yake da abaya ɗin jikinta tun na ɗazu, tun ƙarfe sha biyu ya fita daga gidan domin kai Salimah gidan Neneh, har yanzu bai dawo ba, horn ɗin da taji ne ya sanya ta firgita, dan wani kalar tsoronsa da tsoron gidan ne suka ɗirar ma ta arai, ita kaɗai ƙwal kamar mayya.

Da ɗan sauri taje ta buɗe ƙofar ta kusa mintuna uku ta na buɗe shi saboda nauyinsa da yawa yake, da mugun gudu ya shigo cikin gidan, goge gumin da ya zubo ma ta tayi haɗe da kulle gate ɗin da ƙyar sannan ta fuskanci ƙofar shiga falon dan shi ya jima da shiga cikin gidan.

Tsaye ta tadda shi ya na haska falon da wayar hannunsa ''Ni kike jira na kunna miki inverter ko ba ki san aikin ki ba?."

Ya yi maganar ya na ɗan takowa wajen da take, ''Dan girman salatin Annabi kar ka dake ni.'' ta yi maganar ta na ɗan ja da baya zuwa wajen stairs, wani kalar tsantsi ne ya kwasheta kanta ya buge da benen farko wanda hakan ya sanyata sakin wani kalar razananniyyar ƙara.....

Durrah Hydar.✍

"Tomorrow is not promised but I will keep the things that I need."

THE REGRET.

Pending Amarya ce ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION.

THE NOBLE WRITER'S TEAM

*** Pending Amarya 39***

Tsaye ta tadda shi ya na haska falon da wayar hannunsa ''Ni kike jira na kunna miki inverter ko ba ki san aikin ki ba?."

Ya yi maganar ya na ɗan takowa wajen da take, ''Dan girman salatin Annabi kar ka dake ni.'' ta yi maganar ta na ɗan ja da baya zuwa wajen stairs, wani kalar sulɓi ne ya kwasheta kanta ya buge da benen farko wanda hakan ya sanyata sakin wani kalar razananniyyar ƙara....

Takowa ya yi har wajen da take a yashe, tare da zuba hannayensa cikin aljihu, a hankali ya tsugunna a wajen tare da faɗin ''I don't care about kin faɗi ko kin ji ciwo, all I know is that sai kin canza change over, and right now not later.'' ya ƙarashe maganar haɗe da hankaɗe ta da ƙafafunsa ya na mai ball da ita.

Wani wahallalen kuka ta saki haɗe da dafe kanta tare da yunƙurawa ta tashi domin zuwa backyard ta kunna solar.

A daddafe ta kunna solar sannan ta dawo cikin falon, inda Allah ya ceceta ma kanta kumburi kaɗai ya yi ba ta ji ciwo sosai ba, direct kitchen ta nufa tare da ɗora tukunya dan har ga Allah ba ta san mai za ta dafa ba, kashe gas ɗin ta yi tunawa da conflakes da ta yi.

Komai na conflakes ɗin da za'a iya amfani da shi wurin shan shi ta zuba a resin tray, haɗe da jera shi akan dinning table ɗin.

Wanda ta jiƙa ma kasa sha ta yi dan ba ta wani jin yunwa.

Hydar kam ya na shiga ɗakinsa ruwa kawai ya watsa tare da jona phones ɗinsa a charge, sallolinsa ma acikin ɗakin ya yi su dan a lokacin har an fara kiran sallahr isha.

Wayarsa ce ta fara ringing wanda hakan ya sa shi sakin wani ɗan gajeren tsaki dan ya tabbatar ƙila Abbhi ne, dan wayar Liyanar na hannunsa har yanzu, tun ɗazu Abbhin yake kiran wayar daga ƙarshe ya kasheta gaba ɗaya.

Ko da ya ɗauko wayar nasa ma Amir ne ke kiransa hakan ya sa shi ɗaga wayar a hankali, tare da faɗin ''Assalamu alaikum, Amir what's wrong ka yi min booking ɗin?.''

''Wassalamu alaykum, Man an ɗan samu matsala babu jirgin da zai je China direct.''

''Fucked up, yanzu sai yaushe?, ɗaga meeting ɗin zan yi kenan?."

''I think soo Man, ka ɗaga meeting ɗin, wannan ACn da ka turo min ita ake son ka ƙera a companyn ka?."

Sai da Hydar ya ɗan ja numfashi sannan ya ce ''Yeah, na ma rasa wani suna zan saka mi shi.''

Dariya Amir ya yi sannan ya ce ''Toh ka saka sunan matarka ma na .'' ya yi maganar ya na gimtse dariyarsa.

A take muryarsa ta canza cikin wani kalar salon rashin mutumci kalar na Hydar ya ce ''Soo ka na son Ac ɗin ya ƙi samun karɓuwa ko ajanye offer ɗin Almost 70 billion dollars, kar ka sa raina ya ɓace da daren nan please.'' daga haka ya kashe wayarsa tare da jan duvet ya na mai kwanciyarsa.

Jin shiru bai fito bane ya sanyata shigiɗa akan kujerar parlourn tare da duƙunƙune jikinta wuri ɗaya, dan har a lokacin ba ta san asuba ta yi ba. Cikin shirinsa na masallaci ya kalleta kan kujera takure waje ɗaya ta na baccinta hankali kwance, direct kitchen ya wuce haɗe da buɗe fridge tare da ɗaukan goran ruwa mai sanyi, da sauri ya ɓalle bottle ɗin haɗe da juye ma ta shi gaba ɗaya a fuska wani kalar wahallalen ajiyar zuciya ta sauke, haɗe da tashi a zabure ta na mitsitsika ido.

Da ga haka ya fice i zuwa masallacin, ta shi ta yi haɗe da nufar stairs ta na mai nufar ɗakinta.

Sai da ta yi wanka haɗe da brush sannan ta yi sallar jikinta duk agajiye.

Hijabyn jikinta ta zare tare da saukowa ta na mai nufar kitchen ɗin, chips kawai ta soya da ƙwai sannan ta ɗaura coffee a coffee mixer, tare da ɗaukan flask ta tari ruwan zafi a dispenser.

Ƙarar shigowarsa ta ji wanda hakan ya tabbatar ma ta da ya dawo daga masjid, hakan ya sanya ta ɗan gyara kitchen ɗin dan ta san zai shigo ɗaukan coffee.

Kayan da ta jera a tray ta ɗauko tare da nufar dinning room ɗin ta na kallon cikin tray ɗin da ta ga wani ƙwaro na yawo aciki, karo ta ci da shi da yake kallon waya wanda alamu sun nuna kallon wasu abubuwan yake masu muhimmanci acikin wayar.

Abincin dake cikin tray ɗin ne gaba ɗaya suka zube ajikinsa wayarsa dake hannunsa kuma ya yi flat a ƙasa.

''Inna lillahi wa inna ilaihir rajiun, am dead, wallahi tallahi billahillaxi la ila ha illahuwar - rahmanu i didn't do it intentionally, ka ji rantsuwar Musulunci kenan.''

Ta yi maganar hawaye na zuba a idanunta. ''Thank God kin san kuɗin wayar da kika fasa right?.'' gyaɗa kanta ta yi sannan a hankali ta ce ''Is 4 million plus.''

Murmusawa ya yi tare da faɗin ''Smart girl, oya miƙo min wayata before I turn your face to blue black.'' ya yi maganar a tsawace.

Durƙusawa ta yi da niyyar ɗaukan wayar wanda hakan ya sata jin saukan wani kafirin duka a bayanta.

Runtse idanunta ta yi tare da ƙarasa ɗaukan wayar tare da miƙo ma sa idanunta na zubda hawaye.

Sai da Aliyu ya sa ta gyara gidan ga ba ɗaya tsaf sannan ta huta, still kuma he didn't gave her, her phone, duk hakan ya sata shiga wani hali.

_____

Da sassafe kamar yadda ta ɗan saba a kwanakin nan ta tashi tare da yin iya abin da za ta iya, glass cleaner da mooper da kuma towel a hannunta ta nufi kan dinning domin goge area ɗin .

She was surprised to see her phone akan dinning table and also shocked at the same time, ''Ahh wannan halittan ya manta wayar yau anan kenan, ɗan ƙwal uba.'' ta iddasa maganar haɗe da ajiye tarkacen dake hannunta ta na mai ɗaukan wayar, screen ɗin wayar a kunne yake picture ɗinta da Ammi da Ilham da kuma Abbhi ne agaban wayar,wanda da alama dai hoton last year eid ne.

Kallon wayar ta yi haɗe da faɗin ''One big family." Ƙwalla na ɗan zubo mata.

''Uban mai kike da wayar hannunki?." Wani kalar bugawa da zuciyarta ta yi sai da ta tsorata, wani tsawa da ya daka ma ta sai da wayar hannunta ta faɗi aƙasa.

''Hasbunallahu wa ni'imal wakil, my phone, innalillahi wa inna ilaihir rajiun.'' ta iddasa maganar ta na fashewa da kuka.

''Idan ba ki rufe min baki ba za ki gane shayi ruwa ne.''

Da sauri ta yi shiru haƌe da cigaba da goge dinning ɗin ta na kallon wayarta dake yashe a ƙasa.

Sai da ta gama gyara gidan duk da bai wani gyaru ba, sai arround 3 i clock sannan ta ci abinci shi ma abincin bai ma ta wani daɗi ba, noodles ne sai hollandia strawberry da ta haƌa da shi.

_____

Sosai ya canza turarensa ya mai da shi shumuk luxury scent ba Valentino da Baccarat ko Georgia armani ba, dan sosai shumukh ya take su wajen tsada, mazubin sa ma abin kallo ne.

Shi da Amir ne suka je shopping sai da suka biya ta gidansu Liyana da Neneh har gidan Mami da kullum take cigiyar Liyana.

Bayan sun fito daga gidan Mami ma sai da ya biya restaurant ya yi take away ɗin fried rice and chicken sannan ya sauke Amir shi kuma ya zaryo gidansa.

Ta na daga cikin falo a zaune ta ji an yi horn, da gudu ta tashi haƌe da saka slippers ɗinta tare da buƌe masa huge gate ɗin.

 Bayan ya yi parking motar na sa a wajen flowers ya tsaya ya na ƙare musu kallo, da ƙyar ta ƙarasa rufe gate ɗin da ƙirjinta ke amsa nauyinsa sannan ta wuce shi da niyar shiga cikin gidan.

''Ke dan ubanki come back here.'' dawowa ta yi baya a hankali haƌe da faɗin ''Gani.''

Sai da ya mata kallon some seconds sannan ya ce ''Uban wa kika barwa watering flowers ɗin gidan nan, abi na me you dey wait make i remind you tun da agidan ubanki ba ki saba ba?."

Ɗago kanta ta yi ta kalle shi ƙwalla na ziraro ma ta cikin sassanyar muryarta mai haɗe da kuka ta ce '' I'm sorry.''

Da ga haka ta nufi backyard domin ɗauko abin da za ta yi watering flowers ɗin.....

Manage please b yawa

THE REGRET.

Pending Amarya ce ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION.

THE NOBLE WRITER'S TEAM

*** Pending Amarya 40***

''Ke dan ubanki come back here.'' dawowa ta yi baya a hankali haɗe da faɗin ''Gani.''

Sai da ya mata kallon some seconds sannan ya ce ''Uban wa kika barwa watering flowers ɗin gidan nan, abi na me you dey wait make i remind you tun da agidan ubanki ba ki saba ba?."

Ɗago kanta ta yi ta kalle shi ƙwalla na ziraro ma ta cikin sassanyar muryarta mai haɗe da kuka ta ce '' I'm sorry.''

Da ga haka ta nufi backyard domin ɗauko abin da za ta yi watering flowers ɗin.....

Da ga haka ta nufi backyard domin ɗauko abin da za ta yi watering flowers ɗin.

Direct ɗakin shi ya nufa ya na mai shirya turarukkansa akan standing mirror ɗin.

** After 3 weeks**

Zaune take akan kujera ta na kallon TV ɗin ɗakin amma sam hankalinta ba ya kan kallon da take, yau sati uku kenan da fashewar wayarta da har yau bai ba ta ba, ga rashin chatting da Abbhinta da su Rashidat da ke ta ɗawainiyya da ita.

Tunanin kalar halin da Abbhi zai shiga idan ya kira ya ji wayarta a kashe ta ɗinga yi, duk ta rasa abin da ke ma ta daɗi, yaushe rabonta da ta ci abinci mai nauyi yau kusan wata biyu kenan tun barin Salimah daga gidan nan.

Cikin takunsa na ƙasaita haɗe da aura ɗinsa ya fito cikin shigarsa na manyan kaya black color wanda suka ma sa kyau matuƙa, ƙamshin sabon turarensa da ya canza ne ya fara ratsa ƙofofin hancinta, kafin ta kai kallonta garesa.

Sosai ya mata kyau girarsa da ta kusan haɗewa ta mugun tafiya da zuciyarta, lips ɗinsa da ɗan ƙyalli kamar wanda ya sanya lipstick.

Har ya ƙaraso inda take ba ta sani ba ta na aikin kallonsa, cikin muryarsa mai amo ya ce ''Biyo ni.'' still ta ƙafe shi da ido dan har ga Allah kawai lips ɗinsa ta ga ya motsa wanda suka ƙara narkar da zuciyarta, dan ta kasa dawo da kanta hayyacinta ita dai kawai ta tafi duniyar imagination.

Kallon 3 seconds ya mata ganin da gasken gaske ba ta san ma ya na wani magana ba ya sanya sa shinfiɗa ma ta wasu lafiyayyun ranƙwashi har guda biyu, wanda hakan ya sanyata dawowa hayyacinta.

''Za ki sanya hijabin ne ko za ki tsaya min halinki na biye - biye anan?." Ya faɗa tare da murtuke fuskarsa.

Cikin shashsheƙar kuka ta ce ''Na rantse ban ji ba.''

Tsaki ya ja kawai sannan ya wuce zuwa compound ɗin gidan, daman abaya ce ajikinta, mayafinsa kawai ta yana akai tare da shafa lipstick a saman laɓɓanta haɗe da zira slippers sannan ta fito zuwa compound ɗin.

Ya na zaune cikin motarsa ya yi balance ya na jiranta for almost 1 minutes.

niyar shiga motarsa take ƙoƙarin yi hakan ya sa shi ɗaga kansa haɗe da kallonta, cikin wani kalan tune ya ce ''What are trying to do?, ko ba ki san aikin ki ba?."

''I'm sorry bara na buɗe.'' daga haka ta nufi gate haɗe da buɗe shi gaba ɗaya, fita ya yi da motar tare da yin parking a ƙofar gidan sannan ya fito daga cikin motar, kallonta ya yi da kyau kafin ya cillo ma ta key haɗe da faɗin ''Kulle ki same ni à mota.'' da toh ta amsa tare da rufe gate ɗin da saka masa pad lock.

Bayan ta gama kullewa cikin motar ta shige tare da kulewa a hankali, da mugun gudu ya figi motar basu zarce ko ina ba sai rijiyar zaki, gidansu Aliyun.

****_____****

Acikin motar ma shiru ne ya ratsa motar, sannan a hankali ya ce ''Kin ga yadda za mu je gidan nan, You better behave yourself, Kuma kar kiyi min kauyanci ki yi ta pretending kamar kina jin tsorona, wallahi kika min haka ubanki za ki ci, ki min magana normal yadda kike wa samarin ki na da, idan ta kama You can touch my hand, ki min magana kuma in form of biyayya, wallahi kika min iskanci sai kin koma gida a ƙafa, kuma idan na riga ki zuwa gida ki sa ran ƙarewar rayuwarki na har abada, am I clear?." Nodding ɗin kanta kawai ta yi ba tare da ta kallesa ba idanunta na zubar da ƙwalla.

Horn ya yi mai ƙarfin gaske wanda hakan yasa mai gadi buɗewa da sauri, bayan ya faka motar a parking lot, saukowa ya yi ta na biye da shi jikinta sukuku, har suka ƙarasa babban falon gidan da gaba ɗaya family ɗin suke zaune, Sultana na chatting da wayarta, yayin da Mami da Abbuh suke kallo a tashar Aljazeera, shi kuma Sultan ya na kan dining ya na aiki da laptop ɗinsa.

Color fatarsa ya yi kyau sosai, ya yi fresh kayansa, jikinsa sanye da combat sai wani polo shirt ash color, ta ma sa kyau sosai ma shaa Allah.

Assultanah ce ta fara an karewa da su , hakan ya saka ta yin cilli da wayar hannunta haɗe da rungume Liyana da hannunta ke maƙale da na Hydar, da take ta ɗaɗɗari da shi.

Murmushi ta saki mai kyau haɗe da rungumeta ita ma, sannan ta kama hannunta suka ƙarasa cikin falon, har ƙasa ta durƙusa haɗe da gaishe da Mamin tare da Abbuh zuciyarta na wani kalar bugawa kamar zai fashe.

Bayan sun gama gaisawar Abbuh ya kira Aliyu dan akwai taron da zasu je, za'a bawa companyn Abbuh na takalma award, Soo zasu je amsa.

Tun shigowar Liyana Mami ta fuskanci yarinyar duk ta yi wani kalar rama idanunta duk sunyi zuru zuru, kamar mai shan wahala.

Kallonta Mamin ta yi da kyau tare da faɗin ''Fatima ki yi haƙuri ban samu time mun yi magana yadda ya dace ba a wancan ranar, sai kwanaki muke maganar da Neneh take faɗa min abin kusan dole ne, soo am sorry da yadda aka ɓillo miki da lamarin, hope kuma za ki zama good wife the way da kike ganin mahaifiyyarki na zaune da mahaifinki, we are all sorry rayuwar aure sai haƙuri, idan ba'a yi haƙuri da juna ba zaman ba zai taɓa yuyuwa ba, sai anyi haƙuri akan cimma nasara, gazawar haƙurin kuma kan haifar da mummunar ciwo na har abada, na san Hydar na da wuyar sha'ani most times, ki ma sa biyayya za ki ci moriyarsa, ki shanye duk wa ta muzanta ko ƙasƙanci da yake cikin rayuwar aurenki, Fatima.'' ta iddashe maganar tare da kiran sunanta.

Ɗago kanta ta yi tare da faɗin ''Na'am Mami.''

A hankali Mamin ta ƙara faɗin ''Babu wani aure da babu ƙalubale acikin sa, kowa sai da ya sha wahala sannan ya samar da gidansa, go ask everyone da kika sani yake da aure kafin ya zauna da ƙafafunsa acikin gidansa sai da ya fuskanci ƙalubale, even me ban cire kaina ba, though I don't know about your mom's side, buh kowa sai da ya fuskanci ƙalubale, ldan kika zama mace mai haƙuri, kin yi fice a wajen mijinki.'' ta ƙarashe maganar tare da gyara zamanta sosai.

Liyana kawai bin Mamin take da kallo ta na ya ba wayewarta, no one has ever told her this before, ita dai she lives her life ne kawai, ta yi duk wani badaƙalar da take

so,.money is available for her, her dad is available for all her need, soo she don't panic.

''I think lokacin sallah ya yi daga nan sai ku ɗaura girkin dare, ma za Sultanah kuje ku yi sallah ku mana girkin dare kafin Abbhu ya dawo.''

Ta ƙarashe maganar ta na kallon Sultan da ya zuba mu su idanu, wani harara Mami ta maka ma sa tare da faɗin ''ka wani tsare mu da ido ba zaka wuce ka fita wurin da ya aike ka ba sai ya dawo.''

''Mami fa har yanzu am heart broken à ɗinga lallaɓa ni.''

''ƙanin ubanka Wanda Qassim da zuwaira ba su haifa ba suka mutu, leave my presence, oloshi.'' (Ashe yaya Alih anan aka samo leave my presence 😂😂😂).

''Sorry Maa.'' daga haka ya ɗauki laptop ɗinsa da car key sannan ya fi ce daga falon, ita dai Liyana ko kallonsa ba ta yi ba, dan ta na kiyaye eye contact da shi a yanzu.

Hannunta Sultanah ta ja suka nufi kitchen ɗin tare, in less than 30 mins suka dafa lafiyayyan cous cous jollof da ya ci hanta da kaza, sai pepe soup da fruit salad da suka yi, duk da Sultana ce jagaba wajen ayyukan.

Sosai gidan ya ɗau ƙamshi y'an aikin har sun gama gyaran gidan sosai.

Mami ce ta fito sanye cikin wani Adire gown maroon color ta yi kyau sosai, a time ɗin har sun kammala komai akan dinning table ɗin.

A daidai lokacin kuma suka ji parking motoci a cikin compound ɗin, cikin minutes suka shigo shi da Abbhu hannunsa riƙe da award ɗin mai form of takalmin wanda aka kera shi da glass, amma kallo ɗaya zaka ma sa ka san cewa da diamond aka yi shi.

Bayan sun yiwa Abbhu sannu da zuwa, basu zauna ba suka wuce masallaci da Abbuhn da kuma Hydar, after 20 mins suka dawo gidan, suka ci abincin gaba ɗayan su amma ban da Sultan da har time ɗin bai dawo ba.

Sosai ta buɗe cikinta ta ci abincin, ƙarfe tara na dare ya ce da ita ta shirya su koma gida.

Lokaci ɗaya wani kalar baƙin ciki ya ziyarce ta mara misaltuwa, dan har Mami sai da ta yi noticing ɗin halin da take ciki.

''Fatima ba kya son komawa gidan na ki ne ko ƙaƙa?."

''A'a Mami, ban leƙa gidan Neneh ba ne kuma gashi har zamu tafi.'' taƙarashe maganar hawaye na zuba a idanunta.

Ga mamakin Mami sai kawai ta ga hawaye a fuskarta ta na gogewa.

Ita tun shigowar su daman yadda ta ga yarinyar wani iri duk a rikice ta san ba lafiya ba, kamar yarinyar ba ta jin daɗin gidan Aliyun.

''Is Okay daughter, Aliyu maza ka kaita wurin Neneh sai ku wuce.''

Da toh ya amsa tare da kama hannunta suka fice daga gidan gaba ɗaya.

_____

Ɓangaren Neneh kam kullum sai sun yi hirar Liyana da Salimah, ta na ba ta labarin yadda Hydar ke kula da ita.

Cikin muryarsa mai amo yayo sallamar hannunsa sarƙafe da na Liyanar suka ƙaraso cikin falon.

''Dan halak ya ƙi ambato, ku ce shegun kuna kusa, toh Allah yaso ni alherin ku nake faɗa ba sharrin ku ba balle ku ɗebe min albarka." Nenehn ta faɗa ta na gyara zaman glasses ɗinta.

Har ƙasa ta durƙusa cikin sassanyar muryarta ta ce "Nda Dubdo Neneh."

Amsa gaisuwarta Neneh ta yi tare da faɗin.

''Yau kuma da wannan salon aka zo kenan.''

A fakaice Liyana ta dallah ma ta harara wanda hakan ya haɗa idanunta da Nenehn.

" A uzubillah, Fatima mai ya sami fuskarki ta yi baƙi haka kamar lantarki?, Aliyu a haka na baka jiƙata ko zallar baƙin halinka ne haka?."

" Malama za ki tashi mu tafi tun da kin ganta, ko jiƙata za ki yi ki shanye?." Ya yi maganar tare da ɗago kansa daga wayarsa da yake dannawa.

Kamar za ta yi kuka ta ce " Neneh sai da safe."

" Allah ya tashe mu lafiya, kai dai Aliyu ko a aljanna na ganka sai na tambayi sababi, dan har ga Allah kallo ɗaya za'a yiwa jiƙata aga wani kalar baƙi da tayi kamar hadari, toh daman dai wajen ƙiba bana ce ka ramar da ita ba saboda daman can ko skeleton ya fi ta ƙiba."

Cikin muryarsa mai amo ya ce" nifa Neneh kar ki jefa ni à bakin duniya, ciki ne da ita, laulayi take, sai ki barni na huta ai ko?, ke kuma taso mu tafi.''

Daga haka ya finciki hannunta suka koma can gidan nasu, ko ledar da Sultana ke bata, ba ta bi ta kansa ba ya wulla ta cikin motar tare da mata key suka bar gidan.

''Ke dan ubanki ba nace dake you should feel free ba, kiyi rayuwarki yadda kika saba ba?." Ya tambaye ta ya na wani kalar zaro idanunsa waje, wani kalar karkarwa jikinta ya soma yi, sannan a hankali ta ce ''Please, ka bar ni ko fuskar iyayena na gani i don't think idan na cigaba da rayuwa da kai zan kai labari, ban san tsoro ba, kai ka fara sanar da ni, ban san menene zubar hawaye ba a silar ka na san hakan, please and please, for once ka barni na shaƙi iskar farin ciki arayuwata, honestly na gaji am tired please.''

''Okay ni da ke mun zama sa'anni da har za ki kalli idanuna ki gaya min magana san ranki ko, ko dan na riƙe hannayenki yau a tunaninki shinfiɗa na haɗa dake?, is alright, za ki wuce ki buɗe gate na shigar da mota ko sai na ɓaɓɓalla ki?."

Ba ta tanka ma sa ba ta ɗauki key ɗin tare buɗe ma sa haɗe da buɗe gate ɗin gidan, da gudu ya shigo cikin gidan haɗe da parking motar a wajen da aka tanada.

Hannunsa riƙe da award ɗin da Abbuhn ya bashi ya ajiye a wurinsa ya fito daga motar, ya na kallon yadda take kiciniyar kulle ƙofar.

Da ƙyar ta gama sannan ta wuce backyard ta kunna solar, haɗe da watering flowers ɗin gidan gaba ɗaya.

Sai wajen 12 na dare ta kwanta, kasa bacci ta yi saboda tunawa da Birthday ɗin Abbhi da ta yi, wanda al'adarta ce ita ke fara yi masa wishes da gifts.

Wani kalar fashewa da kuka ta yi ta na mai ƙanƙame jikinta, murɗa handle ɗin ƙofar aka yi tare da shigowa cikin ɗakin, wanda daman ba ta kulle ƙofar ba, dan ya sha mata warning akan kulle ƙofa, akan hakan ma ya sha mata duka, jikinsa sanye da pyjamas white color ta janye sleep mask ɗinsa zuwa kan gashinsa, hannunsa sanye cikin aljihunsa.

Kallonta ya yi cikin shigar kayan baccinta pyjamas purple color, buh wandon is short, kanta sanye da hula, santala santalan cinyoyinta ya bi da kallo da sai wani kalar sheƙi suke, dan yanzu ba ta kwana babu haske tun da ta na rashin waya.

''Am even regretting why ƙanwar ki ta ɗauki number na ta bawa mahaifinki, kusan kullum sai ya min 10 miss call I donno ko ba shida aikin yi ne.''

Ba zato babu tsammani ta ji kawai ta yi wani mugun fashewa da wani kalar kuka mai cin rai, ita arayuwarta da a zagi Abbhi gwara a zagi Ammi, dubi filthy words da yake faɗawa mahaifinta fi sabilillahi.

Dailing number Abbhinata ya yi tare da miƙa ma ta wayar, ring ɗaya kamar jira ake ya katse kiran haɗe da biyo kiran, ''Hello dear, kin wuni lafiya?."

Sai da ta kalli fuskarsa sannan ta ce ''Ina wuni Abbhi, ya gida, ya su Ammi da Ilham?."

Sai da Abbhi ya yi yʻan sakanni, because all his life Liyana ba ta taɓa gaida shi cikin ladabi haka ba, sannan a hankali ya ce ''Lafiya lau, kowa lafiya, mai sa muryar ki ya yi sanyi haka rashin lafiyar ne har yanzu?, ga shi kusan last 3 weeks kika ce za ki zo, ba ki zo ba?."

Ita ta manta da wani Hydar ma a kusa da ita cikin wani ɗan murya mai nuna zumuɗi ta ce ''Kaji Abbhi da wani zance, Allah na tuba sai ka ce baka san gidana ba, kai ba zaka zo ba ni zan ta zuwa?.'' ta yi maganar ta na wani kalar dariya haɗe da rufe bakinta da hannunta.

A ta can ɓangaren Abbhi ya ce ''Daughter kin manta birthdayn Abbhinki kenan?."

''Allah sarki Abbhin Liyana kar kayi fushi kana can cikin raina, wallahi riga ni faɗa kawai ka yi, toh Happy Birthday,my rock, Allah ya kawo shekaru masu Albarka.''

''Yeah Daddy's girl.''

''Abbhi am a lady not a girl manaa.''

Ta yi maganar ta na turo baki.

''I will come tomorrow in shaa Allah, let's goo for our annual shopping.'' Abbhin ya faɗa ma ta tare da yi mata sai da safe.

Wani banzan kallo ya watsa mata sannan ya ce ''Sai in ga uban da zai fita gate balle yaje shakatawan.'' daga haka ya fice daga ɗakin.....

Manage please b yawa

THE REGRET

PENDING AMARYA CE ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION

The Noble Writers team.

Pending Amarya 41

What goes around comes around □ □

Try to be a good father to your children not a cowed □ □ □

Not edited □□□

****

Wani banzan kallo ya watsa mata sannan ya ce ''Sai in ga uban da zai fita gate balle yaje shakatawan.'' daga haka ya fice daga ɗakin.

Da ido ta bi shi har ya fice daga cikin ɗakin, sannan a hankali tayi kwanciyarta haɗe da rungume jikinta, bacci mai daɗi ya yi awon gaba da ita.

****

Washegarin ranar da sassafe ta tashi domin shirya abubuwan da za tayi ta koma bacci tun da har yanzu bai barta ta koma makaranta ba, hakan ya sa lokacin ta a barci da aiki take ɓata shi.

Sai da ta gyara gidan tsaf sannan ta ɗaura chips da plantain da yanzu hannunta ya faɗa sosai a sarrafa su a yanzu.

Bayan ta gama jera abincin a dinning table kitchen ɗin ta koma domin haɗa masa coffee kafin ya dawo daga gym, ƙarar buɗe ƙofar da ta ji ne ya sanya ta rikicewa.

Direct kitchen ɗin ya nufo tare da duba coffee maker ɗin domin haɗa coffee, ganin coffee akan kitchen island ne ya sanya shi kallon kitchen ɗin dan ganin ta inda za ta ɓillo.

''Kina ina?, za ki fito daga bayan ƙofar nan ko sai na ba ki dirty slap wanda za ki ga kan ki a gidan ku.''

A hankali ta fito daga bayan ƙofar kanta a ƙasa ta na wasa da hannayenta, wani shegen kallo ya bita da shi tare da faɗin ''Sau nawa ina faɗa miki ki daina haɗa min coffee a gidan nan?."

Fashewa ta yi da kuka haɗe da ɗaga hannayenta ta na ma sa alamar biyu.

''zan kwashe ki da mari idan ba ki min magana yadda na miki ba.''

Cikin shashsheƙar kuka ta ce ''Sau biyu yau ne na uku.''

''Alright, tun da ke naga ba kyau jin magana is like ba kya son rayuwar da babu punishment, ki zauna kayan ki ba tare da kin shiga harkokina ba ke ba kya jin daɗi, ya'r tusai ba kwarjini, i command you ki wuce ki gyara min ɗakina, ko da wasa kika min abin da ba shikenan ba yau ɗinnan na lahira sai ya fi ki jin daɗi, oya!."

Ya yi maganar tare da yi mata pointing ƙofar.

Jikanta a sukwane ta nufi hanyar corridor ɗinsa idanunta na fidda hawaye, a hankali ta buɗe ƙofar ɗakin, falo ne mai kyau sosai babu tarkace kallo ɗaya za ka masa ka ga luxury living room, it looks rich and elegant, parlourn bai yi wani datti ba sai wani kalar zallar ƙamshin turarensa dake tashi kamar ya na cikin ɗakin.

A hankali ta fara tattare falon duk da ba wani lalacewa ya yi ba, kawai tsabar tsafta ce irin na Hydar amma ai babu abin da falon ya yi hakan ya sa ta kawai mopping ɗinsa ta yi sannan ta shiga master room ɗinsa da ko ina yake tsaf tsaf, standing mirror ne kawai yake ɗan hargitse daga shi babu komai a ɗakin da za'a gyara, dan alamu sun nuna kullum sai ya gyara ɗakinsa da kansa.

Mirror ɗin ta nufa tare da ɗaukan glass cleaner da towel ta fara goge mirror ɗin, mistakely jikinta ya gogi turaren da aka ajiye shi ba dai-dai ba, hakan ya sa turaren faɗuwa a ƙasa tare da fashewa, wani kalar ihu ta saki wanda a garin juyowa shima kansa madubin ya biyota ya tarwatse a ƙasa, kalar mirror ɗin nan ne wanda ake jingina shi akan standing ɗinsa.

Wani kalar kakkarwa jikinta ya fara yi wanda hakan ya sanyata fashewa da kuka tare da tisa mirror da turarukan agabanta ta na kallonsu.

Ta ma rasa wani kalar addu'a za ta yi, hakan nan ta tsinci kanta da faɗin ''La 'ila ha illa anta subahanaka inni kuntu minal lil zali min.''

Haka tai ta nanatawa ta na kuka.

Ganin ta kai kusan hour ɗaya har yanzu ba ta fito ba ne ya sanya shi hawa saman a fusace tare da tura ƙofar ɗakin, zaune ya ganta agaban mirror ɗin dake zube a ƙasa duk dakin ƙamshi ya baibaiye shi wanda hakan ya bashi tabbacin cewa turarensa ne suka fashe.

Kallonta ya yi sosai tare da faɗin ''Gyara na ce ki yi ko ɓarna?."

Cikin shashsheƙar kuka ta ce ''Dan Allah dan Annabi ka yi haƙuri, wallahi ban san ya akayi ba sharrin shaida'n ne.''

Ta ƙarashe maganar ta na kneeling da ƙafafuwanta hannunta ta na alamun pleading da shi.''

Kallonta ya ƙara yi da kyau tare da kaudar da kan sa gefe haɗe da faɗin ''Kina da zaɓi biyu, na ɗaya, za ki bi ta kan glasses ɗinnan ki wuce ki fita, na biyu kuma za ki frog jump za ki zagaye compound ɗin gidan nan sau goma.''

Ƙura mai idanunta ta yi na ya'n daƙiƙu, sannan a hankali ta fara tunanin gwanda ta jewa zaɓi na biyu, akan ta yi jinya kuma dole ne ta yi aikin gidan.

" I choose the second punishment." Ta faɗa a sanyaye.

Press ɗinsa ya buɗe tare da ɗaukan wani bulalar fata mai baki biyu, wanda ya siye shi da daɗewa.

Zaro idanunta ta yi waje ba tare da ta yi magana ba ta bi bayansa ganin har ya fice daga ɗakin.

A lokacin har sha biyu ta gota wani kalar rana ake yi mai zafin gaske.

*****

Ɓangaren Abbhi kam tun bayan da suka yi waya da Liyanar sa yake jin wani kalar farinciki, dan Rufy ji take kamar ta mauje shi, dan sam - sam ba ya barin su su wataya a gidan sanadiyyar shaiɗaniyyar yarinyar da yake kira favorite, ita matsalar ta ɗaya yadda doctor ya ce mahaifarta ba zai iya ɗaukan ciki ba, shi ne babban damuwarta a yanzu.

Da sassafe ya fara shirye-shiryen zuwa gidan Liyanar saboda suje shopping ɗin da suke yi duk shekara idan birthday ɗin waninsu ya zagayo a gidan, wani black color tissue yard ya saka wanda suka masa mugun kyau na fitar hankali.

Cikin shigarta na Abaya Ammi ta shigo ɗakin na sa tare da ajiye ma sa break fast cikin sanyin muryarta ta ce " Abbhinsu Happy Birthday, Allah ya ƙaro shekaru masu albarka unlimited money in your account."

Sai da ya ɗan kalleta sannan ya yi ɗan murmushi da suka tsaya a iya lips ɗinsa tare da faɗin ''Amin Iki dear, Finally yanzu kin girma, da wannan breakfast ɗin da kika kawo da kin sha ranƙwashi, kin taɓa ganin na sha hollandia yourghurt ba strawberry hollandia ba?." Ya yi maganar ya na kallonta sosai.

A hankali ta ce ''Ayi haƙuri Yallabai strawberry ɗin ne ya ƙare shiyasa, amma bari a mayar.''

Ta yi maganar tare da kai hannunta kan tray ɗin.

A hankali ya ce ''Just leave it I will manage.''

Murmushi ta sakar ma sa mai kyau tare da faɗin ''Your wish is my command sir, thank you Sir.''

Daga haka ta baro ɗakin.

Till date ta na matuƙar son Nabil ba ta son wani abu da zai ɓata mata ransa.

Bayan ya gama breakfast ɗin ma sai arround 12 ya fito domin zuwa gidan Liyanar, Ammin na ma sa a dawo lafiya.

A hanyarsa na zuwa gidan Liyanar ma sai da ya biya ta Boutique ya mata siyayya sosai, daga kan palazzo trousers da jeens skirts, da boots, da shirts babu abin da ya manta, sosai ya mata shopping, dan so yake ya ga murmushi a fuskar mafi soyiwa a wajensa.

Ya ɗan sha wahala wajen gane gidan Liyanar saboda ko ranar da yazo shi da Ilham, da daddare suka zo gidan, kuma Ilham ce ta yi driving ɗin motar dan zuwan bazata ya mata, kuma a time ɗin da ita yake waya, shiyasa da ƙyar ya gane gidan.

A hankali ya fara horn a daidai luxury gate ɗin, ganin ya ɓata kusan mintuna biyar ba'a buɗe ma sa gate ɗin ba, ganin small gate ɗin a buɗe ne ya sanya shi canza shawara haɗe da yin parking ɗin motar ta sa a wajen gidan.

Fuskarsa ɗauke da ɗokin ganin ɗiyar ta sa ya buɗe motar haɗe da fitowa daga cikin motar hannunsa riƙe da ledoji wanda ke cike da kayayyaki na alfarma.

Unguwar shiru take babu wani hayaniyya abin ka da unguwar masu hannu da shuni, a hankali ya ƙarasa bakin gate ɗin tare da buɗe ƙofar a hankali.

A tsugunne take idanunta na fiddar da zallar hawaye, fararen ƙafafunta babu slippers, hannuwanta na kame da kunnuwanta, wanda dukkan alamu sun nuna frog jump take.

Tsayawa ta yi da niyyar hutawa, hakan ya sanya shi ɗaga bulalar hannunsa, haɗe da zula ma ta shi a gadon baya, wanda hakan ya sanyata sakin wani ƙara haɗe da wani kalar nishin wahala, ka na ta saki kuka mai mugun cin rai.

A hankali aka turo ƙofar haɗe da shigowa cikin compound ɗin gidan, idanunsa suka ma sa mummunar gani, ganin Liyana acikin rana, shi kuma Hydar ya na zula ma ta bulala kamar an jefo shi.

Take Abbhi ya saki ledar hannunsa wanda hakan ya jawo hankalin Liyanar da Hydar ɗin suna mai kai duban su wajen gate ɗin.

Cikin muryarsa mai amo ya ce ''Abbhi ina wuni.''

Cikin wani kalar murya wadda ba ta fita sosai Abbhin ya ce ''Riƙe gaisuwarka ba na buƙatar ta, Liyana kwaso kayan ki mu tafi.''

Cikin wani kalar murya wadda ba ta fita sosai ga wani kalar kuka da take ta ce ''Abbi kayi haƙuri bazan iya rabuwa da mijina ba ko da ka d'auke ni gangar jikina ka d'auka sabida my heart and soul will be left in this house, Just pray for me Abbhi ka faɗawa Amminah I really need her prayers.'' ta yi maganar haɗe da goge hawayenta, ta na mai kallon Abbhin da ya matso dabb da ita.

''Are you out of your mind?, ta ya kike tunanin zan barki acikin wannan gidan a kuma halin da kike ciki, anya ba ki fara zarewa ba?.''

Cikin murya mai sanyi ta ce ''Abbhina ni ina son mijina, ba zan iya barinsa ba, and I know what I'm doing, Abbhi just go and seek Ammi's forgiveness, na san duk abin da ta fuskanta acikin gidanka, akwai wani da ga danginta da suka zo suka ɗauketa?, ka tafi kawai na girbi abin da ka shuka, my hope and prayers shi ne punishment ɗin ya tsaya a kaina kar ya taɓa min lly, just goo and pray for me.''

Ta ƙarasa maganar tare da tashi tsaye.

Murya a sanyaye Abbhi ya ce ''Daughter please.''

''Abbhina not now, yaushe muka fara arguing?, just goo okay, I'll be fine, ai wuya ba ta kisa.''

Jiki a sanyaye Abbhin ya fice daga gidan tare da tayar da motarsa ya bar unguwar idanunsa na zubar da wasu hawaye masu zafin gaske.

Ita ma tun fitar Abbhinata take wani kalar kuka take mai tsuma zuciyar mai sauraro.

Wani kalar bulalan da aka zula ma ta ne ya dawo da ita daga nisan kiwon muzuran kukan da take.

''Shhhhhhhh.'' ya faɗa haɗe da yi mata alaman da tayi ma sa shiru, haɗiye kuka ta yi tare da ziraro da wasu kalar hawaye masu zafin gaske.

A hankali ya ajiye bulalar dake hannunsa a ƙasa tare da ɗaga wayarsa dake ring da sunan Amir ke ta yawo akan screen ɗin.

''Assalamu alaikum Man.'' Amir ya faɗa ta ɗayan ɓangaren.

''Wassalamu alaykum Bud buddy.'' Hydar ya amsa ma sa.

''Man flight ɗinka is tomorrow in shaa Allah, sai ka fara shirye-shirye, amma sai ka je Lagos first thing in the morning, because babu jirgin direct daga kano har yanzu.''

Wani kalar tsaki Hydar ya ja tare da faɗin ''Okay Buddy, buh you told me, kayi min suggest na sunan Ac ɗin nan, i want anything to be intact before morning.''

Wani kalar dariya ya yi tare da faɗin ''Yeah..... Yeah we are still on it ai, karka ji komai kawai, yanzu ma ina hanyar zuwa Barakat ne zan biyo ta gidanku, how's Amar.....''

Amir bai ƙarasa ba ta yi ƙit ya kashe wayar.

Wani banzan kallo ya dalla ma ta fusakarta har a sannan ba ta daina hawaye ba.

A hankali ta fara motsa baki kamar mai shirin magana, bai barta ta faɗi abin da ke ranta ba ya ce ''Za ki tashi ki wuce ciki ko saina bubbuge miki baki?."

A hankali ta tashi jikinta ba lakka, ta na mai jan ƙafafunta da suka ma ta tsami.

Direct ɗakinta ta nufa ta na mai shiga toilet haɗe da haɗa ruwa mai zafi a jacuzzi.

Ta fi kusan 30 mins a ciki sannan ta fito daga banɗakin, goge jikinta ta soma yi tare da shafa mai, muryar Abbhi na mata ringing bell a kunne.

Wani kukan ta fashe da shi, tare da ƙarasa shiryawarta.

_____*

Bayan Abbhin ma ya koma gida bai zame ko ina ba sai ɗakin Ammi dake yiwa Ilham kitso, da hawaye a fuskar shi, ya ƙaraso cikin ɗakin, ganin hakan ya sa Ilham fita daga cikin ɗakin, kansa ya ɗaura akan cinyar Ammi haɗe da fashewa da wani kalar mahaukacin kuka.

''Subhanallahi, Abbhisu what's wrong?."

Atake wani kalar zazzaɓi ya kama sa hakan ya sa shi fara kakkarwa atake, paracetamol ta na sa tare da lulluɓe shi, wanda hakan ya sanya shi bacci a take.

Cikin shigarta na normal abaya mara kwalliya ta fito ƙafarta sanye da slippers, kanta sanye yake da normal hula.

Dubanta ta kai tsakiyar falon da yake zaune cikin wani jeens trouser mai kyau da T-shirt white color, sai wani soft slippers dake sanye da ƙafarsa, hannunsa riƙe da mug ɗin coffee.

Ajiye mug ɗin ya yi tare da kallonta tare da faɗin ''Muje.''

Duk da yunwar da take ji hakan bai hana ta binsa ba, backyard ya nuna ma ta, hakan ya sa ta ɗaukan kayan aikinta ta fara gyara flowers ɗin gidan haɗe da musu ban ruwa.

Horn aka danna a ƙofar gidan hakan ya sa shi kallonta tare da faɗin ''Heys, je ki buɗe ƙofar nan, and be fast don't keep him waiting.''

Da sauri ta nufi hanyar gate ɗin da buɗesa ya zame ma ta jiki, tare da buɗe shi da ƙyar.

Da gudu Amir ya shigo da motarsa ƙirar BMW cikin compound ɗin gidan tare da parking ɗin sa a kusa da water fall ɗin gidan.

Saukowa ya yi cikin yadinsa na white color tare da ƙarasowa wajen da yake tsaye, rungume junansu suka yi tare da kuma yin musabaha duk a lokaci ɗaya.

Kallon Liyana ya yi tare da faɗin ''Uwargida agidan Hydar." Murmusawa ta yi a hankali tare da faɗin '' Ina wuni, Ya Amir.'' ''Lafiya lau, mai kike ba wa abokina ya yi wannan ƙiba haka kamar wani bons.''

Kafin ta bayar da amsar Hydar ya caɓe tare da faɗin ''Ita wannan ɗin, sai aka gaya maka wife material ce?, ke get us something liquid dallah kika tisa mu agaba kamar sa'annin ki.''

Wani ƙwalla ne ya taho ma ta ta yi sauri ta share tare da wucewa cikin building ɗin.

Cikin wani resin tray, ta zuba musu coke haɗe da Hollandia, sai kuma wani chips ɗin leda da ta zazzage acikin bowl.

A hankali ta fito tare da nufar cikin wani ɗan rumfar shakatawa dake cikin gidan ta na mai ajiye musu shi akan table ɗin da yake a wajen.

''You see barb, ka ga abin da nake ma ka complaining kenan, yanzu da ta kawo wannan abun da mai za'a sha, kee where is the glass cup?."

Cikin sassanyar muryarta ta ce ''Ya na ciki kitchen.''

''Wuce ki ɗauko, before I hose you slap.''

Cikin tattausar murya Amir ya ce ''Hydar calm down mana.''

''Amir don't tell me to calm down, ba ta iya girki ba, ba ta iya magana ba, ba ta san wannan kayan na cikin gidane ko na fita yawo ba, babu abin da ta iya sai rawa a social media, who does that, a haka kake cemin na koyi sonta?, babu wannan qualities ɗin mace ta gari a tattare da ita, Amir ba'a tauye ni ba a tunanin ka?." Ya iddashe maganar a zafafe tare da tashi tsaye.

Tun da ya fara maganar hawaye ke zuba a idanunta, kanta na ƙasa ta na wasa da hannunta.

Ajiyar zuciya Amir ya sauke tare da faɗin ''Ka ga ta fifita ka akan family ɗinta for the sake of the love that she had for you, ta ci wannan alfarmar mana Man.''

''I didn't ask her to sercrifice them to me.'' ya yi maganar ya na ɗaura hannayensa kan kujerar wurin.

Kallonta Amir ya yi tare da faɗin ''Shige ciki, zan neme ki Okay.''

Cikin muryar kuka ta ce ''Na gode Ya Amir.'' da ga haka ta fara ƙoƙarin komawa gidan.

''Malama wajen aikin ki za ki koma." Ya faɗa a gadarance, nodding kanta kawai ta yi tare da wucewa wajen favorite flowers ɗinta, wato tulip flowers.

Wani kalar tsaki Hydar ya ja tare da ƙoƙarin barin wajen, da sauri Amir ya dawo da shi ba ya.

''Wallahi Amir idan ba ka sake ni ba zan mare ka a wajen nan....."

THE REGRET

PENDING AMARYA CE ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION

The Noble Writers team.

Pending Amarya 42

What goes around comes around □ □

Try to be a good father to your children not a cowed □ □ □

Not edited □□□

Cikin muryar kuka ta ce ''Na gode Ya Amir.'' da ga haka ta fara ƙoƙarin komawa gidan.

''Malama wajen aikin ki za ki koma." Ya faɗa a gadarance, nodding kanta kawai ta yi tare da wucewa wajen favorite flowers ɗinta, wato tulip flowers.

Wani kalar tsaki Hydar ya ja tare da ƙoƙarin barin wajen, da sauri Amir ya dawo da shi ba ya.

''Wallahi Amir idan ba ka sake ni ba zan mare ka a wajen nan....."

****

Cikin muryar kuka ta ce ''Na gode Ya Amir.'' da ga haka ta fara ƙoƙarin komawa gidan.

''Malama wajen aikin ki za ki koma." Ya faɗa a gadarance, nodding kanta kawai ta yi tare da wucewa wajen favorite flowers ɗinta, wato tulip flowers.

Wani kalar tsaki Hydar ya ja tare da ƙoƙarin barin wajen, da sauri Amir ya dawo da shi ba ya.

''Wallahi Amir idan ba ka sake ni ba zan mare ka a wajen nan."

Murmusawa Amir ya yi tare da faɗin ''dake an gaya maka Liyana ce ni sai na tsaya ai ka mareni.''

Tsaki Hydar ya ja tare da zama akan kujerar wajen tare da faɗin ''Ina jinka ka faɗi abin da yake tafe da kai.''

Sai da ya ɗan nisa sannan ya ce ''Yanzu tsakanin ka da Allah ace Assultanah ake yiwa hakan za ka ji daɗi?, kwata -kwata wannan rashin girki dasu waye- waye, duk ba hujja ba ce, can't you teach her how to do it?, ko ba ka iya ba?."

''Amir kayi maganar da ta shafeka ba na son third person acikin alaƙar dake tsakanina da mata ta.''

Wani dariya Amir ya sheƙe da shi tare da faɗin ''Awwww habaa..... Su third person manya, da kan ka za ka zo ka same ni wallahi Aliyyu, zo ka raka ni please.'' Amir ya iddashe maganar tare da ɗaukar key ɗin motarsa daga kan table ɗin wajen.

Tsaki Hydar ya ja sannan ya ce ''Ba ka faɗa min sunan da zan saka ba kuma a ACn.''

Sai da Amir ya duba agogon dake ɗaure a tsintsiyar hannunsa sannan ya ce ''Idan ka raka ni sai na faɗa maka a mota.'' daga haka ya fice daga cikin rumfar domin shiga cikin motarsa.

Wani ɗan gajeren tsaki Hydar ɗin ya ja tare da binsa cikin motar.

Ganin sun shige cikin motar ne ya sanyata saurin buɗe gate ɗin gidan haɗe da yiwa Amir waving ɗin hannu alamun sai anjima.

Da sauri ta rufe gate ɗin tare da shigewa cikin living room ɗin, direct wajen dinning ta nufa tare da buɗe warmers ɗin abincin, ta ga wayam babu komi, fashewa ta yi da kuka tare da ɗauko indomie ɗanya ta soma ci ta na korawa da hollandia.

Sai da ta ƙoshi sannan ta yi sallar azahar tare da la'asar, sannan ta hau gyaran gidan da babu abin da ya same sa.

****

Bayan ya tashi daga baccin ta shigo cikin shigarta na koda yaushe wato classic Egyptian abaya, wanda ya gaji da haɗuwa.

Ƙarasa shigowa ta yi ta ganshi a kwance, kamar yadda ta bar shi bayan ta ɗan watsa masa ruwa, a hankali ta ƙaraso wajen da yake tare da fara kiciniyar ɗago shi daga kwancen da yake, dake Abbhin ginannan jiki garesa hakan ya sa ta zubewa ajikinsa tare da ƙurawa kyakkyawar fuskarsa idanunta masu bala'in tafiya da guntun imaninsa.

A hankali ya fara sauke idanunsa ya sauke su akan fuskar kyakkyawar black beauty ɗin matarsa, ƙarasa buɗe shanyayyun idanunsa ya yi tareda sauke su akanta ganin gaba ɗayanta akan faffaɗan ƙirjinsa.

''Iki.'' ya furta cikin wata kaliyar murya wadda ta daɗe ba ta jisa da ita ba.

A hankali ta tashi a jikinsa tare da zama kusa da kansa ta na mai ɗora kansa akan cinyarta yadda za ta kalli fuskar na sa sosai.

Ajiyar zuciya ta sauke tare da faɗin ''Naam Yaya, mai ke damun ka?."

Fashewa ya sake yi da kuka kamar wani yaro tare da faɗin ''Iki nah Ina yi DANA SANIN duk wani abin da ya faru a shekarun baya, please and please, I'm Soo soo sorry, na amshe ki da hannu bibbiyu ki zame min mata, ki haifa min yara maza, su cika gidan nan, wallah ina matuƙar son ki tun a baya, is just that you're not how I expected, shi ne ya dagula al'amurran, Ni kuma na san ke nutsatsiyya ce, buh you see that lady we called Rufaidhat is a devil, she ruin everything, wallahi ita ta ɗinga poison zuciyata na yi ta wulaƙanta ki, dan Allah ki yafe min, Our daughter is now facing the same trauma, violence wanda ya fi wanda na miki.''

Ya ƙarashe maganar ya na kamo kumatun ta daga kwancen da yake idanunsa na zubda ƙwalla.

Ita ma Ammin hawayen take sannan kuma cikin sassanyar muryarta ta ce ''Yaya, wallahi ni na yafe maka, buh you know karma, bai damu da ita ɗin ya'ta bace, Yaya i loose my virginity ba da son raina ba I'm ashamed to tell you people that I'm not a

virgine and duba da yanayin zamanin mu banyi wayewa da zance zan yi taking wani action ba, kuma is our principal,shi ne yayi min, i cried kamar babu gobe, kuma har yau kukan nake ban daina ba, buh I later received a message that ya mutu, tun a ranar na yafe ma sa, kuma kai ma na yafe ma ka.''

Ta ƙarashe maganar ta na fashewa da kuka.

A zabure ya sauko daga kan lallausar katifar dake ɗakin tare da kneeling da ƙafafuwansa haɗe da faɗin ''Na zubar miki da ciki har sau bakwai, na hana ki bacci dare rana kullum cikin takura miki, na hana ki ƙarasa makarantar ki wanda har yau a grade6 (jss3) kika tsaya a school, na saka kowa ya tsane ki a dangin mu, na sa ya'rki ta farko ta kasa sakin jiki dake, na kori dukkanin ƙawayen ki da suka zo gida na, na mai da ke mai gadi, mai bawa flowers ruwa, mai wankin mota, mai wankin kayana da na yaran, motsin kirki na hana ki acikin gidan nan, amma still Ikimat kika yafe min?." Ya ƙarashe maganar tare da nuna kansa, hawaye sosai a fuskarsa.

Sassanyar murmushi ta yi haɗe da faɗin ''Yaya kenan, forgive and forget menene ma duniyar, dududu yaushe ya rage a tasheta, let bygones be bygones, That's all, and focused on your way to achieve something big in life, ni ban riƙe ka da komai ba Allah ya yafe mana kawai, amma ni yanzu you're free.'' ta yi maganar haɗe da murmusawa ta na mai lanƙwasar da kanta gefe.

Da sauri ya tashi haɗe da rungumeta tsam jikinsa, ya na mai shi ma ta albarka tare da faɗin ''Zo ki bani twins yau ɗinnan.'' a take muryarta ta sauya cikin wani kalar murya ta ce ''Yaya ka manta ba nida mahaifa?."

Ajiyar zuciya suka sauke a lokaci ɗaya tare da ƙara shi ma ta albarka.

****

Sai misalin ƙarfe goma Amir ya sauke shi abakin gidansa, tun ya na cikin motar Amir, yake jin wani kalar ciwo a wajajen ƙasan cikinsa, dakewa ya yi kawai, sannan ya matsawa Amir ɗin da ya juyo da shi gida, dan wai kaisa zai yi wajen wa ta girl ɗinsa, dan Amir ya na zuba life dai-dai gwargwado.

Wani kalar mahaukacin bugu ya ke yiwa ƙofar wanda atake, sai da ta zabura, daman already ta shirya cikin kayan baccinta waya'nda ba sa wani rufe ma ta jiki na arziƙi, da sauri ta zira slippers ɗinta tare da buɗe ƙofar gidan, a tsaye yake hannunsa dafe da cikinsa, ya ƙarasa shigowa cikin gidan.

Da idanu ta bi shi tare da ƙarasa kulle gate ɗin da pad lock, sannan ta bi bayansa a hankali, dan kar ta yi wani laifin.

Sauri ta yi ta shige gabansa tare da wani ɗan gudu, wani kalar ƙara ya saki ya na mai ƙara dafe cikinsa.

A take ta yi pause a wajen kamar wadda aka sawa remote, tare da waigowa ta na kallon yadda ya runtse idanunsa dake hasken falon ya na reflecting wajen da suke.

Ɗago jajayen idanunsa ya yi tare da ƙafeta da su ya na ma ta wani kalar kallo da bai taɓa ma ta irin da baa.....

Love is blind 😊

THE REGRET

PENDING AMARYA CE ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION

The Noble Writers team.

Pending Amarya 43

What goes around comes around □ □

Try to be a good father to your children not a cowed □ □ □

Not edited □□□1

****

Sannan suka fara harraman tafiyya, tsayar da su Mami ta yi tare da kawo musu wa ta leda dake cike da turaruka.

''Amaryarmu har za ki tafi.?"

''Eh Yaya Amir, sai anjima.'' ''Okay dear.''

Daga haka suka fice daga gidan.

Tun a ƙofar gate ɗin suka fara dariya, Ilham na ta kwaikwayon Liya yadda take wani sissinne kai kamar mayya.

Banza ta yi dasu tare da shiga cikin gidan Nenehn da har motarsu Abbhin na pake, alamun sun dawo gidan.

<><><><><><><><><><><><><><><><><><><><

A kwance yake yau ɗin bayan ya dawo daga meeting ɗin da suka yi da ADAFAR VENTURES na Singapore akan kayan da suke son a siyar musu da shi, laptop ɗinsa a kan cinyarsa sai wayarsa a hannunsa ya na kallon wasu reels a Instagram. Sannan ya ga saƙon Amir alamun ya turo ma sa hoto.

A hankali ya ajiye laptop ɗinsa tare da shiga cikin message ɗin, zaune take ta na wasa da hannunta abinci a gabanta, sai ɗayan kuma ta ɗan cuno baki alamun kamar wasu da portait ya lulluɓesu he can't say su waye su.

Sai kuma ɗayan ta ɗago fuskarta ta zazzaro idanunta kamar wadda ta yiwa sarki ƙarya.

He just smiled, tare da ƙurawa pictures ɗin idanu, wanda suka ma sa kyau sosai.

Reply ya ma sa da faɗin ''For.???" Emojis ɗin dariya Amir ya turo ma sa tare da faɗin ''Ka dawo ka kwashi gara my guy, ta dawo yadda kake so wallahi.''

Ganin message ɗin Amir ɗin ya sa wani kalar murmushi suɓuce ma sa tare da ma sa reply ɗin ''Really.?"

''Yeah.'' daga haka suka shiga wani hirar da ban.

Bayan sallar isha ma office ya koma ya duba wasu takardu tare da dawowa gida.

><><><><><><><><><><

Ko da suka shiga cikin falon da Mama Fatuh suka fara cin karo, suna zazzaune kamar ana sulhu.

Can dai suka saki jikinsu gaba ɗaya aka fara hira.

Ƙarfe goma na dare kowa ya watse, dan sai da suka ƙara wani faɗan da Yusrah, sannan ta kamo hanyar gida ita da Salimah.

Bayan Salimah ta buɗe gate, shigar da motar ta yi tare da ajiye shi a muhallinsa.

Ko ina na gidan shiru, direct backyard ta nufa tare da kunna wutan solar sannan suka shiga cikin gidan, da ko ina ya wadatu da haske.

Direct ɗakinta ta shige dan ba yunwa take ji ba, dan abincin gidan Mamin sosai ya yi ma ta rana.

Toilet ta shige tare da yin wanka ta fara shiryawa cikin kayan baccinta dan gobe ta na tunanin zuwa ganin Doctor.

Wayarta ne ya fara ringing hakan ya sanyata ƙarasa k'ulle towel ɗin jikinta tare da ɗaga wani number ƙasar waje da ba ta san code ɗinsa ba.

Har za ta ɗaga sannan wayar ta katse, in less than 5 seconds aka ƙara biyo kiran, a hankali ta ɗaga tare da manna wayar akunnenta.

''Assalamu alaikum.'' ta faɗa a sanyaye, amma ba'a ba ta amsa ba, ''Hello.'' ta ƙara magana ta na mai ɗauke wayar a kunnenta haɗe da mai da shi.

''With whose permission kike fita da mota, and da izinin wa kike fita, bayan school na yarje miki da kije?, kin fara wasa da ni ko.!?" HYDAR ɗin ya faɗa a ɗan faɗace.

Wani kalar bugawa ƙirjinta ya yi jin muryar na sa a cikin kunnenta, sannan kuma a hankali ta ce ''I'm sorry, Mami ce ba ta da lafiya, shiyasa nake fita, amma trust me wallahi babu inda nake zuwa bayan nan.'' ta ƙarasa maganar a sanyaye.

''Shi kuma kwanar badawan gidan ƙanwar ubanki ne acan.?" Wani iri ta ji a ranta da kalar amsar da ya bata, hakan ya sa ba ta amsa ma sa ba ta yi shiru.

''Ba magana nake miki ba?, kika min shiru.?" Ya yi maganar da ɗan zafi.

Cikin shashsheƙar kuka ta ce ''Yaya dan Allah ka yi haƙuri.'' ta yi maganar a sanyaye.

''Shut that your dirty mouth idan ina magana, ni sa'anki ne.?" Ya ƙara faɗa a tsawace.

Haushi faɗan da yake ma ta ya ba ta dan idan ta cigaba da sauraronsa za ta iya mayar ma sa da martani, hakan ya sanya ta kashe wayar haɗe da cilli da shi akan gado ta na mai fashewa da kuka.

Cikin shashsheƙar kuka ta ce ''Mai nayi wa kowa ya tsane ni, ni Fatimatu, mai nayi?, ba ga uwar da ta haifeni ba ba ga kowa ba, saboda zallar tsana da Neneh ta yi min ɗan bariki ta aura min, wanda ba ya daraja Mahaifina, why me??, why now?, why not later?, ya Rabbi I'm still young for all this, wayyo Allah na Aliyu zai min lahani, Allah ya ishewa mahaifina kalar cin mutuncin da kake yi ma sa, kai ma Billah sai an ma ka.'' ta ƙarashe maganar hawaye na fita daga idanunta.....

''Ya Ubangijina ka basu daman share."

Allah ya yiwa fans ɗina masu sharing arziki fiye da Dangote □□□

Ma ra sa share Allah ya kawo kuɗi na siyi mota na tada muku ƙura □□😂😂□

THE REGRET

PENDING AMARYA CE ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION

The Noble Writers Team.

Pending Amarya 49

What goes around comes around □ □

Every ending is a new beginning □□ even if the heart disagrees.□○□□

□ □ □

Not edited □□□

****

Cikin shashsheƙar kuka ta ce ''Mai nayi wa kowa ya tsane ni, ni Fatimatu, mai nayi?, ba ga uwar da ta haifeni ba ba ga kowa ba, saboda zallar tsana da Neneh ta yi min ɗan bariki ta aura min, wanda ba ya daraja Mahaifina, why me??, why now?, why not later?, ya Rabbi I'm still young for all this, wayyo Allah na Aliyu zai min lahani, Allah ya ishewa mahaifina kalar cin mutuncin da kake yi ma sa, kai ma Billah sai an ma ka.'' ta ƙarashe maganar hawaye na fita daga idanunta.....

Tun da ta yi cilli da wayarta take wani kalan kuka mai cin rai sannan kuma a hankali ta sanya kayan baccinta haɗe da yin kwanciyyarta.

Ko ta kan wayar ba ta ƙara bi ba wani kalar bacci ya kwasheta.

Washegarin ranar ma bayan ta gama abubuwan da ta saba ita da Salimah, shirye take cikin wani hijjabi mai kyau da tsada, wanda ya mugun dacewa da fatarta.

Fuskarta ya yi wani haske ya yi kyau sosai, hannunta riƙe da wayarta da car key ɗinta, ta matso tare da fara ƙoƙarin yin breakfast ɗin dake jere saman dinning.

Fresh milk kawai ta sha wanda Salimah ta dafa ma ta da Lipton da kuma kaninfari, sannan ta wuce tare da sanya Salimah buɗe ma ta gate ta fita daga gidan.

Sosai ta wataya a school ita da Lily sai da suka sha yawo, dan kalamansa na jiya sosai suka taɓa ma ta rai.

Ko da ta dawo gidanma su Ily da Reedah da Rashanda har da Unaisah duk suna cikin falon suna jiranta.

Hakan ya sanya ta farin ciki sosai suka ɗinga hira har sai da suka ja ta yau tayi post ɗin reel a Instagram, wanda acikin second talatin sai da ta samu almost 20k likes comments 1k ina ta shiga, sun daɗe ba su ganta ba(she finds her self again on social media, Dan hakan sosai ya sanyata farinciki).

After 2 months □□□

Zaune take fruits na cike taff a gabanta, jikinta na sanye da wani silky gown wanda ya kame ma ta jiki, har ya yi sanadin bayyanar da ɗan ƙaramin cikinta.

Salimah na gyara falon, ita kuma ta na shan fruits ɗin da take mugun jin daɗinsa.

Wayarta ne ya fara ringing hakan ya sanyata ɗagawa ganin Reeda ce ke kiran na ta, ''Hello Babe.'' Reedah ta faɗa a ta ɗayan ɓangaren.

''Yeah Babe, mai ya faru.?" Ta yi maganar a sanyaye.

''Nothing na kira ki ne mu ɗan gaisa.'' Okay dear I really appreciate.'' daga haka ta katse wayar, dan har ga Allah yanzu ta tsani magana mai nisa.

''Wai ke Salimah uban mai kike gogewa tun ɗazu a jikin TV ne, duk kin cika waje ke ba ƙiban arziƙi ba.'' Liyana ta faɗa a zafafe dan yanzu kowa ma haushinsa take ji.

Shiru kawai Salimah ta yi mata, dan yanzu wani kalar faɗa Liya ke tsiro ma ta da shi kamar jiƙar Bahubali.

Wayarta ne ya ƙara yin ringing na wani baƙon number da tun kusan mintuna goma da suka wuce yake ta faman kiranta.

A zafafe ya ɗaga wayar tare da karawa a kunne tare da faɗin ''Wayee?!." Ta yi maganar da zafi duk da zuciyarta na dukan uku uku.

Cikin muryarsa mai daɗin sauraro ya ce ''How dare you keep me waiting a airport tun ɗazu ina kiranki a waya?." Sassauta muryarta ta yi tare da faɗin ''Yi haƙuri ban san kai ne ba shiyasa.''

A tsawace ya ce ''Za ki zo ki ɗauke ni ne ko za ki tsaya haukan ki anan wajen.?"

Ba ta bashi amsa ba ta katse wayar tare da ɗauko wani dogon hijabi da ta dawo da shi daga hospital yanzu, sai safar hannu da na ƙafa tare da ɗaukan mukullin motarsa ta na ƙara jaddadawa Salimah ta ƙara gyaran gidan sosai.

Ikon Allah ne kaɗai ya kaita zuwa Airport ɗin, ta cikin mudubi ta hangesa, hakan ya sanyata parking motar na ta ɗan nesa da shi haɗe da saukowa daga cikin motar.

Tsaye yake hannunsa ɗaya a kunnensa wanda da alamu sun nuna waya yake, ɗayan hannun kuma dake ɗaure da agogon Rolex explorer ll na dafe da trollynsa.

A hankali ta sauko daga cikin motar iska na ɗan kaɗa hijabinta, ba tare da ta damu da hakan ba ta ci gaba da nufar wajen da yake.

Tun da ta nufo wajen da yake ya fara ƙafe idanunsa da ita, dan da tafiyarta ya gane saboda wani ƙiban da ta yi, walking slowly ta ƙaraso wajen da yake tare da faɗin ''Yaya, sannu da zuwa.'' ta yi maganar tare da sauke idanunta a ƙasa.

Ta yi kusan second biyar a hakan sannan ta ɗagoda kanta a hankali, a tunaninta ya na tsaye ya na kallonta, sai ta ga akasin hakan, because har ya nufi cikin motar , ya na zaune kujerar kusa da driver.

Wani kalar baƙin ciki ta haɗiya, har ƙwalla na niyyar zubo ma ta , gudun kar ya dizga ta a cikin jama'a ya sanyata ɗaukan trollyn da ya bar ma ta ta nufi bayan motar da shi.

Bayan ta saka trollyn ma wucewa ta yi ta zauna a driver sit ɗin motar tare da yiwa motar key ta na mai barin airport ɗin.

Acikin motar ma da dukkannin hankalinta take tuƙi gudun kar ta yi mistake da zai sanyata shan mari yadda ta ƙular da shi ɗin nan.

''By your left hand.'' ya yi maganar tare da ɗan mazewa, ba ta ma sa musu ba ta cigaba da jan motar.

Ƙara tsintar muryarsa ta yi ya na faɗin ''Kai ni wajen da ke da sugar daddies ɗinki kuke zuwa.'' ya ƙarasa maganar tare da mayar da kujerar motar baya domin ya ɗan fara hutawa.

Shiru ta yi domin ita har ga Allah ba ta taɓa fita da wani sugar daddies ba, parker motar ta yi tare da faɗin ''Yaya ina ne zamu je?, ban gane wajen sugar daddies ɗin ba.'' ta yi maganar innocently a ɗan marairaice tare da turo bakinta kaɗan.

Ƙurawa kyakkyawan lips ɗinta ido ya yi, sannan a hankali ya sa hannunsa haɗe da damƙo kanta ya fara ba ta wani kalar french kiss.

Ba tayi jayayya ba ta bashi haɗin kai acikin motar, jin ana musu wani kalar mahaukacin horn ne ya sanyata realising cewa akan titi ma ta yi parking motar.

A hankali ya saki bakin nata ba tare da yaso ba, ita ma sam ranta bai so ba, hakan ya sanyata tayar da motar tare da barin titin.

Wani kalar jaa idanunsa suka yi, murya a shaƙe ya ce ''Hydar's garden, right now.'' ya ƙarasa maganar ya na ɗauke kansa gefe, dan kallonta kwance ma sa lissafi yake.

Gudu take shararawa a titin a hankali ta na jin yadda kanta ke wani mugun sara ma ta, a hankali ta shiga cikin tamkeken gate ɗin da ya gaji da haɗuwa, tare da yin parking a wajen da ya dace ta yi.

Sauka ya yi a cikin motar, ita ma ta bi shi, ko ta kan reception bai bi ba ya danna wani kalar remote a hannunsa wanda hakan ya sanya glass ɗin wajen juyowa ya zama kamar ƙofa, shigewa ya yi ciki, ita ma ta bi shi, yanayin ginin kaɗai ya isheka ka san da cewa kuɗi sun zauna sosai.

Because ginin penthouse ne, looking very rich, ta cikin glass ɗin za ka iya ganin wanda yake waje, musamman yadda wajen yake idan ba ku manta ba.

Ta na tsaye ta na kallon kalar yadda gidan ya tsaru, taji mutum ya wani kalar ɗagata sama.

Ba ta musa ma sa ba ta ba sa haɗin kai, then they made love.

Wani kalar jinta yake a ransa, barin ma idan ya tuno kalar ɗawainiyyar da ta yi da mahaifiyyarsa, and then idan ya tuna a Virgin ya sameta, ya kan ji daɗi sosai.

A kwance take a jikinsa , he can feel the over heat da yake fita daga jikinta wanda shi kansa zafin jikin ya na affecting na sa, ga wani kalar surutai da take marasa kan gado.

''What's wrong with you.?'' ya yi maganar ya na mai shafa bayanta, ka sa magana ta yi wasu kalar hawaye na fita daga idanunta.

Jin saukar hawayen a kafaɗansa hakan ya sanya shi mirginota ta koma ƙasan sa tare da kallonta daga sama har ƙasa, cikinta ya ɗan taso ba kamar yadda ya kusanceta ba aranar farkon su.

Hannunsa ya sanya akan cikin nata tare da ɗan dannasa, saurin riƙe ma sa hannu ta yi cikin muryarta da ba ya fita ta ce ''Stop.'' ta yi maganar hawaye na sake gangarowa daga ƙuncinta.

''Mai yake damun ki wai ko kin fara hauka ne.?" Ya yi maganar ya na ƙara ƙafeta da ido.

Ƙanƙameshi ta yi da sauri ta na sauke wani kalar ajiyar zuciya, wanda hakan ya ƙara firgita tunaninsa.

''Ki yi wanka mu koma gida.'' still shiru ta yi ba ta ma sa magana ba.

''Liyana!." Ya kira sunanta da ɗan zafi.

Fashewa ta yi da kuka sannan a hankali ta ce ''Yaya, jini na zafi, cikin fata na zafi yake min.''

''Ya na miki hakan ne.?" Ya tambayeta ya na mai ƙafeta da idanunsa.

A sanyaye ta ce ''Just today.''

''Shirya muje hospital, can you dress up ko na taya ki.?"

''Your wish is my command sir.'' ta yi maganar da ƙyar.

Bayan sun shirya, direct nearest hospital suka nufa bayan sun fito daga ƙauyen, test aka yi ma ta, because it's emargency kuma Hydar ya sakar musu kuɗi, 7 hours aka basu kafin test ɗin ya fito.

7 hours suka yi a hospital ɗin, suna jiran sakamakon, Liyana ce kwance akan gadon emergency room, hannunta riƙe da cikinta kamar mai tsoron ka da wani abu ya samu abin da ke cikin nata. Hydar na tsaye hannunsa goye da bayansa yana ta safa da marwa, ya na kallonta a kai a kai.

Ƙarar buɗe ƙofan da ya ji ne ya ba shi daman juyowa da sauri, wa ta matashiyyar nurse ce ta shigo, ta kalli Hydar ɗin tare da faɗin ''Sir doctor is calling you for the results.''

Sai da ya kalli Liyana da kyau sannan ya matsa kusa da ita tare da shafa kanta ya fice daga room ɗin.

Lumshe idanunta ta yi hawaye masu zafi na gangarowa, sannan a hankali ta ƙara rufe idanunta kamar mai bacci.

><><><><><><><><><>

Doctor Lamil na zaune akan kujerar da aka tanada ma sa ya na duba takardun da sai confusing ɗinsa suke, kallon giant guy ɗin da ya shigo ya yi sai da suka ƙara gaisawa, sannan a hankali ya ce '' We found something unusual, the scan bayyana womb..... Amma ba mu ga fetus ba. The cavity is blocked by a mass, we can't figure out what's actually wrong with your wife Sir.'' ya ƙarashe maganar tare da kallon Hydar ɗin da idanunsa suka yi ja.

Sai da Hydar ya ja wani kalar numfashi sannan ya ce ''Mass kuma?, mai kuke nufi da Mass ɗin.?"

Sai da Doctor ɗin ya ɗan numfasa sannan ya ce ''Mass a nan na nufin wani abu ne da bai dace ba a cikin mahaifa, yana iya zama cyst, growth, ko wani abu da ke mamaye wuri. Mass na iya leading to Cancer, amma ba zamu iya tabbatar da hakan ba tukunna, Wannan shi yasa muke buƙatar ƙarin tests.'' doctor ɗin ya ƙarasa maganar ya na ƙara ƙafe Hydar da ido.

Wani kalar firgici ne ya ziyarci Hydar ɗin a lokaci ɗaya, cikin wani kalar murya wadda bai san kansa da shi ba ya ce ''Cancer fa ka ce Doctor.?" Ya yi maganar a ɗan ruɗe..... ''

''Love is blind.''😊

''Ya Ubangijina ka basu daman share."

Allah ya yiwa fans ɗina masu sharing arziki fiye da Dangote □□□

Ma ra sa share Allah ya kawo kuɗi na siyi mota na tada muku ƙura □□😂😂□

THE REGRET

PENDING AMARYA CE ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION

The Noble Writers Team.

Pending Amarya 50

What goes around comes around □ □

Every ending is a new beginning □□ even if the heart disagrees.□○□□

□ □ □

Not edited □□□

****

Wani kalar firgici ne ya ziyarci Hydar ɗin a lokaci ɗaya, cikin wani kalar murya wadda bai san kansa da shi ba ya ce ''Cancer fa ka ce Doctor.?" Ya yi maganar a ɗan ruɗe..... ''

''Bamu tabbatar ba tukunna.'' doctor ɗin ya faɗa tare da gyara eye glasses ɗinsa.

Wani kalar iska Hydar ɗin ya furzar haɗe da ficewa daga office ɗin, direct ɗakin da aka ajiye Liya ya nufa.

Ta na kwance yadda ya barta, ba ta canza position ɗin kwanciyarta ba, a hankali ya tako zuwa inda take tare da zare first aid ɗin da aka ba ta, ba ta da wani ƙarfin hana sa abin da ya yi niya, saɓa ta ya yi a hannunsa ya fice daga hospital ɗin ba tare da ya kalli Nurses ɗin dake ta ma sa magana ba.

A hankali yake driving har ya ƙaraso Babban hospital ɗin birnin Kano, wato Aminu Kano teaching hospital, dake ya san wani doctor a hospital ɗin saboda same school suka yi da shi, hakan ya sa akai saurin fara gwaje gwajen da ya dace a yi a kanta, tare da ba ta injection domin ta samu bacci, dan har ƙarfe sha biyun dare ya yi kuma babu wani ci gaba da aka samu.

Around 12:30am results ɗin suka fito, thesame with na wancan hospital ɗin, kuma abin mamaki wannan na nuna Cancer mai ƙonar da jini ya na yawo a jikinta, wani kalar tashin hankali Hydar ya shiga a wannan daren wanda bai taɓa ganin kalarsa ba.

Hannunsa ya kai jikinta ya ji wani mugun zafi fiye da na ɗazu, hakan ya sanya shi saurin janyewa tare da kallon kyakkyawar fuskarta da ya ɗan rame a lokaci ɗaya.

So yake ya kira iyayen su ya sanar da su amma he can't do that duba da yanayin daren da ya tsala.

Wayarsa dake jikin gadon da take kwance a kai ya ɗauka tare da duba notification ɗin telegram ɗinsa tun bayan da ya yi wa Amir reply lokacin da ta zo ɗaukansa.

Message ɗin Amir ya fara karantawa kamar haka ''Hey Man, barka da shigowa, hope ka huta sosai yadda ya dace, na je hotel na ka kuma ban gan ka ba, still naje gidanka Salimah ta ce min ba ku dawo ba, hope say you did nothing to that girl OOO.'' wani kalar jaa idanunsa suka yi tare da dannawa Amir ɗin kira.

Sai da ya yi ring huɗu sannan ya ɗaga, ''Assalamu alaikum, kai ba ka yi bacci ba za ka takura rayuwata ko.?" Amir ya yi maganar da magagi.

Hydar bai yi magana ba sai wani kalar ajiyar zuciya da yake saukewa, a can ɓangaren Amir wani kalar bugawa zuciyarsa ta yi, tare da faɗin ''Hydar hope babu abin da ka yiwa yarinyar nan.?"

Still bai yi magana ba ya yiwa Amir ɗin banza ya cigaba da ajiyar zuciyarsa.

''wai wannan wani kalar iskanci ne Hydar, ka yi min magana mana.''

Juyar da kansa Hydar ya yi tare da kallon Liyana da take numfashi da sauri da sauri, idanunta na saukar da wani hawaye mai zafi, jikinta na wani kalar kakkarwa.

Hakan ya sanya shi fashewa da wani kalar kuka tare da buga kujerar da yake kai ya ce ''Amir zan rasata, Amir mai sa sai na so Abu nake rasa shi?, why?, Wallahi Amir kai ma ka san kalar son da nake yi ma Liyana, please talk to her, tell her not to leave me, idan na rasa Liyana zan iya rasa raina.'' ya yi maganar ya na ƙara kallon yadda kakkarwan ke ƙaruwa kamar jijjiga.

Ganin hakan ne ya sanya shi kiran sunan doctor a ɗimanche, tare da cilli da wayar hannunsa ganin ta na ƙoƙarin faɗowa.

Sauri ya yi ya kama hannunta, ya ji tafin hannunta na wani kalar zafi, iska ya yi ta hura ma ta, dan shi ya rasa ma abin da ya dace ya yi.

.

Doctors biyu ne suka shigo haɗe da saka ma ta Oxygen, sannan suka ƙara ba shi ƙarfin gwiwa akan za ta rayu because za'a magance shi duk da cancer is not a curable disease.

Washegarin ranar da sassafe Amir ya kira Abbhu da Maami, sannan ya sanar da Umminsa duk abin da yake faruwa.

Kiran Hydar ɗin ya yi tare da tambayarsa hospital ɗin da suke wanda a take Hydar ɗin ya sanar da shi haɗe da kashe wayarsa ya ajiye shi a gefe ya na kallon yadda take kwance cikin kayan patients da kuma yadda a take ta yi wani kalar haske.

Doctor ɗin dake gaban sha'anin Liyanar ne ya shigo fuskarsa babu yabo babu fallasa, ya sanar da shi cewa suna da buƙatar jini.

Sai da ya kallesu sosai sannan ya ce wa doctorn da a ɗauki jininsa, bayan an yi gwaje-gwaje aka tabbatar jininsa na da cikakkiyar lafiya, sannan aka ɗauka.

Wayarsa ce ta fara ringing hakan ya sanya shi zira hannunsa a aljihunsa tare da ɗaukan wayar da number Mami yake bayyane a kai, sai da ya sauke ajiyar zuciya sannan a hankali ya ɗauka tare da kara wayar a kunne tare da faɗin ''Assalamu alaikum, Mami ina kwana.'' ya yi maganar a ɗan sanyaye.

''Ban kwana ba Aliyu, wannan ai iskanci ne, ta ya za'a ce daughter babu lafiya amma kuma ba zaka iya sanar da ni ba.?" Ta yi maganar a ɗan tsawace.

Sai da ya nisa sannan ya ce ''Ba na son na tayar wa da kowa hankali ne shiyasa ban faɗa muku ba, buh I'm sorry Mami.''

''A wani hospital kuke?."

''Malam Aminu Mami."

Katse wayar ya yi tare da kallon agogon dake ɗaure da tsintsiyar hannunsa.

><><>>••••••••••<><><

Zaune take a kan sallaya hannunta riɓe da carbi, idanunta na zubar da ƙwalla, cikin takunsa na mazan jiya da na yau, ya shigo ɗakin cikin shigarsa wanda ya dawo da su daga masallaci.

Ƙarasa shigowa cikin ɗakin ya yi tare da zama a edge ɗin gadon ya na kallon yadda ta ɗaga hannayenta ta na addu'a, hakan ya faranta ma sa ransa sosai.

A hankali ta tashi tare da kallon Nabil haɗe da faɗin ''Yaya ba ka kirata ba ɗin.?" Ta yi maganar ta na mai naɗe sallayarta.

Murmushinsa ya sakar ma ta mai kyau tare da faɗin ''Ina kwana Aunty Iki.'' waro idanunta ta yi tare da faɗin ''Yaya ina kwana.''

Janyota ya yi jikinsa sannan a sanyaye ya ce ''Liyana is a blessing in our lives, we all love her, ba zamu so wani abu mara kyau ya same ta ba, please Ikimat ki ƙara samun waje a zuciyarki ki yafe min, honestly our Liyana ta na fuskantar wani hali a wajen mijinta, please Ikimat.''

Muryarta na breaking kaɗan ta ce ''Yaya....., ka daina dawo da hannun agogo baya, komai mai wucewa ne, yanzu ƙuruciyyar mu ta wuce, tun da ba ta yi mana kyau ba, sai muyi ƙoƙarin sanya tsufar mu ta yi kyau, ana kawo ƙarshen komai domin fara sabon abu, and I can see changes right now, tun da daman Allah ba ya bacci Yaya, please ka bar komai ya wuce.'' Ammi ta ƙarashe maganar tare da kwantar da kanta a kafaɗunsa.

Wayarsa ce ta fara ringing hakan ya sa shi yin tsaki kaɗan tare da ɗaukan wayar, ganin sunan Jiddah da yake yawo ne ya sanya shi ɗaga wayar da ɗan hanzari.

''Assalamu alaikum, Sabahul khair ya Abbhi.'' Nabil ya faɗa a ladabce.

Cikin sassanyar murya Jiddah ya mayar ma sa martani da faɗin ''Wassalamu alaykum, Nabil duk inda kuke ku ƙaraso hospital ɗin Aminu Kano yanzun nan.'' ya na faɗan haka bai jira cewar Abbhi ba ya kashe wayar.

Tun da ya ɗaga wayar zuciyarta ke wani kalar bugu da sauri da sauri, hijab ɗinta kawai ta mayar sannan ta sanya Ilham kiran Rufaidhat.

Ba ta bi ta kan Ilham ɗin ba ta ja ƙofarta ta kulle ta cigaba da baccinta.

Ilham ita ma tsaki taja tare da wucewa wajen su Ammin sannan suka wuce zuwa hospital ɗin.

Isar su ke da wuya cikin ward ɗin da aka yi musu kwatance suka tarar da su Mami da Sultan da Abbhu, Amir da mahaifansa shi ma, sai kuma Neneh da Jiddah dake zaune a waje ɗaya, sai su kuma da suka ƙaraso yanzun.

Ko ina shiru, su sun rasa gabaɗaya wa za su tambaya, dubansu suka ƙara kaiwa wajen ƙofar wani ɗakin emergency wanda Hydar ke zaune idanunsa sun ɗan kumburo sun yi jaa.

Buɗe ƙofar room ɗin aka yi wasu doctor's suka fito su uku, cire facemask ɗinsa na farkon ya yi tare da faɗin ''We are sorry to say.....'' bai kai ga ƙarasawa ba Hydar ya yi saurin tashi tare da faɗin ''Ko da wasa kar ka kuskura ka faɗi kalmar da ba ta yi min ba anan.''

Ɗayan doctor ɗin ne ya ce ''Calm down Sir, give him a listening ears.''

''Okay continue.'' Hydar ya yi maganar tare da ƙafe doctor ɗin da ido.

''Gaskiya aikin yarinyar nan yafi ƙarfinmu, because jinin da aka saka ma ta ya ƙara ƙonewa, her condition is very very critical and cutar na nunawa ma ya daɗe a jikinta a yadda x ray ya nuna.'' ya na faɗan hakan shi da sauran colleagues ɗinsa suka bar su a corridor ɗin.

Tun da Ilham ta fuskanci da Liyana ake critical condition, ta zube a wajen sumammiyya.

A rikice aka yo kanta Neneh da abin ya ishe ta ta sanar a platform ɗin family house na su gabaɗaya ana buƙatar taron family duk nisan ka babu uzuri, a gobe ake buƙatar kowa.

Mami is Totally confused a yadda ake ta ambatar sunan Cancer tun shigowarta hospital ɗin, a hankali ta kama hannun Neneh tare da wucewa office ɗin Doctor Farouk.

Bayan sun shigo nuna musu sit ya yi da alamar su zauna.

A hankali Mami ta ce ''Doctor since nake ta jin kuna ambatar cancer tattare da daughter na, I hope this is a prank right?, because my daughter is pregnant, and you people are not even talking about the unborn child.''

Murmushi ya yi sosai sannan a hankali ya ce '' Maama, nothing like pregnancy a jikin yarinyar ki, akwai Mass ɗin da lulluɓe ma ta mahaifa, a yadda ruwayar wancan result ɗin ya bayar, kuma yanzu ya yi explode ya zama Cancer and every minutes jininta ƙara ƙonewa yake.'' Doctor Farouk ya gama musu bayanin tare da miƙa musu sauran test ɗin.

Da sauri Neneh ta amsa tare da faɗin ''Mass ka ce ko masa, meye haɗin shi da jikata da zai shiga jikinta idan ban da zalunci fisabilillahi.'' ta yi maganar ta na jan majina.....

Manage please □□

Mutuwa kan kawo canji

''Ya Ubangijina ka basu daman share."

Allah ya yiwa fans ɗina masu sharing arziki fiye da Dangote □□□

Ma ra sa share Allah ya kawo kuɗi na siyi mota na tada muku ƙura □□😂😂□

THE REGRET

PENDING AMARYA CE ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION

The Noble Writers Team.

Pending Amarya 51

What goes around comes around □ □

Every ending is a new beginning □□ even if the heart disagrees.□○□□

□ □ □

Not edited □□□

****

Da sauri Neneh ta amsa tare da faɗin ''Mass ka ce ko masa, meye haɗin shi da jikata da zai shiga jikinta idan ban da zalunci fisabilillahi.'' ta yi maganar ta na jan majina.....

Murmushi ya yi sosai sannan a hankali ya ce '' Maama, nothing like pregnancy a jikin yarinyar ki, akwai Mass ɗin da lulluɓe ma ta mahaifa, a yadda ruwayar wancan result ɗin ya bayar, kuma yanzu ya yi explode ya zama Cancer and every minutes jininta ƙara ƙonewa yake.'' Doctor Farouk ya gama musu bayanin tare da miƙa musu sauran test ɗin.

Da sauri Neneh ta amsa tare da faɗin ''Mass ka ce ko masa, mai haɗin shi da jikata da zai shiga jikinta idan banda zalunci fisabilillahi.'' ta yi maganar ta na jan majina.

Kauda zancen Nenehn Mami ta yi tare da amsan result ɗin ta na ɗan dubawa a hankali, sannan ta kama hannun Neneh suka fice daga office ɗin.

Ko da suka fito suna tsaitsaye cirko- cirko, Ilham ta farfaɗo, wucewa Mamin ta yi ta sami Abbhu akan maganar a fitar da Liyana ƙasar waje tun da likitocin duk sun nuna aikin ya yi ƙarfi da yawa.

Bai ƙi tata ba ya sami Jiddah da Abbhi ya wassafa musu komai.

A take suka yi na'am da zancen, anan take aka fara preparations ɗin tafiyar, duk wasu takardu na rashin lafiyar na ta sai da aka haɗa su as one documents.

Sannan Abbhi ya bada jininsa har leda biyu aka sa ma ta saboda ta samu wanda zai ɗan riƙe ta kafin a ta fi a goben.

Fashewa Ilham ta yi da kuka akan ita ma sai ta bi Liyanar, jiki ba ƙwari ta koma gida ita ma ta fara shirye-shiryen da ya dace.

Su Rashanda jikinsu duk a ruɗe bayan sun dawo daga lectures, kamar su yi kuka haka suka ɗinga ji, Unaisah kam sai da ta zo da yamma duba Liyanar da ba ta iya shaida duk wanda yake kanta.

><><><><><><>>

Hydar kam gwanin ban tausayi, ya rasa mai zai yi ya samu sauƙi musamman idan ya tuno ranar da ya sanyata wanke wanke kalar shirmen da ta ɗinga yi, wani kalar muryarta ya ji a cikin kunnenta ta na faɗin ''Yaya Alih please.'' wani kalar jaa idanunsa ya yi ya na ƙara hango yadda ta ɗinga rayuwa a gidan time ɗin da yake China.

''Aliyu.'' Mami ta kira sunansa a hankali tare da dafa gwiwar ƙafarsa, daman already sun riga sun shigo ɗakin da aka kwantar da Liyanar saboda sauran sun koma gida sanadiyyar dare yayi.

Ɗago kansa ya yi a hankali ya na ƙafe Mamin da jajayen idanuwansa, sannan a hankali ya furta ''Maa.'' tare da sauke idanunsa ƙasa.

''Aliyu are you not a Muslim?, ba ka yarda da ƙaddara ba?, ina ilimin ka yake?, tun jiya yaushe rabon da kayi wanka ko ka ci abinci na tabbatar tun jiya, please ka cire damuwar nan a ranka, addu'a ya kamata ka yi ma ta, have you prayed.?"

Bakinsa na ma sa nauyi ya ce ''Noo Maa.''

''And you genuinely wants her to be fine?, za ka tashi ka wuce gida ka yi abin da zai fishe ka ko dai na mareka a wajen nan.'' Mami ta yi maganar idanunta a kansa.

Jiki a sanyaye ya wuce parking space tare da wucewa gidansa ya na sassanar ƙamshin turarenta da bai bar motar ba.

Horn ya yi wanda Salimah dake bakin gate da hankalinta yake a tashe ta yi saurin buɗe gate ɗin da wani mugun gudu ya yi parking motar ta sa tare da wucewa cikin gidan.

Direct ɗakinta ta nufa inda ya tarar da shi komai tsaff, banɗakinta ya shige tare ɗaukan brush ɗin da ya tabbatar da cewa na ta ne ya yi brush da shi, tare da yin wanka da duk wani abu da take amfani da su, sannan ya ɗauro alwala ya fito daga cikin banɗakin.

Manta na shafawa ya shafa ajikinsa tare da shafa roll on ɗinta har ma da turarenta sannan ya wuce ɗakinsa ya sanya jallabiyarsa maroon color haɗe da haɗa wasu kaya a cikin trolly.

Sallolin da ake binsa ya gabatar tare da ƙara komawa hospital ɗin da har yanzu ta na yadda take babu wani canji.

Pepe soup mai zafi Mami ta zuba ma sa, shima sai da ta masa jan ido sannan ya ci, kamar zai yi kuka.

Har yanzu mamakin yadda cutar ta zo ma ta yake, daga intercourse kuma sai Cancer, anya ba sa hannu a lamarin nan kuwa.

Washegari kuwa da sassafe suka wuce ta private jet ɗin Abbhu wanda direct a Germany za su sauka saboda suna da high quality cancer treatment and care.

Yanayin ginin hospital ɗin kaɗai zai tabbatar ma ka da cewa ba ƙaramin hospital bane, dake Abbhu ya sanar da zuwan su hakan ya sanya suna zuwa doctor Marcus ya sa aka shigar da ita wasu machines na gwaje gwajen da ya dace ace an yi ma ta dan duk wani takardun Nigeria watsar da su suka yi a gefe aka fara sabon bincike akan Liyana.

After the test results □☹□□

Gabaɗaya test ɗin Abu ɗaya yake nunawa, amma wannan ya banbanta da sauran,dan wannan na tabbatar da cewa ba lallai ta ƙara jimawa ba a duniya duk da basu san yadda ta Allah za ta kasance ba.

Ilham, Hydar, Mami, gabaɗayansu sun shiga tashin hankali mara misaltuwa, barimma Hydar da gabaɗaya ya kusa fin Liyanar shiga wani hali, shi idan ma mutuwan za ta yi ta taimaka ta yafe mi shi , da abin zai fi ma sa sauƙi a rayuwar shi.

Haka rayuwar Liyana ta ci gaba a DKFZ dake a ƙasar Germany gwanin ban tausayi, sam rayuwarta a kwance take yin sa sannan Oxygen a hancinta, sai wani abu da aka sanya mata shi a hannunta wanda kamar supporting numfashinta shi ma yake.

Zaune suke a cikin VIP room ɗin da yake su kaɗai, sai Liyana dake kwance samɓal a kan gadon ɗakin tamkar ba za ta yi motsi ba.

Ilham na zaune kusa da Mami kanta a kan cinyar Mamin da take shafa ma ta kai haɗe da daɗaɗan kalamai wanda ke ƙara sanya zuciyarta cikin positive taughts game da rashin lafiyar yayarta.

Hydar shi kam ya na zaune wajen gefen Liyana kansa a ƙasa ya na kallon wayarsa wanda dukkanin alamu sun nuna kamar hoton Liyana ne, time ɗin da take ji da kanta.

Ɗago kansa ya yi daga kallon videon da ta yi shi ita da Ily a wani babban restaurant jikinta sanye da palazzo trousers fari sai wani top shi ma fari, sai wani faux fur v neck jacket shi ma fari, sai wani heels da ta saka black da jersey veil black color ya yi ma ta mugun kyau, sai wani sun shade da ta ɗaura akan black veil ɗin.

Hannunta riƙe da wani ice cream a wani ice cream disposal container mai kyau.

Ɗayan videon kuma a lokacin suna yara da ita da Ily da Ammi har Abbhin a Saudi Arabi, fuskarta sanye da glasses masu kyau, a ƙasan picture ɗin ta rubuta ''Family over everything □ □.''

Wasu kalar hawaye ne suka zuba a idanunsa, ya yi sauri ya share su tare da ajiye wayar ya ɗan jinginar da kansa kaɗan.

Ƙarar heart monitor dake control numfashinta ne ya fara karaɗe ɗakin irin na cewa mutum na gargarar mutuwa, a firgice ya taso inda har su Mami sun danna bell ɗin kiran doctor, wani kalar ƙara ya ɗinga yi mai mugun ƙarfi, wanda hakan ya sanya doctor's mayar da su waje suka duƙufa wajen ceto rayuwarta.

Ɗiff gaba ɗaya na'urar ta kawo flat line without any zigzag, ma'ana zuciyarta ya daina bugawa, wani kalar hawaye mai zafi ya zubo a kuncin Liyanar.

Sannan ta ja wani dogon numfashi haɗe da wani kalar zabura daga gadon sannan ta koma da ƙarfi, da hanzari doctors ɗin suka fara danna ma ta ƙirji amma kuma Liyana is unresponsive,, Sam ba ta ba da wani alamar ta na da sauran numfashi.

Doctor Samson ne ya naushi bango da hannunsa tare da furzar da wani iska daga cikin bakinsa sannan a hankali ya ce ''Guys we have lost her.....''

Manage please □□

Mutuwa kan kawo canji

''Ya Ubangijina ka basu daman share."

Allah ya yiwa fans ɗina masu sharing arziki fiye da Dangote □□□

Ma ra sa share Allah ya kawo kuɗi na siyi mota na tada muku ƙura □□😂😂□

THE REGRET

PENDING AMARYA CE ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION

The Noble Writers Team.

Pending Amarya 52

What goes around comes around □ □

Every ending is a new beginning □□ even if the heart disagrees.□○□□

□ □ □

Not edited □□□

****

Doctor Samson ne ya naushi bango da hannunsa tare da furzar da wani iska daga cikin bakinsa sannan a hankali ya ce ''Guys we have lost her.....''

Ƙara kallon gawar Liyanar dake kwance samɓal suka ƙara yi, wanda hakan ya ƙara tabbatar musu da cewa mutuwa ta yi.

A hankali Marcus ya zame daga cikin room ɗin tare da nufar ƙofar wajen da su Hydar ke tsaitsaye cirko- cirko, Ilham na jikin Mami yayin da shi ke tsaye a bakin ƙofar kamar wanda ke jiran sallahu.

Jin ƙarar buɗe ƙofar ya sanya shi saurin shan gaban Marcus tare da tsastsare shi da manyan idanunsa, face mask ɗinsa Marcus ya cire tare da sauke wani ajiyar zuciya sannan a hankali ya ƙara kai dubansa wajen Hydar ɗin tare da faɗin ''Sorry to say, I know how you feel bro, buh we have lost your wife.'' ya na maganar ya wuce Hydar ɗin.

Saurin dawo da shi baya Hydar ɗin ya yi muryarsa na breaking ya ce ''I..... Don't gerr you well, ban gane abin da kake nufi ba.'' ya yi maganar idanunsa na kawo ruwa.

Shi kansa Doctor Aliyu tausayi ya ba sa, bai iya yiwa Aliyun magana ba ya zare hannunsa tare da kallon Mami da ita ma wasu kalar hawaye sun fara kawo ziyara idanunta.

Ilham kuwa shock ne ya sameta ta nemi hawayenta ta rasa ga wani zafi da zuciyarta yake ma ta.

Zubewa ya yi a wajen ya na girgiza kansa ya na wani kalar kuka kamar mace, tare da faɗin ''Noo, Fatimah not now, ba yanzu da zuciyata ta aminta da ke ba.''

Ya yi maganar a zauce tare da fito da wayarsa ya na dailing number Amir.

Ring ɗaya kamar Amir jiransa yake ya ɗaga tare da faɗin ''Aliyu ta tashi?,'' bai kai ga yin wata magana ba Ammi ta amshi wayar daga hannunsa tare da faɗin ''Aliyu

ka bawa Liyana wayar na yi ma ta magana.'' ta yi maganar itama hawaye na fita a idanunta, dake gaba ɗaya family ɗin kowa ya hallara.

Kukan Ammi da na Mami da yake ji ke ƙara sanya zuciyarsa zafi, da wani kalar murya mai ɗan kauri ya ce ''Liyana is gone Ammi Matana ta mutu.'' ya na faɗin hakan ya saki wayar a wajen tare da jinginar da kanshi a bango ya ci gaba da kukansa.

><><><><><><><

Can Nigeria kam tun bayan tafiyarsu Hydar ɗin kullum cikin sadaka ake, ba ka taɓa ganin gidan Neneh babu jama'a.

Kamar yadda gidan ya saba gaba ɗaya family ɗin shuwa arabi ne a gidan,wasu na addu'a wasu na hira, har da su Abbuh da Sultan da Amir da iyayensa dukkanin su suna gidan Neneh.

Ganin wayar Amir na Ring ne ya sanya shi saurin ɗagawa saboda ganin sunan Hydar ɗin.

Ya na fara magana Ammi ta amshe wayar wanda daga ƙarshe sai sumanta suka gani a ƙasa, da sauri aka ɗagata saboda su Abbhun da manyan duk sun fita kai sadaka gidan marayu.

Already daman wayar a handsfree yake, hakan ya sanya su jin muryar Hydar ɗin ya na faɗin ''Ammi matana ta mutu.''

Gaba ɗaya falon aka saki salati da salallami banda Mama Fatuh da jikinta ya yi sanyi har ya fara kakkarwa.

Take bowl ɗin wata melon dake hannunta ya faɗi a ƙasa tare da tarwatsewa ta na mai faɗin ''Innalillahi wa inna ilaihir rajiun, Ni Fatuh, Liyana ce ta mutu.'' ta yi maganar muryarta na dashewa a lokaci ɗaya tare da yin wajen gidan ta fice daga gidan gabaɗaya.

Kowa na wajen ya sha jinin jikinsa barin ma yadda Ammin ke zubda hawayenta, Umma Mansura ita kanta ta rasa ya zata yi.

><><><><><><><

Kamar wani abu ya mintsine shi ya yi saurin buɗe ɗakin dai-dai time ɗin da ake haɗa mortuary injection, domin kar gawar ta lalace.

Cikin muryarsa mai amo ya ce ''Don't you dare lay your hands on my wife, she's not dead.'' ya na faɗin hakan ya ƙaraso wajen Gawar Liyana tare da ɗaukan ta a hannu kamar baby, ta yi masa nauyi sannan kuma ta ɗan sake.

Fitowa ya yi da ita daga ɗakin inda ya tarar da Mamin a corridor jikinta riƙe da Ilham, Ilham da ta kasa kuka ta na ganin Liyanar kawai ta wani irin fashewa tayi da kuka ta na ƙara ƙanƙame Mamin a jikinta.

Authority ɗin hospital ɗin suka hana shi fita da gawar akan sai sun ƙara tests da wasu binciken, amma sam Hydar yaƙi yarda akan shi a basa matarsa ya fasa maganin, sai da Mami ta kusan kai masa duka sannan ya ajiye Liya a kan gadon patients aka nufi X-ray da ita.

After 2 hours.

Result ya fitar da komai na ta lafiya, cikin jikinta shi ma ya na nan cikin ƙoshin lafiya amma babu numfashi a tattare da ita.

Abin ya mugun ɗaurewa doctors ɗin kai, amma ba su iya nunawa su Mamin result ɗin ba suka basu gawar Liyanar domin tafiya da ita gida Nigeria.

A cikin jet ɗin ma hannunsa na riƙe da na ta idanunsa na fidda hawaye.

After 7 hours.

Direct airport jet ɗin ya sauka, wanda har su Amir da Sultan sun zo ɗaukarsu dan har ƙarfe tara na dare ya yi, hannunsa riƙe da ita aka gangaro da gadon patients zuwa wajen da yake dan har da ambulance a masu ɗaukan su.

Bayan an sanyata a motar sai da yabi ganyen dake jikin motar gabaɗaya ya ciccizge sannan ya shiga bayan ambulance ɗin shi ma ya na riƙe da hannunta tare da ɗora kansa akan kan Liyanar.

Hawaye na ɗiga a idanunsa zuwa kumatunta.

Har suka ƙaraso cikin gidan bai san an ƙaraso ba sai da aka buɗe ambulance ɗin.

Abbhi ne tsaye da jallabiyarsa shi da Jiddah da Abbhu.

Abbhi idanunsa ya yi jaa, he can't even talk sai hawayen da yake zubarwa, kama gadon ma aikatan ambulance ɗin suka yi tare da yin entrance ɗin gidan Nenehn da ita.

Gidan cike yake maƙil da mutane har da bloggers, ''Ƴar gidan Abbhi is dead.'' ya'n school ɗinsu da exes ɗinta gaba ɗaya duk suna jiran gawar da sai gobe da safe za'a kaita.

Classy Reeda da Sandy Rash da sauransu are all crying, sun rasa ma ya zasu yi kowa sai posting pictures ɗinta yake Ya'r gidan Abbhi ta rasu, Liyana bae is dead.

Ko ina a yanzu ya amsa mutuwar Liyana.

A falo aka shinfiɗeta bayan kulle ƙofar ɗakin iya love ones ɗinta ne a falon, a hankali Abbhi ya rarrafo idanunsa na zubda hawaye tare da faɗin ''Ya'r Abbhinta why?, mai sa za ki tafi ki bar Abbhinki,? Where are the promises?, First fruit wake up na san you're pranking me.'' Abbhin ya yi maganar tare da riƙo hannunta ya na karawa a hancinsa.

''Yaya dan Allah kayi haƙuri ka daina kukan nan.'' Umma Mansura ta faɗa hawaye na sauka daga idanunta itama tare da ɗan jan Abbhin daga kusa da gawar Liyanar.

Neneh kam sai gwale ido take ta kasa kuka sannan ta kasa dariya, duk ilaihirn falon na cike da ya'n uwanta amma banda Mama Fatuh da Rufaidhat, dan har Yusrah kuka take na rashin Liyanar.

Hydar na can gefe Amir na rungume da shi, yayin da Sultan ke shafa bayansa shi ma duk ransa babu daɗi.

Ɗaki ɗaya aka ware ma Liyanar inda za'a ajiye gawan na ta a kwana da shi, da Neneh da Umma Mansura sai Ilham da Unaisah su kaɗai aka ware da zasu kwana da ita.

Ganin duk mutanen falon na ta preparations na binne Liyar da safiyar ranar ya sanya shi barin wajen su Amir tare da nufar ɗakin gawar na ta.

Auduga na toshe da hancinta da kunnenta ya iso wajen da take wanda Ilham ce ke kusa da ita, matsa ma sa Ilham ɗin ta yi tare da komawa bayan su da kaɗan.

Mami ce ta fara yi ma sa alamar ya fita da hannu ganin kukan da yake amma ya yi mata biris tare da ɗauke kansa.

''Hey sweet heart, duk ranar da na mutu, don't cry dan Allah,secondly idan ina da aure a lokacin after 40 days ki auri mijina, thirdly, kin san dai suratul mulk is my favorite surah, and Sheik ya ce ya na sanya sassauci ga mamaci, try to read that surah for me, to cut it short I will miss you guys.'' Liyana ta ƙarashe maganar tare da yin ƙwai da chewing gum ɗin bakinta.

''Yaya da wani talk, TOH yanzu mai ya kawo zancan mutuwa?, ko santin chewing gum ɗinne har haka.?" Ilham ta faɗa ta na ƙarasa saka hular baccinta.

''Ke wasiya nake ba ki, sannan ki kula da yarana abeg.'' ta yi maganar ta na ɗaga video call ɗin Sultan.

''Toh ni ki daina min kalar wannan wasiyar ba na so.'' daga haka Ily ta yi kwanciyyarta akan gadonta hawaye na zubo ma ta.

Firgigit ta dawo daga tunanin jin an dafa ta amma still muryar Liyanar take ji ta na faɗin ''Ily I'm stuck in this pot, please hurry up, ILY save me, kar ki barsu su kai ni ƙasa lokacina ya kusa.''

A zabure Ily ta tashi tare da ɗauko Al- K'ur'ani mai girma cikin muryarta mai daɗi ta fara karanta Suratul mulk.....

Manage please □□

Mutuwa kan kawo canji

''Ya Ubangijina ka basu daman share."

Allah ya yiwa fans ɗina masu sharing arziki fiye da Dangote □□□

Ma ra sa share Allah ya kawo kuɗi na siyi mota na tada muku ƙura □□😂😂□

THE REGRET

PENDING AMARYA CE ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION

The Noble Writers Team.

Pending Amarya 52 countinuation.

What goes around comes around □ □

Every ending is a new beginning □□ even if the heart disagrees.□○□□

□ □ □

Not edited □□□

****

Firgigit ta dawo daga tunanin jin an dafa ta amma still muryar Liyanar take ji ta na faɗin ''Ily I'm stuck in this pot, please hurry up, ILY save me, kar ki barsu su kai ni ƙasa lokacina ya kusa.''

A zabure Ily ta tashi tare da ɗauko Al- K'ur'ani mai girma cikin muryarta mai daɗi ta fara karanta Suratul mulk.....

><><><><><><><><

Tun fitar Mama Fatuh ba ta zame ko ina ba sai ɗan ɗishe, gidan Malam Barbushe, sosai ta firgita ainun da abin da ke faruwa da Liyana, idanunta sun yi jaa kamar zasu firfito saboda firgici, number Rufaidhat take ta dailing wanda MTN suke ta nuna ma ta network busy.

''Innalillahi wa inna ilaihir rajiun, Ni Fatuh mai na aikata hakan, Ni sam ban so a kashe ki ba Liyana, ban taɓa tsammanin hakan za ta faru ba, duk tsubbu na ban taɓa kisa ba, sannan na rasa wa zan kashe sai ya'r ƙanwata, Noooo ba zai yiwu ba.'' ta ƙarashe maganar tare da dukan stiring motar ta ƙirar 206 hawaye na zuba a idanunta a daidai lokacin da ta shawo kwanar gidan Malam Barbushe.

Parker motarta ta yi wanda tun a bakin ƙofar gidan ta fara cin karo da motar Rufaidhat, kutsa kanta ta yi cikin shagon dake ƙofar wani gida, inda candles ke kunne berekete sai turarukan aljanu da babu adadi ke jere reras a kan wani ɗan tebur, sai tulu ƙananu dake ɗaure da jan ƙellaye suma da ɗan yawan su, face wani guda ɗaya dake ware akan wani abu mai kama da mangal amma babu wuta a ƙarƙashin sa.

Wani ɗanyan ƙwai ne a hannun Malam Barbushe jikin ƙwan sanye da wani ƙyalle sai wani ɗan rami dake kusa da shi wanda alamu sun nuna kamar ƙwan yake ƙoƙarin sakawa aciki.

Cikin muryarsa mai amo ya ce ''Daga zarar na saka wannan ƙwan a cikin wannan ramin, Fatima ba zata ƙara rayuwa ba sai dai na bayan mutuwa, kin tabbatar a aikata tun da na ɗauko ruhinta daga tulun nan.'' Malamin dake sanye da wani shegen kwalli ya yi maganar ya na kafa Rufaidhat da ido.

''Malam ni kayi abin da ya dace akan yarinyar nan, bayan komai ya lafa zan dawo a naɗe min ita ma ƙanwarta, ita kuma mahaifiyyarta abin da aka saba za'a ci gaba, dan yanzu ita ce da gidan, amma ni a yanzu idan akwai gaba da mutuwa toh a shirye nake ka aika min Liyana tun da ita ma wadda ta fara kawo shawarar ita ma ta ce ko mai ya dace ayi ta bani wuƙa da nama, kai ma kuma bayan kuɗi akwai ɗayan ihsanin.'' ta ƙarashe maganar tare da kanne ido da kuma lashe leɓenta duk a lokaci ɗaya.

''Ba ki isa ba shegiyya algunguma ya'ta za ki kashe, Malam kar ka saki ka kashe Fatima, saboda babu wani laifi da ta yi, ni ban san kashe ta zata yi ba.'' ta yi maganar tare da fashewa da kuka tana mai durƙushewa a wajen.

Kallon mamaki Malam Barbushe ya tsaya yiwa Mama Fatuhn sannan kuma a hankali ya ce ''Idan za ki iya bawa aljanu kanki su kwana dake na sati ɗaya, a shirye nake da na fasa abin da nake shirin aikatawa.'' Malam Barbushe ya faɗa tare da ƙafe Mama Fatuh da ido.

Cikin sauri ta ce ita ta yarda ko da wata ɗaya zasu yi da ita, ita dai ba zata so a kashe wani ba, da ace kurciyya ne ta saba yiwa ya'ya'n mijinta.

''Toh haka ake so, ku ci gaba da tsula tsiyarku mutuwa ba yanzu ba ya'ya'n sheɗan'' haka ya yi ta yiwa mata kirari tare da kiran jinnuh kala kala sannan ya fara magana cikin wani kalar yare.

Bayan mintuna biyar ya fara warware ƙyallen dake jikin ƙwan, sannan ya rufe ramin da yake a buɗe, bayan ƙyallen ma da akwai wani baƙin zare da jan zare dake tattare da jikin ƙwan, duk sai da yabi ya warware tare da wanke ƙwan acikin wani ruwa saboda wasu rubutu da suke jiki, na kulle ruhin Liyanar wani Ya'r tsana ya ƙara zarowa daga bayan sa tare da fara ciccizge allurorin dake jikinta sannan ya zare pad lock ɗin da aka kulle ya'r tsanar da shi.

''Yawwa an gama abin da ya dace, amma wani hanzari ba gudu ba, idan fa kika kwanta da aljanu babu ke babu haihuwa.'' ya na faɗin haka ya ci gaba da iza wutan sa akan wani allon ƙarfe ya na ɗiga wasu turaruka, wanda ke nufin auran wasu yake shirin farraƙawa. (Allah ka mana tsari da tsarewarka 😭).

" Malam ban gane babu haihuwa ga wanda ya kwanta da aljanu ba.?" Inji cewar Rufy ta na zaro idanunta.

''Eh mana ko kin taɓa ganin kin yi ɓari tun lokacin da kika zo ɗaukar fansar ɗiyar ki da aka kashe, kin san dai ba na son ja in ja, ku ɓace min a wuri ko na mayar muku da cututtukan da na ciro dan kutumar ubanku, in banda ƙarfin Kur'ani da kuma tausayin yarinyar nan wa ya ce muku zan sake ta haka kawai, yanzu ana can ana ƙona Aljani Gujungu, ma za ku tafi kar ɓacin rai ya shafe ku Dan uban Babanku, shegu dangin iblis.'' Malam Barbushe ya yi maganar ya na wani kalar fari da idanunsa.

Da sauri suka fita daga shagon Rufaidhat na zagin Mama Fatuh ta na faɗin ''Wallahi Fatuh nima kin san wacece ni tun lokacin da nake soyayya da Nabil, kin san banda

hali, kuma a juri zuwa rafi watarana sai na fasa komai wallahi.'' Rufaidhat ta faɗa ta na dallawa Mama Fatuh harara haɗe da dungure ma ta kai.

''Wallahi Rufaidhat kema kin san duk kilakancin ki sai dai ki biyo Fatuh, babu record ɗinmu da ban da su, dan haka ki bi ni à hankali, ko an gaya miki ban san ke kika kashe iyayenki ba, ko an gaya miki ban san wace uwarki ba Asabe Karuwar ya'n garuwa.'' Mama Fatuhn ta faɗa tare da shigewa cikin motar ta ita ma.

Wani hawaye ne ya silale ma Rufy, sannan a hankali ta shige cikin motar ta ita ma ta bar wajen jiki a saɓule.

><><><><><><><><

Tun da aka fara karatun take jin wani kalar Abu na sakin jikinta ji take kamar inda ta maƙale an sakar ma ta ƙofa ta fice daga wajen.

Motsa hannunta ta yi kaɗan tare da ɗan damƙe hannunsa jin kamar ana zare wasu abubuwan da aka daɗe da ajiyar su ajikinta.

Jin kamar an damƙe hannunsa ya sanya shi ɗago kansa a firgice tare da amsar Alkur'anin hannun Ilham ya fara karanta Suratul Baƙara da daddaɗan muryarsa mai sanya zuciya sanyi.

Ya yi kusan minti talatin ya na karatun sannan yaji ta yi wani kalar attishawa tare da buɗe idanunta, a firgice ya ɗago kansa sannan kuma a hankali ya ci gaba da karatun hawaye na sauka daga idanunsa.

Hannunta ta sanya a hancinta tare da zaro duk wani auduga cikin hancinta, banda Aliyu dake ɗakin kowannensu a tsure yake barimma Neneh da take ƙoƙarin jike jikinta da fitsarin da ya taho ma ta .

Sai da tayi attishawa sau uku sannan ta fara miƙewa a hankali, tsabar murna Aliyu bai san lokacin da ya ajiye Alkur'anin hannunsa ba ya rungume Ilham da har ta kusa suma tsabar firgici ba.

Da sauri ya saki Ilham tare da rungume Liyanar da kanta ke wani kalar sara ma ta.

Ita ma ƙanƙame shi ta yi jikinta na wani kalar rawa, sannan a hankali ta ce ''Yaya mai yake faruwa?, Neneh yaushe kika z.....'' ai ba ta ƙarasa maganar ba Nenehn ta arce da wani gudu kamar ba tsohuwa ba, ita ma Ily ta mara ma ta baya.

Mutanen falon na zazzaune suna ɗan hawaye da jimami suka ga afkowar Neneh da Ilham cikin falon.

Tambayar su ake mai ya faru amma sam ko wannensu ya kasa faɗar komai, da wani kalar acceleration Mami da Reedah suka fito daga ɗakin.

Hakan ya sanya sauran mutanen falon tsorata, Ammi da Abbhi ne suka fito daga cikin ɗakin Liyana jin ana ihu a cikin falon.

Hydar ne riƙe da Liyana suka fito har cikin falon, jikin Ammi na ɓari ta nufo wajen da Liyanar da ke tsaye fuskarta ya yi wani kalar fayau.

''Iki nah ina za ki je?." Nabil ya yi maganar tare da janyota jikinsa.

''Yaya Liyana nake gani ga ta can, dan Allah ka bar ni na ji ɗimin ya'ta.''

Shi sai a lokacin ya lura da Liyanar dake tsaye jikin Hydar ta na bin mutanen falon da ido.

Jiddah da Abbhu da Abbahn Amir da shi Amir da Sultan ne suka shigo cikin gidan daga amso makara da kuma linkafani, jin ihu, hakan ya sanya su hanzartawa kar a zo matan ne ke kururuwa akan gawar Liyanar.

Da sassarfa suka shigo cikin falon a daidai lokacin da Mami ta taɓa kafaɗar Liyanar tare da rungumeta tsam ajikinta, cikin shashsheƙar kuka Mamin ta ce ''Welcome back to life daughter.''

Ita dai Liyana bin kowa take da kallo kamar wawiya, haɗa idanunta da Sultan da Amir shi ya ƙara razana gidan, dan sosai Sultan mugun matsoraci ne.

Dan bai san lokacin da ya ɗane Amir ba shi ma kuma Amir ya na neman ta yadda zai cillar da Sultan ya yi waje.....□□□😂😂😂

Mu haɗe on Monday

Manage please □□

Mutuwa kan kawo canji

''Ya Ubangijina ka basu daman share."

Allah ya yiwa fans ɗina masu sharing arziki fiye da Dangote □□□

Ma ra sa share Allah ya kawo kuɗi na siyi mota na tada muku ƙura □□😂😂□

THE REGRET

PENDING AMARYA CE ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION

The Noble Writers Team.

Pending Amarya 53.

What goes around comes around □ □

Every ending is a new beginning □□ even if the heart disagrees.□○□□

□ □ □

Not edited □□□

****

Da sassarfa suka shigo cikin falon a daidai lokacin da Mami ta taɓa kafaɗar Liyanar tare da rungumeta tsam ajikinta, cikin shashsheƙar kuka Mamin ta ce ''Welcome back to life daughter.''

Ita dai Liyana bin kowa take da kallo kamar wawiya, haɗa idanunta da Sultan da Amir shi ya ƙara razana gidan, dan sosai Sultan mugun matsoraci ne.

Dan bai san lokacin da ya ɗane Amir ba shi ma kuma Amir ya na neman ta yadda zai cillar da Sultan ya yi waje.....□□□😂😂😂

Ita kanta Liyanar tsoron kanta take, a hankali Jiddah ya ƙaraso wajen da take tare da faɗin ''Ya Zahra, kina raye, Alhamdulillah.'' sannan ya kamo hannunta daga cikin na Mamin ya zaunar da ita a kan cushion ɗin dake falon.

Har su Sultan na niyyar ficewa daga cikin falon Jiddah ya ce da su su dawo.

Duk sanyin Acn falon sai da gumi ya keto ma Sultan da Amir, sannan suka zauna a hankali nesa da Liyanar da kuma shi kansa Hydar ɗin.

Neneh kam sam ta kasa zaune ta kasa tsaye kawai jira take taji tak ta fara ta kanta.

Ily da Reedah da sauran ya'mmatan na zazzaune amma ba kusa da su Jiddahn ba, a hankali Jiddah ya fara magana tare da faɗin ''Ba abin gudu bane dan min kalleta ta tashi, ina ilmin ku yake?, da za kuyi ta yin ihu a cikin dare kamar wasu ya'n karkara, wannan sam ba dacewa ba ce, ai abin farinciki ne ace wadda muke kukan kewarta ta dawo cikin ƙoshin lafiya, kuma duk wanda ya yiwa Zahra Mummunan abu zai koma kansa da yardar Allah, kowa ya nemi waje ya kwanta.'' Jiddahn ya idasa maganar tare da ɗaukan walking stick ɗinsa.

''Ni dai a wurin mu da safe ake wannan, wa zai nemi wuri ya kwanta a gidan nan, salon na ga wannan al'amarin a kaina ta na ƙoƙarin ja na mu tafi, nifa daman ta sha faɗa min ko ta mutu sai ta dawo ta ɗaukeni mun tafi tare, TOH maganar gaskiya ba da ni za'a yi kwanan gidan nan ba Rafiƙ, yawwa.'' Neneh ta ƙarashe maganar ta na satan kallon Liyana da ta ma ta ƙuriii da ido.

''Ajiddeh ba na magana biyu maza ku nemi waje ku kwanta wa'yanda zasu koma gidajensu kuma suyi saurin tafiya kafin ƙarfe 12 ta yi.'' daga haka ya wuce stairs.

Hydar ne ya ƙaraso wajen da Liyanar take tare da miƙa ma ta hannu, ganin yadda mutanen wajen ke ɗan tsoranta sai shi kaɗai da Maminsa hakan ya sanyata miƙa ma sa hannunta tare da manne ma sa ajiki.

Har wajen Ammi ya ƙarasa da ita, wanda a take Ammin ta rungumeta ta na wani kalar kuka mai tsuma zuciyar mai sauraro.

Da ƙyar ta saketa, ita dai Liyana sai ganin yadda Hydar ke fasin fasina da ita kawai yake, har wajen su Abbuh da Abbha duk sai da taje sannan suka nufo wajen Neneh, wanda in less than two seconds ta fara ƙoƙarin hayewa sama.

Reedah kam a daren nan sai da ta saki reel a Instagram da Video ɗin Liya da Hydar ɗin ta rubuta ''Alhamdulillah, she's still alive.''

Daman mutane jiran updates suke, haka Fans ɗin Liya da na Reedahn sukai ta hamdala, kowa na farincikin ganin Liyanar na hugging mutane.

After 2 days.

Da sassafe Hydar ya tashi dake a gidansu ya kwana Amir dake nace ma ɗakinsa idan zai kwana a gidansu yau kam a ɗakin Sultan ya kwana.

Duk wannan badaƙalar da aka yi sai jiya Assultanah ta ga news ɗin mutuwar Liyana na yawo a social media ba ta wani jira ba ta kama hanyar jirgi ta dawo gida ta na wani kalan kuka, ita ma Lily sai a lokacin ta ga news ɗin a Instagram wanda hankali a tashe ta tashi ta yi hanyar gidan Nenehn tun da compound ɗin ake nunawa a cikin video ɗin.

Salimah kam tun ranar da Hydar ya zo gidan gaba ɗaya ta rasa yadda za ta yi da rayuwarta, dan ta ji cewa Liyanar babu lafiya, sai ita ma a ɗazun ta ga cewa news na yawo ya'r Nabil is dead, hakan ya sanyata kulle ƙofar gidan ta nufo hanyar zuwa gidan Nenehn.

Kusa da Ammi Liya ta kwana ta na baccin ne kawai amma sam ba ta jin daɗinsa dan jinta take kamar a wajen da ta yi kusan sati a takure, dan sai anyi sadakan uku yadda Jiddah ya faɗa sannan kowa zai koma gidansa, tun da Liyanar ma lafiyarta ƙalau.

Bayan Ammi ta tasheta da Asuba sallarta ta yi tare da ƙoƙarin komawa bacci wanda sam Ammi ta haneta akan sai ta tsaya ta godema Allah da ya bata dama na biyu a rayuwa ta cike taskes ɗinta .

Da ƙyar ta yi addu'an sannan ta koma ta kwanta wanda sai a lokacin cikinta ya ɗan ɗago wanda da alamu dai yanzu ya ta so daga kwancen da aka sanya shi yin.

Sai a lokacin idanun Ammi ya sauka akan cikin dake jikinta sannan a hankali Ammin ta ce ''Kina zuwa awo or you're taking it un serious just like your life.'' Ammin ta ƙarashe maganar tare da ɗan taɓa cikin Liyanar.

Marairaice face ɗinta ta yi tare da faɗin ''Ammi please later bacci nake ji.'' ta ƙarashe maganar tare da ƙoƙarin kwantawa.

''za ki tashi ko sai kin gane rashin lafiyar da kika yi nafila ne.?" Ammi n ta faɗa rai a ɗan ɓace.

Fashewa ta yi da kuka tare da ɗan dire ƙafarta sannan ta ce ''Ammi please nah, ɗan ya na lafiya ko yanzu sai da ya buge ni manaa.'' ta yi maganar tare da share ƙwallarta.

''Alright magana ta ce ba za ki ji ba kenan har yau, tashi ki fice min daga ɗaki kafin na ɓata miki rai.''

Ammin ta yi magana cikin fushi.

''Ammi atleast ki tausaya min mana, yaushe nayi rashin lafiya na tashi, ko 48 hours ba'a yi ba amma gashi ana ƙoƙarin haɗa min wani.'' Liyana ta yi maganar haɗe da ɗan turo bakinta.

Yunƙurawa Ammin ta yi kamar za ta tashi dan ta ga sturbborness ɗinta ƙaruwa yake ba raguwa ba, hakan ya sanyata saurin ficewa daga cikin ɗakin dan sam ba ta jin wani alamun rashin lafiya a tattare da ita.

Bigewa ta yi da mutum a hanyar ta na ficewa daga corridor ɗin guest room ɗin sannan a hankali ta ja baya ta na ƙoƙarin komawa ɗakin Ammin.

Saurin jawota ya yi jikinsa tare da buɗe ƙofar da yake tunanin empty room ne ya yi saurin kulle ƙofar tare da jinginata da bayan ƙofar.

Ɓare baki ta yi kamar za ta yi ihu hakan ya sanya shi haɗe bakinsa da na ta ya fara sumbatar ta, zaro idanunta ta yi dan ganin Abbhinta ya fito daga toilet hannunsa riƙe da wani towel ya na goge jikinsa da shi.

Ƙara waro idanunta ta yi sanadiyar haɗa idanunta da ta yi eye ball to eye ball da Abbhinta da ya yi saurin juyawa ya koma toilet ɗin ɗakin.

Da dukkanin ƙarfinta ta haɗa tare da turesa, ƙara jawota ya yi jikinsa da sassarfa ya na mai rungumeta tsam jikinsa, buh he can't feel that comfort of hug, saboda tumbin da ya ɗan tokaresa.

Saurin waro idanunsa ya yi tare da yi ma ta pointing cikinta da ya turo gaba sosai.

Ita dai ba ta biye ma sa ba ta sanya kanta ta fice daga cikin ɗakin, dan har ga Allah ba ta son Abbhin ya ƙara tadda ta a wajensa.

Ya yi kusan minti biyar a wajen da ta bar shi sannan ya saki wani kalar murmushi wanda ya tsaya ma sa iya laɓɓansa tare da shafa gemunsa zuwa bayan wuyansa sannan ya bar cikin ɗakin shima.

Dan shi kansa bai san mai ya kawo shi gidan ba, he just feel like ba zai samu nutsuwa ba har sai ya ganta, ya ji ɗuminta.

Fitowarsa daga ɗakin ke da wuya ya kusa cin karo da Neneh da ke cikin shigarta na Lifaya , sai da ta firgita ganin Hydar ɗin a gabanta, sannan a hankali ta dalla ma sa harara ta bi ta gefensa ta shige backyard zuwa traditional kitchen saboda ganin abin da mutanen gidan ke dafawa na sadaka.

Shima Hydar wani kalar harara ya banka ma ta tare da raɓewa ya bi ta kusa da ita ya fice daga cikin gidan, dan shi ya na mugun son ya ga ana jin tsoro a rayuwar sa.

Ko da ya isa gidan Mamin ko ina na gidan tsit, suma ya'n aiki na can backyard ana ta dafa abincin sadaka, ya na zaune a falo ya ji ana wani kalar ƙwanƙwasa ƙofa kamar za'a ɓalla sa, sannan daga bisani ya fara jin muryar Assultanah dake time ɗin har 10 O'clock na safiya ta yi.

Kuka take mai tsuma zuciya ta nufo falon, ganin Hydar a falon, shi ya sanya ta ƙara sakin wani kuka tare da faɗawa jikinsa ta na sakin wani kalar kuka mai tsuma zuciyar mai sauraro, sannan a hankali ta fara magana ''Yaya mai sa a ka binne ta ba tare da an jira ni ba.'' ta ƙarashe maganar cikin shashsheƙar kuka.

Sai da Hydar ya ɗan kalleta sannan ya ɗauke kansa tare da cire kanta daga jikinsa sannan a hankali ya ce ''Gidansu za ki je, sai ki shigar da ƙara.'' daga haka ya ɗauki wani Apple da ke cikin wani fancy basket dake kan center table ya nufi part ɗinsa dake nan tsaf.

Tashi ta yi ta nufi hanyar gidan Nenehn, duk ya'mmatan na zazzaune suna hira har da Liya da suka sa ki jikinsu da ita ana ta hira har Yusrah dake ta shishige musu.

Ko sallama ba ta yi ba ta shigo cikin falon ta na wani kalar kuka, ganin Liyana zaune ta na dariya hannunta riƙe da wasu guava da Hydar ya sa aka kawo ma ta ɗazun ne ya sanyata suman tsaye tare da kallon mutanen falon.

Wani kalar ihu ta saki wanda hakan ya ƙara janyo attention ɗinsu gabaɗaya tare da ƙafe Sultana da idanu.

Ta mugun tsorata da ganin Liyanar a cikin gidan, dan sai da tayi suman tsaye na ya'n daƙiƙu sannan ta dawo hayyacinta.

A na tsaka da shawo kan lamarin Assultanah Lily ta danno kai cikin gidan, a kiɗime ta fara addu'ar ta cikin Greek Words dan a tunaninta Ghost ce, sannan a hankali a ka fahimtar da su.

Har a ka yi sadakan uku da Jiddahn ya faɗa ko ƙeyar Rufaidhat ba'a gani ba a cikin gidan, wanda Abbhin ke sane da ita da hakan da ta yi, ita ma Mama Fatuh tun bayan zuwan su Sultanah da ta zo suka tafi da Yusrah a ranar suka wuce Niger.

Aranar sadakan ukun kan duk yadda aka yi da Neneh akan Liya ta yi bakwai a gidanta ƙi ta yi ta na faɗin cewa ''Kyan ya' mace gidan mijinta.'' a haka aka bar zancen Liyanar ta koma gidan Hydar ɗin da har ya dawo da workers ɗin gidan.

Bayan one week ta koma school dake duk ya'n school ɗin sun san da tashin na ta hakan ya sanya ta ci gaba da harkar gabanta kamar yadda ta saba.

HYDAR kam har wani kalar tsoron kusantarta yake kar ya zamana cewa sihirin dake tattare da kwanciyar ta su ba ta karye ba.

Ammi kullum cikin addu'a take inda soyyayar ta da Abbhi sai daɗa linƙaya take, amma dake ance zaman aure sai haƙuri ba za'a rasa abin da ke damun zuƙatan masoyan guda biyu ba.

Ɓangaren Neneh kuwa har yau cikin shige da fice take dan wajen gano waya'nda suka aikata wannan lamarin ga jikarta, duk inda taje siffofin mutane biyu kawai ake ba ta amma ta kasa gane su waye su.

Zaune take cikin shigarta na wani simple abaya mara nauyi, sai laɓɓanta dake sanye da wani lipstick mai ƙyallin gaske, kanta sanye yake da hula, hannunta riƙe da wani bowl mai ɗan girma da yake cike da kayan cikin naman saa da ya ci uwar garlic.

Ta na ci ta na kallo a TV ɗin falon dan yanzu sam wayar hannunta ba ya damunta tun da cikinta ya kai 5 months and 2 weeks, har yanzu da ta kusa sati biyu da dawowa gidan bai cika wani kulata ba illa ya tambayeta mai za ta ci a siyo ma ta ko a dafa mata.

Sanye yake cikin wani combat black color sai wani white designer plane shirt da ya ɗan kama jikinsa, fuskarsa idan banda ƙyalli babu abin da yake fitarwa banda zallar rich glowing skin.

Ƙarasa sukowa ya yi daga stairs ɗin tare da samun waje ya zauna kusa da ita, sidda kanta ta yi ƙasa dan wani kalar nauyinsa take, ga soyyayarsa dake mamayar zuciyarta.

Waro idanunsa ya yi ganin ƙaton plastic bowl ɗin dake hannunta cike da kayan cikin da sai a iya amfani da su na kwana uku zuwa huɗu.

Amsar bowl ɗin ya yi daga hannunta tare da tallaɓo kanta ya ɗaura akan kafaɗarsa, sannan a hankali ya fara faɗin ''I know it will be a little bit difficult for us to live like a couple, duba da yadda haɗuwar mu ta faro da kuma yadda muka yi treating junan mu a gidan nan, Liyana!." Ya ƙarashe maganar ya na mai kiran sunanta tare da yin yawo da hannunsa akan gashinta.

Cikin sassanyar muryarta mai daɗin sauraro ta ce ''Na'am Yaa Alih.'' ta ƙarashe maganar ta na wasa da hannun abayarta.

Sai da ya ɗan jinginar da kansa tare da shafa fuskarsa izuwa gemunsa sannan ya ce ''Ba zan iya cewa i can't accept you a matsayin matata ba, duba da yadda kike ɗauke da cikin da nayi sanadinsa, and ni ba zan ba ki haƙuri a kan wani laifin da yake a matsayin gyara na yi ba, soo can we friends, friends with benefits.....

Jiya banda data Wallahi kuyi haƙuri 😂

Manage please □□

Mutuwa kan kawo canji

''Ya Ubangijina ka basu daman share."

Allah ya yiwa fans ɗina masu sharing arziki fiye da Dangote □□□

Ma ra sa share Allah ya kawo kuɗi na siyi mota na tada muku ƙura □□😂😂□

THE REGRET

PENDING AMARYA CE ✍

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION

The Noble Writers Team.

Pending Amarya 54.

What goes around comes around □ □

Every ending is a new beginning □□ even if the heart disagrees.□○□□

□ □ □

Not edited □□□

****

Sai da ya ɗan jinginar da kansa tare da shafa fuskarsa izuwa gemunsa sannan ya ce ''Ba zan iya cewa i can't accept you a matsayin matata ba, duba da yadda kike ɗauke da cikin da nayi sanadinsa, and ni ba zan ba ki haƙuri a kan wani laifin da

yake a matsayin gyara na yi ba, soo can we friends, friends with benefits.'' ya ƙarashe maganar tare da ɗage girarsa guda ɗaya yana mai miƙa ma ta hannunsa alamun shaking.

Sidda kanta ta yi daga kallonsa sannan a hankali ta ɗago manyan idanuwanta tare da faɗin ''Babu duka babu zagi, only friends, and banda rankwashi.?" Ta ƙarashe maganar a ɗan shagwaɓe.

Matsowa ya ƙara yi sosai kusa da ita lips ɗinsa ya na brushing na ta, idanunsa a cikin na ta in a whispering voice ya ce ''Yeah of course, amma in one condition.'' ya ƙarashe maganar ya na bata wani light kiss a lips, sannan ya ɗora da faɗin ''Duk abin da na ce kiyi za ki yi shi, and when I want something, dolen ki ki bani, are we good to go.?" Ya yi maganar ya na ƙara matsowa kusa da ita.

Gyaɗa kanta ta yi sosai kafin ta yi maganar da take da niyyar yi ya haɗe lips nasu trying to get what he wants from her, sannan ya sunkucheta ya nufi ɗakinsa da ita, they made love.

Ita ta san ta na son Hydar, soyayyar da ko kwatan shi ba ta nunawa ƙaninsa ba, babu abin da zai ma ta a duniya da za ta ji tsanar sa a duniya.

Da ƙyar ta tashi ta mayar da kayanta haɗe da ƙoƙarin barin dakin na sa amma ya hanata.

Kwance suke waje ɗaya kanta na kan kafaɗarsa jikinta gabaɗaya na mata wani kalar laushi, hannunsa ɗaya na shafa yalwataccen gashin kanta, cikin wani kalar murya mai sanyi wanda ke ƙara jafa ta a cikin wani yanayi ya fara magana ''Ina kike son muje honey moon?." Ta tsinci muryarsa a cikin kunnenta.

Gyara kwanciyarta ta yi a jikin na sa tare da ɗan ɗago kanta ta na mai duban kyakkyawar fuskarsa, sannan a hankali ta ce '' Just suggest, abin da kake so nake so ni ai.'' ta yi maganar ta na wasa da kwantaccen gashin dake ƙirjinsa.

Sosai ya ji daɗin kalmar ta sannan a hankali ya ce ''From Saudi Arabia, sai mu wuce China and Switzerland are you okay with that.?"

Gyaɗa kanta kawai ta yi sannan ya ƙara gyara ma ta kwanciyya a jikinsa bacci mai daɗi ya yi awon gaba da su.

Da sassafe ta tashi ta nufi ɗakinta ganin ba ya cikin ɗakin kuma bai tashe ta ba, bayan ta idar da sallarta ma tilawarta ta cigaba haɗe da yin azkar sannan ta fito kitchen ta kamawa Salimah girki.

Cous cous ne sai pepe soup tare da bread suka dafa, sai coffee da ta haɗa ma sa a coffee mixer ta ajiye a kan kitchen island ɗin.

Within 2 mins ya shigo cikin gym wears ɗinsa hannunsa riƙe da bottle water da kuma hanky.

Already daman bayan ta gama girkin ɗakinta ta shige tare da yin wanka ta shirya cikin wide leg trousers ɗinta (palazzo) sannan ta ɗora da wani babban T shirt Wanda zai sa ka cikin jikinta balance sosai, sannan ta ɗora simple hula a kanta tare da saka slippers ɗinta ta fito falon.

Ta na zaune ya shigo cikin falon, murmushi ya sakar mata mai kyau sannan ya zauna akan ɗaya daga cikin kujerun dake falon.

''Girlfriend, you look beautiful today, irin wannan kyau haka kamar Zebra.''

Ya yi maganar tare da amsan coffee ɗin da Salimah take miƙo ma sa.

She just smiled at him, sannan ta ce ''Yaya ina kwana.'' ''Lafiya lau, ki shirya yau zamu fita siyayya.'' ya na faɗin hakan ya haura sama domin shiryawa.

Tun da ya shige ɗakinsa ta na cikin falon babu inda ta motsa sai ma Tvn da ta ƙurawa ido.

Sanye yake cikin wani plane designer t shirt black color, sai wani _Saint Laurent_ jeans black color, ƙafafunsa sanye cikin wasu Fendi slippers, sai car key ɗinsa a hannunsa.

Har ya ƙaraso wajen da take ba ta san da isowansa ba , ita dai kawai ba ta ma san mai yake damunta ba.

Saitin fuskarta ya saita tare da kaɗa ma ta car key ɗin hannunsa, a firgice ta dawo hayyacinta tare da sakar ma sa murmushinta mai kyau.

''Je ki shirya, and don't keep me waiting.'' ya yi maganar a taƙaice tare da ficewa daga cikin falon.

A hankali ta tashi tare da nufar saman stairs.

Direct ɗakinta ta shige tare da sanya kimono akan shigarta, sannan ta ɗaura da wani babban mayafi wanda hakan ya bawa shigarta wani kalar kyau na wuce misali.

Slippers ɗin ƙafarta ta bari ba ta canza ba sannan ta fito daga gidan ta na mai yiwa Salimah sallamah.

A hankali take takowa har ta ƙaraso cikin motar na sa.

Tayar da motar ya yi tare da barin cikin unguwar gaba ɗaya, shiru ne ya ratsa cikin motar, kowa na ta saƙe -saƙe a cikin zuciyarsa.

A hankali ya kamo zara-zaran fingers ɗinta ya na kallon yadda suke a cike, farare tal dasu gwanin ban sha'awa.

Jin lallausan palms ɗinsa a kan hannunta ne ya sanyata ɗagowa da sauri ta na mai kai dubanta kan sit ɗin nasa.

''Dubi fingers ɗinki kamar na horror movies, Sam ke a rayuwarki idan ba kiyi ƙazanta ba ma ba kya jin daɗi ne.?" Ya yi maganar da ɗan sauri tare da danna horn a dai-dai wani kantamemen building.

Bayan mai gadi ya buɗe gate ɗin, wajen parking space ya nufa tare da yin parking ɗin motar, a babban parking space ɗin gidan dake jere reras da luxury rides.

A hankali ya fito daga cikin motar, ita ma jiki duk ba ƙwari ta sauko tare da zagayowa wajen da yake tsaye.

''Kin san Allah kar ki min ƙauyanci dan naga ku mata da kun yi aure duk wayewarku ƙauyawa kuke komawa, You better behave yourself.'' Ya yi maganar tare da fara tafiya towards the building.

Walking slowly ita ma ta bi bayansa trying to engage with her late courage.

A hankali ta ƙaraso har ƙofar entrance ɗin da yake tsaye yake danna door bell.

Bayan an buɗe musu ƙofar a hankali suka shiga cikin parlourn da sai tashin ƙamshi yake, wata ya'r budurwa ce zaune kan cushion ɗin falon cikin wasu pyjamas white color ƙafarta sanye da wani soft slippers na bacci, wanda da dukkan alamu daga bacci ta tashi.

Ɗago idanunta ta yi da kyau ta kalli yarinyar dake zaune wanda ita ma a dai-dai lokacin ta ɗago ta kai dubanta wurin da suke tafe.

Waro idanunta ta yi ganin Papi a gabanta wanda hakan ya sanyata cilli da wayar hannunta da gudu ta na mai rungume shi.

Unexpectedly ya ji saukar mutum a jikinsa wadda sam bai lura da wanzuwar ta ba a falon.

Shi ma Waro idanunsa ya yi da kyau tare da faɗin ''Ahh Marwa, kar ki karya ni mana.'' ya ƙarashe maganar tare da janyeta daga jikinsa.

Murmushi wadda aka kira da Marwa ta yi tare da faɗin ''Papi na yi missing na ka sosai, for almost six years we didn't see each other, Kuma you're expecting me not to hug you.?'' ta ƙarashe maganar ta na murmushi mai nuna alamar zallar zumuɗi, tare da jan hannunsa ta zaunar da shi kan kujerar.

Ita sam ba ta lura da Liyanar da take tsaye a kumbure kamar yeast ba, ta matsa daga wajensa tare da nufar hanyar kitchen domin kawo masa abin sha.

Cikakken hips ɗinta ya bi da kallo tare da mayar da kansa gefe wanda hakan ya sanya idanunsa da na Liyana haɗuwa ta na tsaye wajen da ya barta.

''Ke azumin zama kike ne da ba za ki zauna ba.?" Ya yi maganar ya na ƙurawa kyakkyawar fuskarta ido.

Ɗauke kanta ta yi tare da juyar da shi gefe wanda hakan ya yi dai-dai da isowar Amir cikin living ɗin, jikinsa sanye da wasu native dress masu kyaun gaske.

Amir na mata magana hakan ya sanyata yin murmushi suka gaisa sannan ya yi mata insisting zama kusa da Aliyun sannan ta zauna.

Tafe ta ke hannunta riƙe da wani serving tray mai kyaun gaske, ɗauke da kayan sha da na motsa baki.

Sannan a hankali ta ajiye tray ɗin tare da kallon Liyana dake kusa da Papi da idon mamaki.

''Who's she Aliyu.?" Marwa ta tambayi Hydar idanunta a kan na Liyana da jin tambayar da ta ke ma Hydar ɗin ya sanyata ɗago da kanta ta kalli Marwa ɗin.

HYDAR dake ta daddanna wayarsa ne ya ɗago tare da kallon Marwa kafin ya yi magana har Amir ya riga shi da faɗin ''Don't you dare create any problem, kina dai jina ko.?" Ya yi maganar tare da dailing wayar Umminsu ya na mai sanar ma ta Aliyyu da matarsa sun iso.

Babu jimawa Ummi ta ƙaraso falon cikin wani simple Egyptian abaya.

Sosai Ummin ta yi farincikin ganin Liyanar da Hydar.

Ba su fi mintuna talatin ba Hydar ke sanar ma Ummi zasu tafi, sosai ta haɗa ma Liyana turaruka da wasu kayan sha'anin mu na mata.

Marwa dai ta kasa magana dan ita a tunaninta wajenta ma Hydar ɗin ya zo.

Bai ƙara kallon Marwar ba ya wuce shi da Liyanar da taƙi Sam ta haɗa ido da kowa na wajen.

Suna shiga cikin motarsa ta haɗe kanta da gwiwa ta fara wani kalar kukan da ba ta san dalilinsa ba.

Har cikin ƙwaƙwalwarsa yake jin kukan na ta wanda hakan ya sanya shi samun gefen titi ya yi parking ɗin motar.

''Fatima what's wrong.?" Ya yi maganar ya na ɗan kallonta, ganin ba ta ba shi amsa ba ya sanya shi ɗan kai hannunsa da niyar taɓa ta.

Da sauri ta ɗago tare da buge hannunsa tare da faɗin ''Don't touch me.'' sannan ta jinginar da kanta wajen sit belt ta ci gaba da kukanta.

Ganin sanyin da yake ƙoƙarin fara ma ta ba son sanya raini a tsakaninsu ne ''ya sanya shi juyo da kanta a fusace ya na mai kallon cikin idanunta.

Ƙoƙarin cire hannunsa take a jikinta amma ta kasa, hakan ya sanyata sadaƙarwa tare da ƙafesa da manyan idanunta.

Haɗe bakinsa ya yi da nata ya bata wani light kiss tare da mayar da ita baya kaɗan, kana ya ce ''Tell me what's going on, why are you frowning, kin san fushi ba ya miki kyau, you look like gorilla, idan kika yi kuka kuma, kama kike da ostrich, sai wuyan ki ya yi dogo.'' ya yi maganar yana gesturing da hannunsa.

Ƙara fashewa ta yi da kuka sannan ta ce ''After the cin mutumci of that hug har da zagina kake, a gabana yarinyar nan ta rungumeka and you're even enjoying the hug, ''Ahhh Marwa kar ki karya ni'', haba Yaya Aliih wannan ba girmanka bane sam sam.'' ta ƙarashe maganar tare da ɗaukan tissue ta na goge hawayenta.

''Ahh okay, sakar miki fuskan da na yi har ya kai da za ki ɗinga ga ya min magana son ranki kenan, ya yi kyau.'' ya na faɗin hakan ya yiwa motarsa key tare da barin wajen.

Bai ma ta magana ba ita ma ba ta masa ba har yaje ya yi shopping ɗinsa ma ba ta fito daga cikin motar ba, a cewarta kar ta ga abin da ya fi ƙarfinta a wannan karon.

Sai da yamma sannan suka dawo gidan shi ma ko abincin da aka jera a dinning ba ta ci ba ta wuce saman ɗakinta duk da yunwar da yake nuƙurƙusanta.

Ya na kwance a ɗakinsa ya na kallon duk wasu moves ɗinta.

Seeing her naked body always turns him on, kamar magnet haka ya yi ta jan ƙafa har ya ƙaraso cikin ɗakin nata.

Tsaye take a gaban madubi jikinta ɗaure da towel light color, ta na shafe jikinta da tsadaddan manta.

Jin an fisge towel ɗin jikinta ne ya sanyata ɗagowa a razane tare da kallon yadda yake binta da wani kalar mayen kallo.

A fusace ta fisge towel din na ta daga hannunsa haɗe da dalla ma sa harara sannan ta yi hanyar restroom ɗinta.

Saurin fizgota ya yi ta faɗo jikinsa, sannan a hankali ya fara massaging jikinta.

''Ni ka daina taɓa ni, just go away, go and make your stupid love to her.'' Liyana ta yi maganar a hasale tare da ƙoƙarin fizge jikinta daga nasa wasu hawaye na zubo ma ta.

''Sorry i can explain.'' Hydar ɗin ya faɗa tare da stretching hannayensa a kan kafaɗarta ya na kallon cikin idanunta.

''Explain what?, the hug?, or that stupid Marwa.'' ta yi maganar ta na nuni da hannunta kamar Marwa na wajen.

Wani kalar numfashi ya furzar wanda a take idanunsa suka yi wani kalar jaa, sosai ta tsorata da ganin yanayinsa yadda yake wani kalar huci kamar mayunwacin zaki, sannan a hankali ya soma magana '' Can you just give me a chance to talk, I can explain na faɗa miki, Marwa..... Marwa is the girl that I intended to marry few years back, na sota a lokacin, amma ta watsa min ƙasa a ido, ta zaɓi wani a maimakon ni, kuma har yanzu ina jin sonta a raina, amma ki yarda dani sam ban yi tunanin za ta yi hugging na wa ba, i didn't even see her, why am I even telling you this bayan ba yarda za ki yi ba.'' ya ƙarashe maganar ya na ƙoƙarin zama a cushion ɗin ɗakin.

''Karka zauna min a ɗaki, tun da Marwa ce wadda kake so sai ka nufi wajenta, thank God da ban ma yi accepting ɗin stupid friendship ɗinka ba.'' ta yi maganar hawaye na ɗan zuba daga idanunta.

''My Lord, ke nake so yanzu ba ita ba just understand.....

Jiya banda data Wallahi kuyi haƙuri 😂

Manage please □□

I'm missing something precious □😭

''Ya Ubangijina ka basu daman share."

Allah ya yiwa fans ɗina masu sharing arziki fiye da Dangote □□□

Ma ra sa share Allah ya kawo kuɗi na siyi mota na tada muku ƙura □□😂😂□

THE REGRET

*PENDING AMARYA CE *□□□

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION✌□

Page 55

Respect that lady that wants nothing from you but your loyalty and real love □□□□❤
Respect her bro 😎 □□□😌

Note edited ✍✍✍

><><<><><><>

My Lord, ke nake so yanzu ba ita ba just understand.” Ya yi maganar ba tare da ya san ya faɗe ta ba.

Jin maganar da ya faďa ne ya sanya ta ďagowa da sauri, Wanda hakan ya sanya shi saurin ďago da wani zancen daban tare da tashi daga zaunen da yake ya na mai tallab'o hab'arta tare da faďin "Liyana , idan kika natsu za ki fahimci duk abin da nake son fahimtar dake, for my pass life I make some mistakes that ni kaina idan na tuna su I feel like dying…'' bai kai ga ḳarasa maganar ba ta yi sauri ta cab'e haďe da faďin " You make love with her right?, daman na san za'a rina, you cheated on me tun kafin ka sanni." Ta ḳarashe maganar tana mai zama a kan edge ďin gadon, hawaye na silala a kan fuskarta.

" Noo wallahi Liyana is not what you're thinking." Ya yi maganar tare da ḳara janyota jikinsa.

" Let go of me, ni wallahi ka daina tab'a ni tun da Marwa kake so, sai ka je ka aureta daman akwai parts da dama a gidan sai ka ajiyeta.'' Ta ḳarashe maganar ta na gyara zaman towel ďinta.

" Liyana ki gane mana, wallahi she's just a friend." Ya yi maganar trying to get her lips on his lips.

" Incredible, first ka ce min she's the girl da kake son aura, amma yanzu you're telling me she's just a friend, are you okay?." Ta yi maganar a hasale.

" Are you insulting me?, ko kin fara shaye shaye ne?, tun da har Ina lallab'a ki kin ḳi ganewa sai mu zuba dake, spoiled brat, oya hau kan gadon nan kafin na kwashe ki da maruka a wajen nan." Ya ḳarasa maganar a zafafe.

Fashewa ta yi da kuka sosai sannan a hankali ta ce “ Daman na san ba sona kake ba, since from day one a haďuwar mu ba sona kake ba, Allah ka zama gatana a gidan Aliyu, daga wannan sai wancan , ni na gaji.” Ta yi maganar ta na mai goge ďan ḳwallan da ya zo ma ta.

Saurin jawota ya yi jikinsa tare da rungumeta sannan a hankali ya fara sakar mata kiss a goshi sannan salon labarin ya sauya.

Washe garin ranar ma da mugun kwaďayin abaćha ta tashi.

Ko da ta farka ba ta gansa ba cikin ďakin jiki ba ḳwari ta nufi toilet tare da yin duk abin da ya dace sannan ta fara harraman sallah.

Bayan ta idar da sallar ma direct kitchen ta nufa tare da kamawa Salimah aikin da ya dace sannan ta koma samanta shirya cikin wani silky gown da ya mannewa shape ďin jikinta.

A hankali take saukowa daga saman stairs ďin hannunta ďaya na dafe da ḳasan cikinta ya yin da ďayan hannun ke riḳe da mariḳin benen.

A dai-dai lokacin kuma Hydar ya buďe ḳofar parlourn hannunsa riḳe da bottle water da hanky ya na goge gumin jikinsa.

Kallon second biyar ta ma sa sannan ta ďauke kanta ta cigaba da taunan chewing gum ďinta, sannan ta tako a hankali ta zauna a kan three sitter tare da ďaura ḳafafunta a saman center table.

Da kallon mamaki kawai ya bita da shi tare da fara ḳoḳarin wucewa domin ya shirya, dan daga yau zai fara shirye - shiryen su na tafiya china.

Har ya wuceta ya jiyo siririyar muryarta a kunnensa na faďin “Yaya Alih dan miḳo min Apple.” Ta yi maganar ta na ďan shafa cikinta.

Bai tanka ma ta ba ya wuce har zuwa inda take ya ďauki basket ďin apple ďin gabaďaya ya miḳa ma ta.

Har ya tafi ta kuma kiransa, ḳanḳance idanunsa ya yi tare da miḳo ma ta remote ďin da za ta iya stretching hannunta ta ďauka, sannan ya ďauka ya miḳa ma ta.

Daga haka ya wuce stairs da ďan sauri ba tare da ya ḳara ko kallon inda take ba.

Ko da ya ḳarasa ďakinsa ma banďaki ya shiga direct tare da yin wanka.

Zaune take a yadda ya barta hannunta riḳe da plate ďin abinci, ďayan hannunta na kan cikinta ta na shafa shi kamar jikin kyanwa.

Ḳarasowa ya yi cikin shigarsa na wani sky blue ďin _Senate wears_ hannunsa na sanye cikin aljihun wandonsa, sai ḳafafunsa dake sanye da wasu takalma masu kyau da tsada black color, kansa kam na sanye da hula black kalar na yoruba people ďin nan.

Kallonsa ta kai garesa ta ga yadda shigarsa ya masa wani kalar mugun kyau, ga wani haska shi da kayan suka yi.

Take taji wani kalar wutan kishinsa na wuruwa a cikin zuciyarta.

Bai bi ta kanta ba ya wuce dinning ya na mai zama, coffee kawai ya sha mai madara sannan ya ďauki car key ďinsa.

“Ina za ka je.?” Ya tsinci muryarta a cikin kunnensa.

A fusace ya juyo tare da faďin “ Wallahi daraja ďaya kike ci a gidan nan you better behave yourself, just because ina ďan ďaga miki ḳafa kar ki saki ki ďauko hanyar raina ni, c’mon wuce ki ďauko himar ďinki ki same ni a cikin a mota.” Ya ḳarasa maganar tare da ficewa daga cikin gidan.

Sai da ta saki wani tsaki sannan ta wuce ďakinta tare da ďaura wani zunbulelen hijab a kan kayan jikinta.

Sai da ta bawa Salimah sallahun lunch ďin da za a yi sannan ta bar living room ďin.”

Tsaye yake jingine da motarsa ḳirar Lexus hannunsa riḳe da wayarsa Wanda alamu sun nuna chatting yake.

Bai ji alamun tahowarta ba sai Jin ḳwace masa waya da a ka yi.

Da sauri ya ďago kansa tare da kai dubansa wajen da take tsaye, ta na kallon screen ďin wayar ta na kuma kallon inda yake tsaye.

Ji take kamar ta buga wayar da ḳasa ko za ta ji sanyin abin da take gani a ciki.

Kamar wata mai asthma haka numfashinta ya yi ta mata barazanar ďaukewa, ganin hakan ne ya sanya Hydar saurin tallab’ota amma ta ḳwace jikinta daga cikin nasa hawaye na ḳoḳarin fita daga idanunta.

Miḳa ma sa wayarsa ta yi tare da shigewa cikin motar tare da mayar da kujerarta baya ta na mai ďan kishingiďa.

Fashewa ta kuma yi da kuka tare da juyar da fuskarta ta na kallon window ďin b’angarenta.

Ko da ya shigo ma sai da ya ďan saci kallonta sannan ya fara tuḳin motar.

Sun ďan yi nisa da fara tafiyar sannan yaji saukar muryarta kamar saukar aradu.

“Explain it Aliyu.” Ta faďa tare da karkato da jikinta ta na kallonsa.

Bai ma ta magana ba ya cigaba da tuḳinsa.

Cikin wani kalar murya ta ḳara faďin “ Aliyu explain what I just saw, ko na kashe abin da yake cikina tun da ka na da wani .” Ta ḳarashe maganar ta na shafa cikinta hawaye na ďiga daga idanunta.

Saurin take birki ya yi tare da parker motar a lokaci ďaya ya na mai juyowa tare da fuskantar Liyanar.

“Please Liya zan miki bayani idan kika ba ni dama stop this childdish okay!.” Ya yi maganar tare da dafa hannunta.

D’ago jajayen idanunta ta yi tare da sauke su akan kyakkyawar fuskarsa.

Wani kalar ajiyar zuciya ya sauke tare da matso da kansa ya sakar ma ta wani kalar kiss a goshi sannan a hankali ya ja baya tare da fara fadi̓n.

“ Amir is my favorite Cousin, he has one sister which is Marwa, Maman Amir da Mami are sisters, and Abbha and Abbhu are also brothers from the same mom and dad.

A gidansu Amir na yi kusan rabin rayuwata, hakan ya saka ni sabawa da Marwa sosai.

Na so Marwa sosai ba wai soyayyar yan uwantaka ba, soyayya na aure, dan har feelings namu bamu iya b’oyewa musamman da muka fara zama teenagers.

Marwa is 28 years old a yanzu, na girmeta da shekaru 5, lokacin da na gama secondary school da zan tafi China a lokacin ita kuma ta na ss one a lokacin ne muka fara sexing each other. That’s the first time that I noticed what women really feels like.

Ko da naje Beijing bayan na yi one year itama tayi waec and neco ta ce dole sai an dawo da university dĭnta a can Beijing.

Shi kuma daman Amir Germany is his best country dan nan ya saka a first choice dĭnsa.

Bayan dawowan Marwa babu abin da muka maida hankali a kai sai kasancewa da junanmu.

Ina level 300 a time dĭn ta na level one ta samu ciki bamu lura da cikin ba sam har sai da ya bayyana.

A lokacin mun shiga tashin hankali sosai mara misaltuwa.

And we have no option sai dai ta haifeshi.

Bayan ta haifi yarinyar da kwana dăya yarinyar ta mutu that was 2011 .

Na barta ta huta for good three months sannan muka cigaba daga inda muka tsaya.

Ko da nayi final year dĭna ban dawo gida ba na cigaba da masters.

2015 ne muka dawo gida gaba ɗaya then muka faɗawa iyayenmu muna son juna har aka fara shirye shiryen aure a tsakaninmu.

Still mukan haɗu da Marwa a hotel ko wani ɗan ḳaramin gida da Abbhu ya siya min, we always made love there.

Bayan results dinmu ya fito ma I suggest na dubo mata, a lokacin aure na da ita saura one week.

Ko da na dawo ban nemi naje gida ba sai gidana da yake a nasarawa.

Ko da na Isa gidan Marwa na tare da wani namiji wannan shine dalilin da yasa na fasa aurenta.

Ita kuma ta koma North Korea ta cigaba da karatunta, Amma dan Allah Liyana I’m very sorry I don’t know that akwai ranar da zan faɗawa wani all this, yanzu hoton jaririyar ta turo min wai we have to remake our little angel again.” Ya ḳarashe maganar hawaye na zuba a idanunsa.

“Innalillahi wa inna ilaihir raji‘un, Hydar you’re once stucked into Haram relationships and calling me yar iska all this years, ni yanzu ya’ya’na kar wani ya zo ya musu abin da ubansu ya yiwa ya’ya’n wasu.” Ta yi maganar hawaye na zuba a idanunta.

Janyota jikinsa ya yi ya na shafa bayanta tare da faɗin “ Babu abin da zai faru da su please, don’t say those words again kin ji , kowa ya na da mistake a rayuwa nawa

mistake dĩn kenan and I’m still REGRETTING.” Sannan ya janyeta a jikinsa tare da tayar da motar suka nufi gidan Neneh dan har ḳarfe shabiyu na rana ya yi.

Jiki a sanyaye ya yi horn a gaban gate dĩn gidan Nenehn, da ďan sauri gate man ya zo ya buďe ya na musu waving dĩn hannu at same time kuma ya na miḳa gaisuwarsa zuwa ga Aliyun.

Aliyu just nodded his head countinue to search for inda zai parker ride dĩnsa.

Bayan ya parker motar ma jikinsu a sanyaye ya riḳo hannunta suka ḳarasa shigowa gidan Nenehn.

A zaune take kamar yadda ta saba zama ta na hira da yan aikin gidanta, idanunta sanye da eyeglasses cikin shigarta na lifaya butter color da ya mata kyau sosai.

Ḳarasa shigowa suka yi bakinsu ďauke da sallama ko da Neneh ta ďago ta ga way’anda ke tafe sai da zuciyarta ta yi wani irin faďuwa sannan ta dake ta cigaba da magana da Fadila sannan a hankali ta ďan kallo su Liyanan tare da fadĩn “Baḳin

lahira maso gabas an iso kenan.” Ta faďa tare da cire eye glasses ďinta ta na mai dallawa Hydar harara.

Shi kam bai wani kulata ba ya ďa rage tsayinsa tare da gaisheta.

“ Wallahi da wannan ya’r iskar gaisuwar mai sifirin da barina ka yi a hakan ba ka gaishe ni ba, Aa toh dan da safe ake kalar wannan gaisuwar.” Neneh ta faďi hakan tare da ďan saci kallon Liyana.

Tsaki Hydar ya ja tare da zama a kusa da Nenehn ya na kallon Liyana da ta kasa ďago idanunta ta kalli ko wannensu.

Ganin ta yi hanyar ďakinta na gidan Nenehn ne ya sanya sa ďago kansa tare da ďan kallon Nenehn.

“ Nifa yarinyar nan yanzu tsoro take bani, ooh ni Ajiddeh.” Ta ḳarashe maganar ta na ďan kakkab’e rigarta.

“ Neneh daman abin da ya kawo mu yau ďin ranar litinin zamu bar ḳasar soo a saka mu a addua dan Allah.” Ya yi maganar ya na ďan wasa da mayafin Nenehn.

“Idan ka yi wani abin kamar mai hankali, toh Allah ya tsare bara na zuba maka wani pepe soup ɗin Abaji da nayi.” Ta yi maganar tare da fara ḳoḳarin tashi.

“Nooo Neneh bar shi yanzu haka muna kan hanya ne zamu je gidan Mami Sannan mu biya gidan Ammi.” Ya yi maganar ya na mai kallon diamond wristwatch ɗin dake hannunsa.

Sannan ya ḳara da faɗin “ Neneh ki ce ta same ni a waje.”

“ Kai malam shiga ka tafi da ita, haka kawai na yi ta zabura cikin dare , wallahi ko bacci take kinkimarta ka tafi da ita, hanyar lafiya a bita da shekara.” Ta yi maganar ta na mai pointing ḳofar ɗakin Liyanar.

Cikin takunsa na isa ya ḳaraso har cikin ɗakinta tare da kullo ḳofar.

Zaune take a kan gadon ta jinginar da bayanta a fuskar gadon hannunta na rungume da pillow.

Ḳarasa shigowa ya yi a hankali tare da ḳarasowa inda take zaune ya na mai tallab’o fuskarta.

“What’s it for ?, mai sa kike saka kanki a damuwa bayan kin san mai ciki baya shiga kalar yanayin da kike ḳoḳarin tursasawa kanki shigarsa?.” Ya yi maganar ya na mai shafa kanta.

“ Yaya Aliih .” Ta faďa a sanyaye.

“ Naam.”

“Did you love me.?” Ta yi maganar ta na kallon fuskarsa.

Shiru ya yi yana kokwanton amsar da zai ba ta sannan a hankali ta ķara faďin “Is a Noo right, Marwa kake so, since she’s the best ta na baka kanta a duk lokacin da kaso right.?” Ta ķarasa hawaye na fita a idanunta.

“Listen Liyana, ina son ki tun da har na kawo yanzu ina tare dake har affairs ya shiga tsakaninmu, just know one thing, son ki yanzu na fara kuma babu ranar dainawa, idan ki na tunanin bana ma sonki toh ki sauke wannan IOS version ďinnan a ķwaķwalwarki Okay, soo are we good to go.” Ya ķarashe maganar tare da ďage girarsa ďaya.

Gyaďa kanta ta yi sannan kuma a hankali ta maida himar ďinta ta kamo hannunsa suka fito daga cikin ďakin.

“Daga can a yi can.” In ji cewar Neneh dake zaune ta na shan apple.

“ Daďinta gidan kakana na zo ba gidan ki ba, idan wani ya isa yaje gidan kakanninsa mana.” Liya ta faďa tare da murkuďa bakinta.

“Wannan kuma da Mijinki kike, yaje Ibadan mana idan ya isa.”

“wannan kuma Ke ta shafa.”

“Ku dai wallahi iyayen butulci ne, da ba dan ni ba ta isa ta yi cikin jikinta ne.”

“ Allah ne ya ḳaddara ai ta dalilinki zaa yi auren amma mun daďe da sanin juna.” Liyana ta faďa tare da ficewa daga ďakin.

“Mtwww ja ‘ira, Allah ya tsare min ku .”

Ko da suka fita ma gidan Mami suka shiga, gidan na nan tsaf tsaf kamar kullum.

Hannunsa cikin na ta suka nufi part ďin Mami because a gidan Neneh ya bar car dinsa.

Mami na zaune cikin wani dakakken super holland da ya yi mata kyau sosai cikin dinkin wani A shape gown mai kyaun gaske.

Ta yi farin cikin ganin Liyana sosai dan ji take kamar ta mayar da ita cikinta.

Sai Bayan ḳarfe uku sannan suka fice daga gidan suka biya gidan Neneh tare da ďaukan motarsu sannan suka fice daga gidan.

Gidan Ammi farin cikinta kasa boye sa tayi dan sai da ta cire kunya ta rungume ya’r ta.

Shi ma around 4 suka bar gidan sannan suka wuce hospital aka dan dubata.

Daga nan ma shopping ya kai ta sannan suka dawo gida around eight na dare.

D’akinsa direct ta nufa, dan ko hanyar ďakinta ba ta kalla ba.

A toilet ďinsa ta yi wanka kafin ta fito har ya ďauko mata pyjamas ďin da za ta saka.

A hankali ta zame towel ďin jikinta tare da fara sanya kayan da ya kawo ma ta bayan ta goge jikinta fa shafa manta, ya na zaune akan sofa ya na kallonta har ta gama saka kayan sannan ta yi kwanciyyarta a kan gadon dan already ta Riga ta yi sallah.

Bayan ta kwanta shi ma toilet ya shiga tare da yin wankan ya fito sannan ya fara ḳoḳarin saka kayansa.

Wayarsa dake kan bedside drawer ce ta fara ring, har ya tawo zai ďauka Liyana ta yi saurin ďauka tare da picking ďin video call ďin.

Kyakkyawar matashiyar budurwa ce wacce Ke da nose ring (b’ulan hanci), fara ce sosai ga kumatu ma shaa Allah saboda ta na da jiki.

Kanta sanye da wani hulan bacci bakinta ya sha lipstick mai shegen ḳyalli Wanda ya fidda shape ďin bakinta da color ďinsa na pink sosai.

Kayan baccin jikinta kam is half naked, a ta can b’angaren kallon Liyana Marwa ta yi sannan ta ďaure fuskarta tare da faďin “Ba wa mai wayar wayarsa, I need to talk to him not you.” Ta yi maganar tare da yin ḳwai da chewing gum ďin bakinta.

“Mijina gashi nan a tsaye ya na Jin ki shi ya ba ni wayar ya ce na miki magana, soo mind your business and stay away from my property , ba na son alaḳar ki da mijina, Am i clear.?” Ta yi maganar tare da katse wayar ta juyo ta na mai dallawa Aliyun harara.

Shi ma bai tanka ma ta ba bai kuma amsa wayar da ta tusa shi a under pillownta ba, ya yi kwanciyarsa tare da ḳurawa ceiling dǐn dǎkin ido ya na mai kallon chandelier dake saman bedroom dǐn.

Sosai ya yi nisa a tunanin nasa sannan a hankali ya ji mutum ya rungume shi, dǎgo Kansa ya yi tare da kallonta ya ga sun haɗa idanunsu.

Kashe ma sa idanunta dǎya ta yi sannan ta ḳara hugging dǐnsa tsamm jikinta.

Washegari da sassafe tare suka shiga toilet suka yi wanka sannan suka yi alwala.

Sallar ma tare suka yi Sannan ya wuce gym dǐn dake street dǐnsu.

Ita ma sai da ta idda duk wasu addu’oin ta sannan ta nufi kitchen suka fara haďa breakfast da Salimah.

Yau dai kam Fufu take son ci sannan ta saka aka yiwa Aliyu soyayyan chips and plantain da coffee dǐnsa.

Around 7:45 ya shigo gidan as usual da komai nasa na gym.

Tafe take cikin wani mini skirt white color Wanda ya fitar da glowing and elegant skin color dǐnta, kanta fake yake a tsakiya, sai kuma wani crop top black color da ta sanya mai dogon play dǐn hannu, Wanda rabin glowing ḳirjinta suke a waje, ga cikinta da yake a cikin watansa na shida da ya yi wani kalar mugun turowa, Wanda sai wani kalar sheḳi yake.

A hankali ta cigaba da saukowa daga stairs dǐn hannuwanta bibbiyun riḳe da ḳugunta.

Wani kalar kyau ta masa yadda take tafiyar nan da ciki, tuna lokacin da Marwa Ke da ciki ita ma ya yi da komai sai tace ciwo ba kamar na Liyanar ba.

Ḳarasowa ta yi har inda yake tsaye tare da yi masa wani ɗan duka a ciki.

Ba ta jiyo ta kallesa ba ta nufi hanyar dinning tare da fara cin abincinta.

AFTER TWO DAYS.

Yau ne ranar da jirginsu zai wuce Lagos sannan daga Lagos su wuce Saudi.

Sanye take cikin wani black elegant abaya da ya yi mata kyau.

Shi ma ya na sanye cikin wasu Senate dress masu kyau sannan Amir yazo ya kai su Airport.

Ba a wani b’ata time ba jirginsu ya ďaga zuwa Lagos.

Hutun minutes talatin suka ḳara yi sannan jirginsu ya ďaga zuwa Saudi Arabia (Ḳasa mai tsarki).

Gidan wani abokin kasuwancinsa suka sauka da yake nan Saudi, An tarbe su sosai kamar yadda ya dace sannan suka samu wani hotel kusa da masallacin Kaaba suka yi launching.

Satin su ďaya a Saudi, sun yi ibada sosai yadda ya dace sannan suka kama hanya zuwa Switzerland……

Wallahi wannan app din babu dadin rubutu 😭😭😭

Mu hadu gobe wallahi na sha wahala a wannan typing ɗin 😹😭😭😭

THE REGRET ❤

Pending Amarya ce □□

JAJIRTATTU WRITERS ASSOCIATION.

THE NOBLE WRITERS TEAM😘□

page 56□□

Whosoever want your cry shall cry your cry □□ bi iznillah.

This page is dedicated to you Mamii □

Uwata ta gari wadda ta yi sanadin zuwa na duniya □

Allah ya jikan ki ya miki rahama ya sanya mutuwa ta zama hutu na har abada a gare ki □

Today is my birthday □ Allah ka ḳaromin shekaru masu amfani da albarka □

Uwata Allah ya ba ki ladan naḳudar da ba ki ci ribarta ba □

Yours sincerely Autar ki Mamana □

Satin su ďaya a Saudi, sun yi ibaba sosai sannan suka kama hanya zuwa Switzerland □□

Sosai ta ji dadin ḳasar musamman yadda suke tafiyar da rayuwarsu.

Aliyu ji yake kamar ya hadiyeta, ko anan ma sai da suka yi faďa a kan Marwa da take kiransa a waya sai da suka yi kusan kwana uku ba sa magana sannan suka fara magana.

After one week □□□□

Yau friday a yau kuma zasu wuce China tun safe take ta b’ata rai domin ita har ga Allah rayuwar Switzerland ya yi mata daďi barimma yadda take fita da wando yanzu da bai cika takura mata ba saboda cikin jikinta.

Zaune take a kan sofa dĭn wani luxury hotel da suka sauka, jikinta sanye da wani light purple dĭn maxi dress , Wanda ya bi shape dĭn jikinta da cikinta ya bayar da wani kyau a tattare da ita.

Hannunta na riḳe da fresh apple ta na ci, ya shigo cikin wani shigarsa na combat da white shirt da suka amshi jikinsa.

“Ki shirya kayan ki please bana son magana biyu.” Ya faďa tare da kwashe wasu Kayan amfaninsu da yake ďakin.

Ko kallonsa ba ta yi ba ta ci gaba da ďaukan glass cup ďin hannunta hoto.

“Drop it, kije ki shirya, idan kika je China ba za ki so dawowa Nigeria ba.” Ya yi maganar tare da ajiye wani jeans trouser na _Calvin Klein_ da rigar D&G plane shirt.

Ba ta tanka sa ba kawai ta hau cire kayanta tare da fara nufar cloth set ďin ďakin.

Saurin ďauke kansa ya yi daga inda take sannan ya cigaba da zab’an kayansa.

Ba ta kulasa ba ita ma ta fara ḳoḳarin shiryawa cikin wasu designers palazzo trousers da wani wide t shirts da ya mata kyau sosai, sannan ta yi rolling mayafinta tare da saka wani heels masu kyaun gaske black color dake kayan na ta fari ne.

Cikin mintuna da ba zasu gaza talatin ba suka gama shiryawa sannan suka kama hanyar waje hannunsa riḳe da trollies sannan suka nufi reception ya bada key ďin ďakinsu suka wuce.

Taxi driver ya tara sannan ya faďa masa inda zasu je.

Tun da tsakanin inda suke da Zurich airport babu wani nisa cikin 20 minutes suka iso airport dĭn basu wani jima ba kuma jirginsu ya ďaga zuwa Beijing.

AFTER TEN HOURS □□□□□

Hours goma suka yi a hanya sannan suka ḳaraso Beijing airport.

Drivernsa ne ya zo ďaukan su basu wani jima a hanya ba suka ḳaraso Shunyi district nan main apartment dĭn Aliyun.

Yanayin tsarin gidan sosai ya burgeta, babu hayaniya amma sai kyau na haḳiḳa, komai na wajen looks luxurious.

Paint na gidan fari ne tal, babu ko alamun tabo, ga unguwar wani kalar shiru babu hayaniya sai dogayen gine - gine masu ban mamaki da shaawa.

A parking lots a ka yi parking motar sannan gabaďayansu suka fito daga bayan motar.

Jikinta is very weak ba ta wani kalli gidan sosai ba tabi inda ya bi kawai, drivernsa na tafe da trolly ďinsu gabaďaya.

Is a Very big and huge living room da ya gaji da haďuwa da kayan zamani wanda yaci uwar na Nigeria.

Shi ma falon kallo ďaya ta masa ta ci gaba da bin bayansa dan Allah ya gani har yanzu fushin da take da shi tun a Zurïch bai gushe ba a zuciyarta.

A hankali take taka stairs ďin har ta ḳaraso ďakin da yake saka password domin buďewa.

Ḳarasa buďe ḳofar ďakin ya yi tare da yin sallama ya shige, binsa ta yi a baya ita ma bakinta ďauke da sallama, ďakin ya ďan yi ḳura sosai, hakan ya sanya shi ajiye trolling da ya amsa a hannun driver bayan shigowarsu, ya hau fara gyaran ďakin.

Liyana na tsaye ta na kallon ikon Allah har ya gama gyara gadon ya ďauko sweeper da mopper ya fara gyara ḳasan.

Neman kujera ta yi ta zauna tare da miḳar da ḳafarta ta na shafa cikinta da yake a watanshi na bakwai.

Sai da ya gama gyara ďakin tsaf sannan ya shige toilet shi ma ya wanke, tare da haďa wani ruwa mai zafi a cikin bathtub.

Ko da ya fito har bacci ya kwasheta, sai da ya ďan ma ta kallon some seconds sannan ya hau fara tashinta.

Kamar ta mare shi haka ta ďinga ji, jiki babu ḳwari ta nufi toilet ďin tare da fara wankan kamar yadda ta ga ya haďa mata ruwan.

Sosai taji dadin ruwan da ya haďa mata hakan ya sanya ta jin daďin jikinta sosai.

Ko da ta fito ma har ya ajiye mata kayan da zata sanya ajikinta domin ta huta dan time dĩn da suka ḳaraso dare bai yi ba anan dĩn.

Bayan ta shirya dĩn ma wani kalar yunwa Ke nuḳurḳusan cikinta, ganin baya ďakin ne ya sanyata samun waje ta zauna ba tare da ta damu da inda yaje dĩn ba.

Cikin minutes ashirin ya ḳaraso cikin ďakin hannunsa riḳe da wani wood tray mai kyau, ḳarasowa yayi har kan gadon da take zaune ya ajiye mata pepe soup dĩn catfish tare da wani salty bread sannan ya juya ya nufi toilet dĩn ďakin.

><><><><><><><><><><><>

Tun bayan tafiyarsu Aliyu Neneh ta dage da addu’oi wanda sai da ḳyar ta sama wa kanta salama shi ma sai da Jiddah ya tsawatar mata.

Tun a lokacin da ta san waya’nda suka yi mummunar aikin ga Liyanar ta saka ranar family meeting a platform dĩnsu na family.

><><><><••••••••••••><><><><>

Mama Fatuh kam tun bayan barinsu Nigeria, Sam bata dawo dai-dai jikinta ba, dan ita kawai Liyana take hangowa acikin idanunta, ta na mamakin kalar kishin da take ma Ikimat dĩn yadda a koda yaushe yake rinjayar soyayyar da take ma ḳanwartata.

Ita da Rufaidaht are friends for almost 30years, tare suka yi yarinta, then Nabil Babban ďa namiji ne a kaff familynsu.

Ita tun da ta b’ude idanunta take tsanin son Nabil, sai ta wa yi gari ta ga ḳanwarta ta aure shi, ḳanwar ma ýar stepmom dĩnta.

Wannan shi ne dalilin tsanar dake tsakanin ta da ḳanwarta Wanda bayan Rufaidaht babu Wanda ya san da zancen nan, da ma yadda suka tara kuďi har dubu ďaya a lokacin suka kai ma principal dĩnsu Ikimat ya yi raping dĩnta, da yadda suka yi ta wura wuta a tsakanin Ikimat da Nabil dĩn yake wulaḳanta ta.

Ita Sam tun da ta ji Neneh ta ce akwai family meeting next week hankalinta ya kasa kwantawa, ta san Neneh idan ta yi find out komai zai faru ne, gashi Mama Lantana ba ta nan, ita kuma Mama Maimu ba mai surutu bace a wajen taron dangi.

Tsaff ta san halin Jiddah idan ya yanke hukunci kuma wallahi nata ya ḳare ne kawai.

D’umin da taji a kumatunta ya sanyata kallon Yusrah da take danna waya a kusa da ita amma ta bata baya.

Wani kalar ajiyar zuciya ta sauke sannan ta gyara kwanciyyarta ta na mai roḳon gafara a cikin zuciyarta, domin har ga Allah she’s REGRETTING for all her evil deeds.

••••••••••••••••••••••

Hajiya Rufy kuwa ko ina ya mata zafi ga rashin haihuwa ga kuma wani ɗan iskan rashin girls ɗinta da yake damunta, ga rashin samun kulawar Nabil yadda ya dace.

Yau ma kamar kullum bayan sun gama lunch mukullin motarta ta ɗauka ko kallon Nabil da Ikimat dake falon ba tayi ba ta yi ficewarta a falon.

Parking space ta nufa tare da ďaukan motar da Nabil ya bar mata ta fice daga harabar gidan.

Bata zarce ko ina ba sai Dan dishe layin gidan boka barbushe, ko da ta isa gidan a kulle yake babu kowa sai ḳofar shagonsa dake a b’ude babu ko labule, yara na wasan ḳasa a cikinsa.

Da ďan alamun mamaki a tattare da ita ta ḳaraso cikin shagon tare da kallon leader ďin wasan da ta ďan fisu wayo tare da faďin “Ya’r Baby mai ya faru da malam ďin na gan ku a shagonsa kuna wasa haka?.” Rufaidaht ta yi maganar tare da ďan duḳawa.

D’ago kanta yarinyar dake sanye da wani fading ankara ta yi fuskarta duk ḳasa, sannan a hankali cikin muryar yarinta ta ce “Ai Babanmu ya koma niḳa a injin ďin mai wando na bayan layi.” Ta yi maganar tare da amsan gwagwanin maltina a hannun ḳanwarta ta shiga yanka sa domin hada kasko a wasan nasu.

Sai da ta ďan yi shock na wasu daḳiḳu sannnan a hankali ta ce “ Toh Baby ko za ki iya kai ni wajen nasa?.” Ta faďa kamar za ta yi kuka.

Tashi yarinyar ta yi tare da kakkab’e hannunta a kan rigarta tare da kallon ḳaramar ḳanwarta tare da faďin “Ke Sajida kafin na dawo ki gama tuḳa tuwon sannan ki ďebo dusa a wajen Iya ki fara haďa miyar kafin su Umma su dawo su tashi mu daga wasan.” Ta na faďin haka ta fara tafiya Rufy na biye da ita.

Tafiyar minti biyar ne ya kawo su wajen Malam barbushe, da Ke sanye da wani ḳaton riga kalar na Sudanese, jikinsa da fuskarsa duk gari ya b’ata shi.

“Yawwa ga wajen Baban can.” Yarinyar ta faďa tare da nunawa Rufaidaht wani langa-langa, sannan ta juya ta koma inda ta fito.

A hankali ta ḳarasa har wajen da yarinyar ta nuna mata ya na tsaye ya na ḳoḳarin tada injin dǐn, ta shigo wajen da duk ḳurar garin tuwo ya babbaďe ko ina.

“Dan ubanki yadda kika shigo ki koma jiḳar iblis.” Ya yi maganar idanunsa a rufe.

Babu yabo babu fallasa ta ďauki Alynerh tare da miķawa Marwar.

Goya ta tayi ita ma da abin goyon sannan suka fice daga gidan ba tare da kowannensu ya ďauki Abu makamancin trolly ba.

Direct Airport suka nufa ba su wani jima ba suka shige private jet ďin Abbhu Wanda bai koma Nigeria ba.

AFTER SEVEN HOURS

KARFE uku na rana jet dĩnsu ya dira a Aminu Kano babban filin jirgin da ke birnin jihar mu ta dabo.

Amir na tsaye ya na jiransu a jikin motar sa ḳirar Tesla model S black color.

Idanunsa na kan jet din da ya dira a wajen, cikin minutes ḳalilan suka fito daga cikin jet dǐn, shi ne a gaba sai Liya da kuma Marwa dake last dǐn fitowa, he was very surprised da ganin jarirai a hannunsu. Amma da ya tuno da Liyana da ciki ta bar ḳasar sam sai ya cire mamakin hakan daga zuciyarsa.

Hydar ne ya ḳaraso wajen da yake tare da sakar masa ranḳwashi dan tuntuni yake masa magana amma sam yaḳi basa amsa.

“Oouch Man, kai a rayuwarka idan ba ka yi mugunta ba ba ka Jin dadǐ ne?.”

Amir ya yi maganar tare da ya mutse face dǐnsa.

“Shut up jare, ḳanwata za ka aura you better start to dey practice yadda za ka dǐnga min biyayya if not i will sue you to court.” Hydar ya faďa tare da buďewa Liya bayan motar.

Ita ma Marwa zagayawa ta yi ďayan b’angaren tare da zama a bayan kujerar.

Shi ma Hydar gaban motar ya nufa sannan direct suka ďauki hanyar gidan Neneh.

To their surprise sai suka tarar da gidan a cike sosai da family cars na Maiduguri.

“Malam dallah wa yace ka kawo mu gidan nan, kai mu gidanmu mai son ganinmu ya zo ya same mu.”

Hydar ya faďa a fusace.

“Wa fushinka zai bawa tsoro?, sai dai matar taka dai.” Amir ya faďa tare da zare mukullin motar.

“Bani pink jet ďina dallah idan ya so kayi ta soki burutsunka, ďan rainin hankali kawai.” in ji cewar Amir ďin tare da amsar Aida daga hannunsa.

Tsaki Hydar ya ja ya na mai faďin “ Ai na zaci ba ka gan su ba ko makantar naka ya motsa.”

Amir bai tanka masa ba ya shige cikin living room dïn Nenehn da ake ta rairai waḳoḳi na larabawa.

A hankali suka shiga takawa ita da Marwa har suka shigo cikin falon gidan inda ya haďa mutane da yawa cikinsu har da Abbhu da Abbhi da Ammi da Mami da ma su Rashanda da Umma Mansura.

Ily na zaune daga can wani corner ta na chatting.

Gidan gaba ďaya ya hargitse saboda murnan ganin jarirai har uku.

Aliyu kam tun da ya ga ba ta shi ake ba ya tattara shi da Amir suka wuce can garden ďin gidan Mami.

Ganin ita ma babu mai bi ta kanta ne ya sanyata shigewa ďakinta tare da fara rage kayan jikinta. Wanka ta yi sannan ta sanya kayan Ily a jikinta.

“Yaya Liya ba ki da kirki wallahi tun da kika zo nake ta miki magana ko kula ni kin ḳi yi.” Ily da shigowarta kenan ta faďa tare da zama a kan kujerar dake ďakin nata.

Shiru Liyana ta mata tare da ci gaba da abin da take yi.

“Liya magana fa nake mik…” ba ta ḳarasa ba Liya ta sauke ta da wasu maruka zafafa guda uku.

Sannan ta cigaba da rayuwarta.

“Mai na miki.?” Ily ta faďa tare da dafe ḳuncinta ḳwalla na zuba a idanunta.

“Ni za ki ciwa amana Ily?, yanzu Sultan za ki aura?, mai yasa za ki min haka, ni ba ma wannan ba, saboda ni maḳiyar ki ce har ni za ki b’oyewa aurenki sai a wajensu Rashidat nake Jin maganar aurenki, yanzu da ban auri yayansa ba, da ci min amana za ku ďin ga yi ta bayan idona kenan, toh na gode.” Liya ta faďa tare da share ḳwallarta.

“Wannan Wace kaliyar magana kike yi haka Yaya, yanzu na fasa aurensa kike nufi?, miye aibunsa?.”

Ily ta faďa a sanyaye.

A fusace Liya ta ďago kanta da niyar ba ta amsa amma ido huďun da ta yi da Aliyu ya sanyata saurin haďiye zancan da yake bakinta.

Cikin takunsa na ḳasaita ya tako har inda suke tsaye tare da faďin “ Which Sultan are you talking about?.” Ya faďa da kakkausar murya.

“Magana muke a kan bikin Ilham Ya Aliih.” Liya ta faďa tare da yin murmushin yaḳe.

“Ba next week bane ba auren?, ai next tomorrow za a fara events na ji kamar Ana faďa.”

“Yeah, that’s what we’re discussing.” Ily ta faďa da sauri.

“Okay, keep it up.” daga haka ya fice daga gidan.

Ya na fita Neneh ta shigo.

“Ilham sai kuma kika ji labarin jikar Bob Marley , ḳanwar Naira Marley ta haifi ya’n uku ko?.” Nenehn ta faďa tare da fara shafa wa Ily wani ruwan turare a jiki.

“Babu ruwana Neneh.”

“Toh wake tsoron ta mutu balle ta yi rai, gobe za a kawo lefenki da safe, zan aurar da ýar gata ba ayawo ba.” Neneh ta faďa tare da tab’e bakinta.

“Wallahi Neneh idan kika b’ata min rai za ki ga rashin mutumcin da zan miki, ba sanyi nayi ba, wallahi gwara ki tattala tsufanki ko na maida Abbhina da Umma Mansura marayun dole, soo respect yourself.” Ta na faďan haka ta fice daga ďakin.

Ko da ta fita su Rashidat da Reedah na ta ďawainiyya da jariran dan Unaisah sai gobe za ta zo.

Zama tayi acikinsu ta na hira, ganin tara saura 15 minutes ya sanyata sanya slippers ďinta tare da ďaukan wayarta domin zuwa garden dan wannan lokaci ne da iska mai ďadi ke fita a garden ďin.

Tsaye suke a jikin bushiyar wani Guava, hannunsa ďaya na dafe da trunk ďin bushiyar.

ba ta wayi su waye su ba sai da taji muryar Marwa na faďin “Ya Alih ni mutuwata ita ce kaďai ma fi alheri agareni, idan nace zan yi auren wallahi bani da mutumci a idon Wanda zai aureni.” Ta faďa tare da fashewa da kuka.

“Yanzu Marwa aurenki kike so nayi ko mai?, kema dai kin san ba na raayin auren mata biyu, kuma na Riga na yiwa Liyana alḳawarin ba zan mata kishiya ba.” Hydar ya yi maganar a sanyaye.

“ No God forbid, ba zan ma shiga farin cikin kowa ba.” Ta ḳarashe maganar tare da goge hawayenta.

Jin an dafa kafaďarsa ne ya sanya sa juyowa a ďan firgice.

“Marwa has gone through alot, Allah ya maka arziḳi daidai gwargwado, wanda zaka iya tufatar da mata ma fiye da ďari, and ni na ya’r je maka da ka aureta In dai har za ta zauna lafiya da ni, bani da matsala, ni dai Kar ta shiga sabgata shi ne matsalata, wuce ka taho mu tafi.” Ta faďa a ďan tsiwace tare da jan hannunsa suka bar Marwar a tsaye.

“Uban mai ya kai ka wajenta.” Ta faďa a faďace Bayan sun bar wajen.

“Malama respect yourself uwa kike yanzu, ki ajiye childish behavior din nan naki.” Hydar ya faďa tare da wuceta ya fice daga gidan Nenehn gaba ďaya.

Tsaki taja tare da shigewa gidan Nenehn da ta tarar da Alya na ta tsala kuka.

Sai da ta dallah ma yarinyar harara sannan ta fara ba ta nonon.

Bayan ta gama ma dakinta ta shige tare da kwanciyyarta.

Har ta fara bacci ta ji ana kai hannu kan kumatunta.

A hankali ta dago da kanta tare da ḳafe manyan idanunta akan kyakkyawan fuskar mahaifinta.

“Woooh Abbhi!.” Ta faďa a ďan tsorace tare da tashi ta na mai jinginar da bayanta ajikin fuskar gadon.

“Babyn Abbhi kin manta da Abbhi right?.” Ya faďa tare da zama a kusa da ita, haďe da janyota jikinsa.

“Noo,ta ya zan manta da soyayyata, I missed you Abbhi.” Ta faďa tare da marairaice idanunta ta na mai ķara manna jikinta a jikinsa kamar mage.

“Abbhina alot has happened da bana nan ko?, wait gist me! Gist me.” Ta ķarashe maganar tare da gyara zamanta sosai a jikinsa.

Shafa kanta ya fara yi a hankali sannan ya ce “Noo, Ke ki fara bani labari akan honeymoon dinki then sai na baki nawa.”

“Promise?.”

“I never failed you, you know?.”

“Yeah, haka nè Abbhi, first mun je Zurich the place was very nice, sannan muka biya China then that his stupid Cousin ruined everything.”

Ta ḳarashe maganar kamar za ta yi kuka.

“Mai ta yi ?.”

“Abubuwa da yawa wallahi Abbhi, ex dinsa ce kuma har yau wai yana sonta, Abbhi na bar sa ya aureta a daura auren da na Ily ko kar na amince?.”

“That wasn’t our agreement tsakaninmu da iyayensa kafin muka bashi ke, idan Banda mamanki waye mai kishiya a Family ɗinmu?, ko kin taba ganin na siya miki Abu kala daya dake da Maimunatou?, sooo duk wani Abu da zaa ce ku biyu da wata ke da shi I dislike it dan haka babu zancen wata kishiya.” Abbhi ya fada tare kokarin tashi daga dakin.

“Buh Abbhi.”

Tare numfashinta Abbhin ya yi da faɗin “ kar na sake Jin kalar wannan maganar a bakin ki, is that clear?.”

“ Okay Abbhi.”

Fita ya yi daga dakin ita ma ta koma ta kwanta tare da kunna datar wayarta dan yaran na wajen Ammi da Neneh.

Wani message nè ya shigo anyi save number da “My Favorite Headache □ □😒□□.”

Bude message dïn ta yi ta fara karantawa a hankali “Ke ma kin san an wuce time din da zan yi sa in sa dake, come outside naga wannan kyakkyawar fuskar naki mai cike farinciki, and wear something sexy we’re going out.”

Murmushi ta yi mai kyau sannan ta masa rply da fadïn “A Ina zan bar yaran😒.”

“Mai ye amfani wannan fitinanniyyar tsohuwar.?”

“Watch your tongue she’s my Grandma 😒.”

“Sooo what , malama ki fito I’m starving.”

“Na taho maka da abinci nè😊?.”

“yunwanki nake ji ai ba na abinci ba, just hurry up before i kick the bucket.”

“Ina off abi you don forget say i born pikin.”😊

“Come out jare kullum a nan kika fi ḳwarin pidgin make I no change am for you ooooo.”

Emoji din dariya kawai ta tura masa sannan ta tashi ta ḳara shiga wanka tare da canza pad da kuma wasu abubuwan.

Wani lingerie dress ta saka tare da ďora wani dogon himar a kai, dan har yanzu kwai kayanta a gidan Neneh, sannan ta fito daga cikin falon da ya rage daga Ammi sai Neneh da wasu danginsu na Maiduguri.

“Ke Sirikar Kyari Ina za ki da daren Allah, yayin da halittun Allah ke bacci.” In ji cewar Neneh dake riḳe da Aida.

“Ina ruwanki wai da ni?.” Ta faďa tare da murguda mata baki sannan ta fara kokarin tafiya a hankali.

“Ba da ke ake bane?.”

Ammi ta faďa a zafafe

“Ke ko da ki bar tijararriyyar ta ci gaba da abin da ta saba.” Neneh ta faďa tare da cuno baki.

Sai da ta harari Neneh sannan ta ce “Daman Ammi Papan yaran nan nè zan kaiwa saḳo.” Ta yi maganar a sanyaye.

“Ahhh, kaji sabon kwartanci, toh aikam babu inda za ki, ya latsi bulus na shekaran jiya da na jiya ya jira kuma sai kin yi arba’in.” Neneh ta faďa tare dallawa Liya Harara.

“Na miki maganane?.” Inji cewa Liya.

“Malama wuce ki shige ciki.” Ammi ta faɗa tare da amsan abin da wata cousin dinta ke mika mata…..

Ga update din yau 😂😊

The Regret ❤

Not Edited □□

Pending Amarya ce ❤

https://whatsapp.com/channel/0029VbAyucH7j6g0IDCpPi2V

Faridatool Noor □

JAW □

Surah Al-Hadid (57:4)

“And He is with you wherever you are.”

Let’s Dive in

Bismillahir Rahmanir Rahim ❤

Pending amarya 63.....

“Ke ko da ki bar tijararriyyar ta ci gaba da abin da ta saba.” Neneh ta faďa tare da cuno baki.

Sai da ta harari Neneh sannan ta ce “Daman Ammi Papan yaran nan nè zan kaiwa saḳo.” Ta yi maganar a sanyaye.

“Ahhh, kaji sabon kwartanci, toh aikam babu inda za ki ya latsi bulus na shekaran jiya da na jiya ya jira kuma sai kin yi arba’in.” Neneh ta faďa tare dallawa Liya Harara.

“Na miki maganane?.” Inji cewar Liya.

“Malama wuce ki shige ciki.” Ammi ta faďa tare da amsan abin da wata cousin dinta ke mika mata.

Kamar ta rushe da kuka, jiki a sub’ule ta wuce ta shiga ďakinsu ba dan ranta ya so ba.

ko da ta shiga ďakin wayarta kawai ta ďauka ta tura masa saḳon ba za ta samu damar fitowa ba.

Cikin seconds 30 ta ga reply dinsa.

“Dama na san za’a rina, an gama komai kema gobe zaa kawo naki lefen na sunan Yaran nan, and I need to discuss something important with you, Please.”

Murmushi ta yi sosai sannan ta masa reply da “Ba Lallai fa na fito ba yanzu, ance ba zaka kara ganina ba sai nan da 40 days 😂□□.”

“Which 40 days you’re kidding me right?.”

“Wallahi I’m serious, toh mai kake son fada min let’s discuss anan din.”

“Wallahi Fatima maganar nan ba na waya bane, ki san yadda za ki yi ki fito.”

“They won’t let me out manaaaa 😫😂□□.”

“Ta ya kike fita before?.”

“Ta sanadin Abbhina mana 😑.”

“Then Ina mijinki I command you ki fito ko ranki ya bace ko ta sanadin waye.”

“ka ji ḳarfin hali kuma□.”

Ganin har an yi minti biyar da tura masa message dǐn ḳarshen bai mata rply bane ya sanyata maida hijab dǐnta ta na mai tunanin hanyar da zata fita.

Ta na cikin wannan tunanin su Ilham suka shigo hannunsu riḳe da ledoji na kayan maḳulashe.

“Yaya kin ga na siyo miki favorite drink dǐnki.” Ily ta faďa hoping yayarta za ta mata magana.

“Wai wannan kuma mai aka mata take ta hawa kamar yeast daga ganin mutane kuma sai ki wani ďaure fuska?.” In ji cewar Reedah dake cire earrings dǐnta a bakin madubi.

“Bari mu gayyato ma ta Yusrah ta ďan ci mata mutumci za ta dawo daidai.” Rashanda ta faďa tare da kyalkyalcewa da dariya.

“Wannnan kuma matsalar ku ce, wani ya fada min ya zan fita daga gidan nan na sami Hydar abeg.” Liyana ta faďa a sanyaye.

“Eleven fa ta yi mai zaku yi?.” In ji cewar Reedah.

“Ka ji ya’r iska?, Ina ruwanki da abin da zamu yi?.” Liya ta faďa a fusace.

“Allah ya baki hakuri, ku taho mu fita a sace I think babu Wanda zai gane ki a cikinmu.” Reedah ta fada tare da gyara zaman gyalenta da bata cire ba.

Daga haka su duka hudun suka fice daga ɗakin, sun ci saa kam domin babu kowa a living room ɗin.

Komawa suka yi gaba ɗayansu suka barta ita ta ɓarasa fita daga falon.

karo ta kusan ci da shi, dan har ya gaji da jiranta ya nufo cikin gidan da kansa.

Da sauri ya fizgota jikinsa tare da nufar garden din gidan da ita.

Kujerun dake wajen na hutawa ya nufa da ita tare da zama kanta a kan kafaďarsa.

“Ya Alih.”

“What’s wrong?.”

“Ka ce zamu yi magana, kuma kayi shiru, bacci nake ji.” Ta yi maganar a hankali dan haka kawai zuciyarta Ke dukan uku uku.

janyeta ya yi daga jikinsa, Sannan ya karkato da ita suna masu fuskantar junansu.

“Fatima.” Ya kirata da kakkausar murya

“Naam.” Ta amsa a sanyaye tare da ɗago kanta.

“Fatimah Kar kiyi tunanin na ci zarafin ki ko kuma wani abu da zai sanya ki Jin kaman ba kiyi min yadda ya dace ba, let me go straight to the point, please Fatima ki amince na auri Marwa dan saboda future ɗinsu Alynerh, yanzu abubuwa da dama na judging dina akan wannan abun da muka aikata cikin rashin sani.” Ya yi maganar tare ɗurḳusawa a kan gwiwowinsa.

“You called it rashin sani, in dai addinin da nake yi kake yi na tabbatar da cewa tun da ka shiga 10 to 15 years ka san hukuncin Zina da kuma haramtata da akayi, toh daman tun da can ba sona kake ba, go on, marry her idan hakan ne zai sanya ka farinciki.” Ta ḳarashe maganar hawaye na zuba a idanunta.

“Wallahi Ke nake so a yanzu, I’ve feelings for her buh naki ya danne.” Ya faďa tare da matso da fuskarsa gabb da nata.

“Oh really, by the time da zaka haďa jiki da ita kuma nata zai danne nawa ko?, Aliyyu kayi duk abin da ya dace, lokacinka ne, sai yadda kayi da shi.” Ta faďa tare da ḳoḳarin tashi daga wajan.

Jawo ta ya yi tare da ḳoḳarin haďe bakinsu waje ďaya, wani fitila mai hasken gaske ne ya dallo su wanda hakan ya sanya shi saurin hankaďeta tare da tashi dan ya san ba zai wuce Neneh ba ce.

“Aahhh lallai, yanzu har nan kuke iskancin naku kenan?, dole gobe Usama ya samo min masu welder su samin ḳofa a wajen nan.” Ta ḳarashe maganar tare da ḳara dalle fuskokinsu da fitilar.

“Daďinta dai auren sunnah ne a tsakaninmu.” Aliyu ya faďa tare da bin ta kusa da ita ya na kokarin wuceta.

Sai da ta sakar masa duka a baya sannan ya wuce ya na dalleta da harara duk da duhun dake wajen.

“Uhhhmm, Karina uwar soyayya kya shiga ciki kiyi wa Salamatu bayani, dan ni dai kalar wannan da safe ake yin sa.”

“Ko da rana ake yi mai ruwanki?, sa ido.”

“Borin kunya ne kuma wannan, ki shigo ciki shine magana.” Neneh na faɗin haka ta bar wajen.

Sai da ta raka Nenehn da harara sannan ta tattare hijab dinta, ta nufi building din gidan.

Ammi na falo a tsaye ana ta fadin ina Liyana ta shiga saboda yaran ke ta kuka, an tambayi su Rashida suma sun ce basu ganta ba.

“Ai sai da na bincikota, ta na can ta bajesu Lantana da Talatu a barbaje, toh ni dai Allah shi kyauta ace yarinya bata Jin magana, ta girma bata san ta girma ba, a zamaninmu idan muka haihu sai mu kusan shafe shekaru biyar ba mu ga mijinmu ba, kuma mu zauna lafiya.” Nenehn ta fada tare da yin upstairs dinta.

Hawaye na zuba a idanunta ta karasa shigowa cikin gidan da Ammi Ke tsaye da Alynerh a hannu ta na jiran shigowarta.

“Wai Fatimah mai sa ba kya Jin magana ne a rayuwarki, yaran da suke naki ba na riḳo ba ki basu Nono sai ya zama bala’i?.” Ammi ta yi maganar ta na mai nunawa Liyanar fushinta.

“Ammmiiiiii.” Ta yi maganar cikin damuwa da muryarta dake a sanyaye alamun kuka take yi.

Saurin ďago kanta Ammi ta yi tare da kallon Liya da hawaye ke ta zarya a idanunta.

“Ya’r Abbhinta, what’s wrong with you?.” Ammi ta faɗa tare da miḳawa Ily Alynerh.

Faduwa ta kusa yi hakan ya sanya Ammi saurin tallab’o ta tare da zaunar da ita a kusa da ita.

A take su Rash suka fiffito.

“Ammi kishiyya zai min, Amminah ki taimaka min Wallahi Ina son sa.” Ta yi maganar muryarta a dishe.

Wani kalar tsawa da Ammi ta daka mata shi ya sanya ta yin shiru tare da hadi̓ye hawayen da ba ta yi niyar hadiye shi ba.

“A kan kishiya kike wannan kukan kamar ba mace ba?, maza ki goge hawayen ki kiyi salatul istikhara Allah ya sa hakan nè mafi alheri, wacece zai aura.”

Fashewa ta yi da kuka tare da fadi̓n “Cousin dinsa ḳanwar Amir.”

“Toh ki ajiye damuwar nan naki ki fuskanci abin da zai fishe ki, ba za ki yi koyi da haḳurina ba Liyana?, Ni da na zauna da kishiya mutuwa nayi?.” Bata yiwa Ammi magana ba kawai ta tashi da gudu tare da shigewa dakinta na gidan Nenehn ta ḳara fashewa da kuka.

A ranar dai yaranta sai madara aka basu.

Tun da ya koma gidan Mami yake kiran wayarta amma ba ta picking haka kawai ya hakura tare da kiran Marwa suka ɗan fara tab’a hira sama-sama.

Washegarin ranar da sassafe ta tashi tare da yin wanka ta saka wani atamfa mai kyau Wanda ya amshi jikinta.

Around 12 na rana ta ɗauki jariran uku tare da niyar daukansu ta nufi gidan Mami dasu.

Classy Reedah ce ta shigo ɗakin tare da kallonta sannan ta ce “Ina za ki je Mrs. Kyari?.” “Gidan Mami.” Liyana ta bawa Reedah amsa a takaice.

“Can I come along?.”

“Why not sai ki riḳe min ɗaya.”

Daga haka ita ma Reedah ta dauki backpack ɗin da ɗaya daga cikin yaran suke ciki.

ihun su Ily da Rash Ke ta shi hakan ya sanya su zuwa falon da sauri.

Unaisah ce ta shigo cikin shigar wani classy abaya hannunta rike da trollynta.

Waro idanunta Unaisah ta yi tare da cire glasses ɗinta ta ce “Mrs Kyari.”

Ita ma Liyana Wani kalar murna ta yi tare da faɗin “Yes Mrs Khaleepha to be.” A yangance suka bawa junansu side hugs, sai da ta kalli yaran sannan ita da Reedah suka wuce.

Gidan shiru yake, amma kallo daya za ka masa ka Wanda cewa an ḳara masa sabon paint, da wasu abubuwan.

A hankali Liyanar ta shiga building din Mamin da shi nè a tsakiya, sai na Aliyu a bangaren dama da yake sharing da Sultan sai kuma side din Abbhu.

Babu kowa a falon sai yan aiki dake ta gyaran falon duk da a gyare yake tsaff.

Neman ďaya daga cikin kujerun falon suka yi suka zauna tare da rugume biyu daga cikin yaranta, ita kuma Reedah ta riḳe kyakkyawar cikinsu Alya, dan ita kamnaninta da dan banbanci da na sauran.

“Hajiya, welcome Big Hajiya dey sleep she neva wake up.” In ji cewar Agnes da hannunta Ke riḳe da towel da glass cleaner.

Kallonta kawai Liyana ta yi sannan ta ďoke kanta ta ci gaba da kallon ya’r hannunta.

“Wooh, Matar Yaya, Awwn Ma shaa Allah, finally her Liyanar Yaya.” Assultanah ta faďa tare da fara saukowa daga benen a hankali ita da wasu counsins dinta.

“Which kind Liyanar Yaya, Liyanar Abbhinta dai.” Ta yi maganar a sanyaye, dan haka kawai kowa haushinsa take ji.

“Lemme see the kids, Ma shaa Allah, wallahi kamar Mamanta.” Ta yi maganar tare da amsan Alya daga hannun Reedah.

Har za ta bawa Assultanah amsa daddaďan ķamshin turarensa dake sanya zuciyarta sanyi a koda yaushe, ya daki hancinta.

Cikin aura ďinsa ya ķaraso har living room ďin, sai da ya ďan saci kallonta Sannan ya dauki kansa tare da nufar dinning area din dake falon.

“Sir wetin you go chop?, Hajiya ta sa an dafa maka favorite food naka.” In ji cewar Agnes dake sanye cikin uniform dinta iya gwiwa.

Sai da ya saci kallon Liyana kaďan sannan ya ce “To my room.” yana faďin haka ya miḳe tare da barin wajen ya nufi hanyar da zai sada shi da part dinsa ta bangaren Mamin.

Da sauri Agnes ta nufi kitchen tare da ďauko tray ta fara haďa duk wasu abubuwan da Hydar din ke so, har za ta wuce Liyanar, sai kuma taji muryarta na faďin “Stop there, thats my job i will do it, je ki karasa cleaning dinki.” Liya ta yi maganar tare da mikawa Sultana da cousins dinta yaran hannunta sannan ta barsu su da Reedah dake ta forming big girl.

Bata tray din Agey ta yi sannan ta cigaba da ayyukan nata.

A hankali take tafiya har ta ḳarasa fita daga cikin living room ɗin bangaren Mami, wani ḳaton compound ne a wajen da yake cike da flowers na ban mamaki, sai wani fitilu dake fita daga cikinsu duk da safiya ne, ḳasan gidan ma shi kansa da epoxy aka yi shi, the building looks rich and elegant, komai na ḳamshin kuɗi a part ɗin dan part dinsa ya fi na Mami kyau duk kyan na Mamin na sa kuwa.

walking slowly ta ḳarasa shiga cikin building ɗin dake cike da haske, da ḳamshin turaruka masu mugun ḳamshi da sanyaya zuciya.

The living room seemed to be the most beautiful and peaceful living room she has ever seen, babu hayaniya komai na falon fari ne tass tun daga bangon har ḳasan falon fari ne tass sai kuma wani rock Persian carpet dake malale a ḳasa.

Furnitures dinma fari ne tass babu alamun datti a wajen, sai wani signature Tv dake tsaye ḳiḳam akan Tv stand. Everything about this living is odogwu babu Wanda aka siya da Naira, rock carpet kaɗai ya ishi ya cire mutane da dama daga talauci ba sai an kai ga sauran accessories da aka narka a falon ba.

Amma still falon ba shi da tarkace saboda abubuwa kalilan aka sanya.

upstairs dĩn da ta gani a falon ne ya sanya ta bin ta ciki tare da wucewa ta fara hawan saman.

D’akuna biyu ne kaďai rak a saman, hakan ya sanyata buďe ḳofar na farko a hankali.

Babu komai a ďakin sai wasu pictures da suke cikin frame da tun na yarintarsa har na yanzu da ya girma.

Tab’e bakinta kawai ta yi sannan ta wuce ta buďe next door dĩn.

Zaune yake a kan cushion dĩn da yake master room dĩn nasa.

Jikinsa na sanye da Kayan da ya shigo da su b’angaren Mamin ɗazu.

A hankali ta tako har inda yake zaune, ɗauke kansa ya yi tare da kallon agogon dake hannunsa, sannan ya fara ḳoḳarin tashi daga kan kujerar.

“Wai mai kake nufi da ni yau da safen nan ne?.” Ta yi maganar a raunane tare da kallon cikin idanunsa.

“Har za ki fassara ni da sanyin safiyar nan da ko karya wa ban yi ba.” Ya faďa tare da komawa ya zauna akan kujerar da karfi.

“Kaga su Alya ba ka musu magana ba, nima na gaishe ka baka amsa min ba, dama da gaske ne idan maza za su ḳara aure sai sun wulaḳanta wadda suka ajiye a gida, toh wallahi ka bini a hankali har yanzu da sauran hauka na.” Ta yi maganar tare da zuwa har inda yake ta na mai dungure ma sa kai.

Janyo hannun na ta ya yi tare da murďesa sannan kuma ya ḳara janyota jikinsa.

Wani kalar ḳara ta saki bai jira ta dire ba ya haďe bakinsu waje ďaya Wanda kamar jira ita ma take ta cafke bakin na sa ta na mai amsan sakonnin sa.

Ganin ya na ḳoḳarin wuce gona da iri ne ya sanyata saurin hankaďesa.

Janyota ya ḳara yi jikinsa tare da sanya kansa akan kafaďarta.

“Idan na wulaḳanta ki tamkar na wulaḳanta yarana ne and kema kin san kalar soyayyar da nake ma yarana, sannan Liya ki ji tsoron Allah da yaushe kika gaishe ni?.” Ya yi maganar tare da mur za yan yatsunta a hankali.

“A cikin zuciyata na gaida ka mana zaka rantse kace baka ji ba?.”

“Allah ya shirye ki, what are you planning game da naming ceremony ɗin yaran nan?.”

“Yar izala ce ni ai bana taro.”

“Na wash, abeg ke da kike Dajjal din kan ki kece kike claiming ɗin ahlul sunnah?, kune ke b’ata mu ashe.” Ya ḳarashe maganar tare da kyalkyalewa da dariya.

“what do you mean?.” Ta faďa a hasale.

“I mean the way you dress, ko Christmas albarka.” Ya yi maganar ya na wani dariyar kuma.

“Waye Christmas kuma?, kowa ai da past life ďinsa babu Wanda bai da tabo, idan kaji na wani ai naka sai dai kace Alhamdulillah, kuma har gobe dole naga wando a clothset dina na saka a…..”

har ga Allah ita maganarta ta yi bata kawo komai a ranta ba.

Da sauri Hydar ya katse ta da faďin “Ya kuma ishe ki motivational speaker.” Ya faďa tare da ďan b’ata ransa.

“Ka tsargu ne?, Nifa magana ta ce ta biyo ta nan, idan ya b’ata maka rai toh a yayyafi juna, a Ina muka kwana a zancan sunan.”

“Get out.”

“Mai na maka?.”

“I said get lost.”

“Allah ya baka haḳuri, zan je lalle a bani kuɗi.”

“Tun da kin bani ajiya sai ki zo ki warta.”

“Ni kuwa na baka ajiya.”

“Ke ya fa ishe ki.”

“Duniya, yanzu ni Aliyu yake cewa ke, Marwa aikin ki na kyau.”

Ko kallonta bai yi ba ta gama tsoki burutsunta sannan ta fice ta koma b’angaren Mamin da har ta fito.

“Mami Ina kwana.” Ta gaida Mamin cikin ladabi da biyayya kalar Wanda ta saba Mamin.

“Daughter nah ashe kina sashen mijin naki, ya kike ya su Umman naki?.”

“Lafiya lau wallahi, Mami, daman su Alya na kawo ki gani.” Ta yi maganar tare da sauke idanunta ḳasa.

“Iyeee, da ba dan su Alya ba ba za ki shigo ki ga Mamin taki ba kenan ko?.” Mamin ta faďa a ďan barkwance.

“Laa, Billah Mami ba haka bane daman can na yi niyyan zuwa tun ranar da muka dawo, toh da yake kuma kina zuwa gidan Nenehn saboda shirye shiryen biki kawai sai na bari sai kin dawo gidan ki steady.” Ta ḳarashe maganar ta na mai ďan wasa da hannunta.

Ta ďan taya Mamin wasu abubuwan, aka ďan nuna mata danginsu Mamin wayanda suka zo bikin sannan ita da Reedah suka fita daga gidan.

Mai lallen da ta yi ma Ilham har ta gama haďa kayanta za ta tafi, Liyana ta tsayar da ita aka fara yi mata ita ma.

Da yamma aka fara gudanar da Mother’s Day inda a gidan Nenehn aka yi sa.

Gaba ďayansu abaya suka saka mai shegen kyau da ďaukan ido.

After three Days.

Rana ba ta ḳarya, yau aka yiwa yaran Liyana yanka kuma a yau aka ďaura auren ABUBAKAR AHMAD QASSIM KYARI (Sultan) da MAIMUNATOU NABIL ALIYU SHUWA (Ilham), da na UMAR ABUBAKAR QASSIM KYARI (Amir) da FATIMA AHMAD QASSIM KYARI (Assultanah), sai kuma ALIYU AHMAD QASSIM KYARI (Hydar) da kuma MARYAM ABUBAKAR QASSIM KYARI (Marwa).

Auren da dubunnan mutane suka shaida.

A can b’angaren Liyana kam tun safiyar ranar take kuka mai cin rai.

Har shi kansa Aliyu was shocked da Jin wannan maganar aurensa da aka ɗaura, dan shi da ya ga Liyana ba ta so sai ya janye ya bama Marwa hak’uri.

Jikinsa na rawa ya nufi gidan Neneh dan ya san duk inda Liyana take labari ya riske ta.

Gidan cike yake da mutanen arziki, a hankali ya yi ta ḳeta mutane har ya shiga dakin da yake da tabbacin ta na ciki.

Aikam tunaninsa ya basa daidai because ta na kwance ta na kuka, sauran sisters ďinta suna tare da ita duk sun zagayeta sai kuma wayanda yaranta ke hannunsu.

Ganinsa da ta ḳara yi ya ḳara sosa mata zuciya da gudu ta tashi tare da juya masa baya ta fashe da Wani kalar matsiyacin kuka.

Su Reedah da Unaisah na ganin hakan suka fice daga ďakin gaba ďaya da sauran ya’mmatan ďakin. Dan Ilham na tare da Ammi.

A hankali ya karasa shigowa ďakin tare da zama kusa da kanta, haďe da kai hannunsa zuwa ga jikinta.

“Don’t touch me, ba dai aure ba, ka yi ai sai ka bar rayuwata na huta tun da ba sona kake ba daman.” Ta yi maganar tare da jinginar da kanta a kan gadon.

“Liyana, please listen, ki tsaya ki saurareni.” Ya yi maganar tare da hawa kan gadon sosai.

“Ba na son maka magana, Just goo ka bar ni, daman ni I didn’t deserve to be happy a rayuwata, ka tafi ka bar ni bana son dogon sharhi just leave me alone.” Ta karashe maganar tare da jan bargo har kanta.

“Okay.” Ya faďa a sanyaye tare da zura takalmansa ya bar ďakin.

Da ido ta bi ḳofar tare da fashewa da wani sabon kuka hannunta riḳe da kanta.

Da fitarsa bai zarce ko ina ba sai gidan Mami, dake cike da mutane because a gidan ake gabadaya shagulgulan har da nasu Amir din, ďakin da abokansu ke ciki ya nufa a guest room din gidan nasu.

Ko da ya shigo cikin ďakin kwanciyyarsa ya yi akan gadon dake guest room ďin gidansu, Amir ne ya ḳaraso kusa da shi tare da ďan dafa shi Sannan ya ce “ Hope ba ta cikin damuwa?.” Wani kalar ajiyar zuciya ya furzar tare da faďin “she’s there

crying, ni na rasa ma yadda zan yi, tun da na fara maganar auren nan ba kullum take bama yaranta Nono ba , wallahi na rasa ya zan yi, kai ma kuma ka san duk biyun Ina son su.” Ya karashe maganar tare da dafe kansa.

“Shegee.” Amir ya fada tare da kyalkyalewa da dariya.

Tsaki kawai Hydar yaja tare da manne kansa a pillow ya na tunanin solution.

Daren ranar

Nasiha sosai aka yiwa Ilham dake kuka kamar ranta zai fice sannan aka wuce da ita ďakin mijinta.

Liya babu abin da take sai kuka, su Aida kam sai madara kawai aka dinga banka musu.

Neneh kam she’s busy da kawayenta da ma cousins dinta dan jira take a watse ta fara kinsawa jikarta abubuwa dan wannan Marwar mai zubin karuwai da wannan halittar da ba a waye take ba barinta da Marwa babban hadari ne.(kai Neneh Liyana ce ba ta waye ba 🤣🤣🤣)?

Washegari bayan mutane da dama sun watse Neneh ta shigo ɗakin Liyanar da ita ma ta gama shiryawa su Unaisah da sauran yammatan na ta bata baki a kan Kar ta tafi ta bari ta gama wankan gidan.

“Oh ni Ajiddeh da ban da aure da naga takaici, yanzu akan kishiya kike kokarin barin abin da zai ceceki, toh ai shikenan ruwanki ki zauna ruwanki ki tafi, amma kishiya kamar Marwa sai kin daina saka wannan shaigun wandunan naki kin dawo kin fara saka riga Iya gwiwa, Allah na tuba Marwar da duk k’iba ya mai data kamar saniya ai idan kika saka Kayan da nake fada miki ko kallo bata ishe sa ba.” Nenehn ta faɗa tare da ajiye mata wani haɗin data kawo mata sannan ta fice daga dakin.

Fashewa ta ḳara yi da kuka sannan ta kalli Salimah dake tsaye da suka shigo tare da Neneh.

Shanye abin da Nenehn ta bata ta yi sannan ta ɗauki mukullin motar ta picanto dake gidan Nenehn.

“Wai Liya tafiya za ki yi yanzun?.” In ji cewar Reedah.

“Just think Wallahi Liya, yanzu ki dauko atm dinki Muje kasuwa muyi siyayyar Kayan shegu, sai ta Raina kanta for sure.” Unaisah ta fada tare da ajiye laptop dinta akan standing mirror

“Toh ku taso mu tafi.” Liyana ta fada tare da turo bakinta.

daga haka suka fice daga gidan.

sai da ta biya ta gidan Lily sannan suka fita tare.

Kaya suka siya na gani na faďa, sannan suka dawo gidan.

still ba ta daina shirya kayanta ba dan a cikin satin nan zata koma gidanta.

B’angaren Baban gida Hydar kam sun nunawa junan su yadda suka yi missing junansu shi da Marwa.

Amma har lokacin bai sakar mata fuska ba.

After a week

“Wallahi tafiya zan yi babu wani kwana arba’in da zan zauna yi, mijina na can tare da wata.” Liyana ta faďa hawaye na zuba a idanunta.

Su Reedah ne keta bata baki da ta zauna Kar ta tafi amma hakan nan ta yi biris tare da ďaukan wani basket ta zuba yaran gaba daya a ciki.

“Ku bar ta kar wanda ya hana ta , Nima daman na gaji da zamanki ki tattara ki tafi ďin tun da ba’a dole, yara kuma an riga da anyi musu yanka to mai ya rage daman?.” Neneh ta faďa tare da shigowa ďakin sosai.

“Ni ai ban miki magana ba.” In ji cewar Liya da fuskarta ke a haďe.

“Ke kin isa kiyi dani?, ai kin yi kaďan sai mai jan kunne.”

“Neneh ki daina zagar min Abbhina.”

“Ka ga masu Uba?, toh Allah ya jikan mahaifina da gafara.”

“Wannan ke ta shafa, Reedah ku Taya ni kai kayana mota mana yamma na yi.”

“Ba za ki je yiwa Khairatun Sallama ba?.”

“Ai ba uwar mijinki bace.” Liya ta fadawa Nenehn tare da dauke kanta.

“Ba shakka, ai Biri ya yi kama da mutum.”

Tashi su Reedahn suka yi tare da kama mata ɗan trollynta da Aliyun ya kawo mata da ta yi fitar suna da su ranar bikin Ilham.

Sai ḳarfe biyar da minti 47 ta iso cikin gidan, ko ta kan trollyn ba ta bi ba ta kwa shi yaranta ta nufi cikin gidan dasu.

Ba ta wani tsaya kwankwasa ḳofa ba ta bude kofar living room din a hankali.

Guje-Guje suke a living room ɗin kamar yara, kowannensu hannunsa riḳe da throw pillow, Aliyu ne ya yi nasarar kama Marwa hakan ya sanya sa buga mata pillow ɗin a kai har sau biyu tare da rungume ta ta baya ya na mai ɗaura kansa a kan kafadar Marwar.

D’ago kansa da zai yi suka yi ido hudu da Liya da ta kusan mintuna biyu a tsaye a wajen ta na kallon su, da sauri ya saketa tare da sosa ḳeyarsa tare da faɗin.

“Babe you’re back?.” Ya faɗa ya na dan sinnar da kansa.

“Noo, I’m gone, Rubbish.” Ta karashe maganar tare da yin wani kafirar tsaki.

Jiki a sanyaye Marwa ta ce “Maman Triplets sannu da zuwa.”

“Riḳe kayanki, za ta miki amfani.” Ta na faɗan haka ta ɗauki yaranta sannan ta wuce saman ɗakinta da su.

Ita ma Marwa bayanta ta bi ta shige ɗakinta aka bar Aliyu kaɗai a falon ya jinginar da kansa a kan kujera.

”Buh you told me ta amince sannan ka aure ni , Ko dai ba ta sani ba.?

Saḳon da ya shigo wayarsa kenan, wani tsaki yaja Sannan ya mayar da kansa kan kujerar tare da lumshe idanunsa.

A hankali ya tashi tare da nufar cikin ďakin nata.

A tsaye take jikinta daure da towel, Wanda alamu sun nuna daga wanka ta fito .

Ḳura mata idanu ya yi dan ya rasa ma ta ya zai mata bayani.

“Malam ka faɗi abin da ke tafe da kai zan kulle ḳofa.” Liya ta faɗa tare da ɗaukan wani auduga da kwalban misk a hannunta.

“Liya Please ki yafe min.”

“Na ce kayi wani abu?, toh dan girman Allah ka rabu da ni, jeka wajen matarka zan nemeka.” Ta faɗa tare da ḳara tamke fuskarta.

“Tom na gode, can I see my daughters dan Allah?.”

“Ga ka ga su.” Ta yi maganar a dakile.

Ya kusan hour ďaya tare da yaran ya na ta musu wasa sannan ya mata sai da safe ya bar mata ďakinta haďe da kulle mata ķofar.

Wani kukan ta ķara fashewa da shi yadda ta ga ko wani damuwa bai yi ba.

Haka rayuwa ta cigaba har yaran suka yi wata hudu Aliyu bai taba nemanta ba, sai dai ya shigo ďakin ya dauki yaransa ya musu wasa ya kuma Karawa gaba.

Abin tun baya damunta har ya fara damunta domin Ko da wasa bata sakarwa Marwa fuska gashi wani shishige mata da take yi har tausayi Marwar ke bata.

Kamar kullum ta na zaune ita da su Alya da ta ajiyesu a kan kujera suna wasa ita kuma ta na zaune ta na chatting a wani group dinsu na instagram _Cousins forum_ wan da na iya cousins na su ne.

Marwa ce ta ḳaraso cikin falon cikin shigarta na wani atamfa mai kyau da ya gama shan crystal stones masu tsadar gaske.

jikinta sai tashin ḳamshi mai dadi̓ yake.

Cikin sassanyar muryarta ta ce “Sis zan je gidanmu na dawo Abbah ya dawo daga Saudi tun shekaran jiya.” ta yi maganar tare da mikawa Alynerh hannu da tun shigowarta take ta ɗan shure-shure alamun ta ɗauketa.

Liyana ce ta ɗago ta kalli Marwar da Alynerh ke sab’e a kafaɗarta tare da fadi̓n “ Toh a dawo lafiya, da Alynerh za ki tafi?.” Ta yi maganar a dan sanyaye.

“Eh sis yanzu zamu dawo.”

“Ai kam kin taimaka min bara na ɗauko miki madara da feeder da spare na kayanta.”

“Ina dasu anan ba sai kin sha wahala ba.” Ta karashe maganar tare da sakin wani lallausan murmushi.

Bayan sun fita ma babu abin da Liya ke yi sai judging dꞌin kanta da Marwar.

“Yeah Marwa is a very kind person, na dade ina testing hakurinta ba ta tab’a tanka min ba, ta na son yarana, ya’n uwana idan sun zo ta fi mai da hankalinta a kansu , I think gwara na ajiye kaina mu yi zaman lafiya , na bawa mijina peace of mind da yake da bukata, yeah a good idea.” Ta na fadꞌin haka ta janyo keken yaranta sannan ta sanya su a ciki, tare da kiran Salimah da ta dawo gida, dan tun da ba girki take ba shiyasa ta bar Salimah a can gidan Nenehn.

Cikin hour biyu Salimah ta iso gidan suka fara abin da ya dace.

Misalin karfe shida motar Aliyu ta ḳaraso cikin gidan, bayan ya yi parking dꞌin cikin gidan suka nufa shi da Marwa da har Yarinyar hannunta ta yi bacci, dan bayan ya

dawo daga office din Abbhu ya biya gidan Kanin baban nasa dan gaida sa tare da dauko Marwar suka nufo gida.

Hannunsa cikin nata suka ḳaraso cikin falon, Zaune take cikin wani lifaya lace black color ɗinkin bubu gown mai mugun kyau da tsada, ḳafar ta na sanye da wasu flat designer shoes masu kyau da aji.

A lalace ya ɗago da kansa tare da kai dubansa gareta, ta masa wani kalar mugun kyau mai tsayawa a rai.

Da sauri ya ďauke kansa daga dubanta tare da sakin hannun Marwa ya yi saman ďakinsa.

Tab’e bakinta ta yi tare da binsa a baya.

Har ya fara cire kayansa domin shiga wanka ta yi sauri ta shige jikinsa tare da Fashewa da Wani kalar kuka.

Wani nannauyan ajiyar zuciya ya sauke tare da Kara rungume ta a jikinsa ya na mai shafa mata baya....

> Soft Noorah ☺

> Pending Amarya as usual

> Pending Amarya's Book corner Extra ordinary every day 😊

> I'm back 🙃

Pending Amarya as usual✍

THE REGRET

JAW

Pending Amarya 64

Ending.....

https://whatsapp.com/channel/0029VbAyucH7j6g0IDCpPi2V

Death is a reminder that this worldly life is temporary, and the eternal life in the Hereafter awaits those who obey Allah.

Da sauri ya ďauke kansa daga dubanta tare da sakin hannun Marwa ya yi saman ďakinsa.

Tab’e bakinta ta yi tare da binsa a baya.

Har ya fara cire kayansa domin shiga wanka ta yi sauri ta shige jikinsa tare da Fashewa da Wani kalar kuka.

Wani nannauyan ajiyar zuciya ya sauke tare da Kara rungume ta a jikinsa ya na mai shafa mata baya.

“I missed you badly Wife.” Ya fada da wata dasasshiyar muryarsa.

“Missed you More Tesoro.” Ta faďa tare da kankame sa.

They make love ❤

Ganin yaran nata kuka hakan ya sanyata ďaukansu tare da yin bangarenta da su, a ranar dai a ďakin Marwar yaran suka kwana dan har wajen 10 babu alamarsu.

Sosai suke zaune Lafiya da Marwa, komai idan Marwa ta gani sai dai kaji ta ce sis. Ita hakannan kawai taji ta na bala’in son Liyana.

After 2 years □□

Yaran Liya sun girma sun yi wayo sosai, tsakanin ta da Marwa kam sai zallar soyayya.

Mr Aliyu namu kam a yanzu komai na electronics a duk faɗin duniya a wajen sa ake samu , sosai ya shahara fiye da yadda a ka san shi a baya, dan a yanzu arziki ya ci uwar na da.

A cikin shekarun biyun nan kam abubuwa da yawa sun faru, har da rasuwar Jiddah da kuma Haihuwar Assultanah da Ilham, da kuma auren su Rashanda da aka yi. (Allah ya jikan Jiddah da gafara ya sa ya huta).

Bangaren Liyana kam zaune suke ita da Marwa a living room suna kallo and at the same time suna shan fruit salad a bowl ɗaya.

Alynerh ce ta fito daga cikin ďakin da yake downstairs idanunta na zubar da hawaye ta ḳaraso wajen Marwa haďe da nuna mata hannunta da Alya ta mintsineta, cikin muryarta mai sanyi dake kuma nuna yarinta ta ce “Ummi Alya ko.” Ta faďa tare da fashewa da kuka ta na pointing ḳofar ďakin da suke wasan.

“Sorry Baby Maama.” Marwa ta faďa tare da ďaura ta a cinyarta da ḳyar saboda ta na da jiki ma shaa Allah.

“Babu wani sorry, your daughter will always be at fault, a tambayi su Alya ďin aji akwai abin da ta musu ai.” Liya ta yi maganar tare da dungurewa Alynerh kai.

Ḳara fashewa ta yi da kuka tare da faďin “Ummiii.”

“Naam yar Ummi, don’t mind Ammi kin ji, kwanta kiyi bacci Papi na dawowa zamu je shan ice cream Okay.?” Marwa ta fada tare da kwantar da ita a kan kujerar falon.

K’amshin turarensa shi ya sanar da su isowarsa, a hankali ta ďago tare da kallon cikin idanunsa.

Murmushi ya sakar musu a hankali tare da faďin “Yau babu shopping ne?.” Shiru ta masa kawai tare da ďauke kanta dan haushin rashin barinta zuwa bikin lily kawai take.

Kallon Marwa ya yi tare da faďin “ ya jikin ki?.” “Da sauki Papi.” Ta fada tare da sauke kanta kasa.

“Ma shaa Allah, mai kuka dafa?.”

“Idon ma tambayi.” Liya ta fada tare dalla masa harara.

“Ina uwayen masu gida for the first plac…?”

Bai karasa ba wasu yara Kananu suka fito da gudu “Papi, welcome.” Suka faďa tare da rungumesa.

Alynerh da har bacci ya dauketa ita ma ta tashi da sauri tare da shigewa jikinsa haka ya yi ta yiwa yaran wasa, suna kyalkyala dariya.

Ta shi Marwa ta yi da tsohon cikinta dake jikinta sannan ta nufi hanyar kitchen ta zubo masa abinci suka hau ci da yaransa.

Da kyar take tafiya ta sannan ta haura saman ɗakinta.

Tashi ita ma Liyanar ta yi ta bar sa a falon shi da yaransa ta nufi ɗakinta domin huta wa.

After 3 months.

Tun safe Marwa ta tashi da faduwar gaba , bayan ta Kira Umminta suka ɗan yi hira sannan ta wuce bangaren Liyana ta fara taya ta gyaran clothset ɗinta dan ita ma Salimah ta yi aure kuma wadda aka kawo musu ba su gama yarda da ita ba.

haka suka ďinga hira har da dariya har suka gama gyara clothset din.

Ko da suka gama ma kitchen suka nufa suka fara ďora girki saboda Aliyu ya na gari.

“Sis baya na ciwo yake min wallahi.”

“Kai Marwa mai ya kawo ciwon baya muna zaune kalau.”

“Laa kin manta Ina EDD dina yau?.”

“Yeah hakane, toh muje hospital mana.”

“Yeah bari na tambayesa toh.”

“Kin ga ki ajiye maganar tambayar nan agefe kin san yanzu wani iskanci ya tsiro da shi na hana mutum fita, mu gama hadawa shi da yaransa abinci mu yi ficewar mu.” Liya ta fada da zallar bacin rai.

Ajiyar zuciya Marwa ta sauke sannan suka karasa girkin.

Ammi da Abbhi sun dawo da Neneh can gidansu da bata da abin yi sai maganar Jiddah, da anyi magana za ka ji ta na fadi̇n Allah sarki Jiddah na Ajiddeh.

Duk ta koma abin tausayi amma baḳin halin nan nata na nan.

Ba su je hospital din ba a ranar sai washegari

Washegari da sassafe suka fara shirya breakfast bayan sun gama suka jera sa a dining.

A hankali yake saukowa daga stairs idanunsa akansu , sosai matan nasa ke burgesa yadda suka haďa kan su suke zaune Lafiya babu wariya.

Karasowa ya yi ya zauna a kan dinning table din, cikin wani kalar sanyin da ba’a san ta da shi ba ta tashi tare da fara serving ďin su abincin.

“What’s wrong Marwa?.” Ya tambayeta a sanyaye tare da kallon fuskarta.

Sunkuyar da kanta ta yi tare da faďin “ Nothing, I’m just missing something da ban san ko mai ye ba.” Ta fada a sanyaye tare da share kwallar dake sauka a idanunta.

“In shaa Allah za ki haihu lafiya kin ji Mom Alynerh?, oya fara cin abincin ki kafin yaranku su farka.

Liyana kawai danne hawayenta take dan sam yanxu ta tsani Jin sunan mutuwa.

Har suka gama breakfast din ta na satan kallon Marwa.

Suna gama breakfast dïn suka fice daga gidan dan sai da Marwa ta tambayi Aliyun za ta je hospital.

Ji ya yi kamar ya bisu zuwa hospital dĩn amma yanayin aikinsa yau da kuma yaransa ba zai sa sa ya fita a gidan ba.

Tun kafin su isa hospital nakudar ta yi tsanani, kafin su karasa ma har wani ruwa da jini ya fara fito mata.

Da gudu Liyana ta Kara figar motar har suka karasa hospital dĩn.

Ta yi kusan 5hrs ta na labour sannan ta haifi kyakkyawar ya’r ta mace fuskarta na fidda hawaye ta kamo hannun liyana tare da faɗin “Sis ba zan rayu ba na sani, ki kula min da wannan ya’r tamkar na ki , dan Allah ki yafe min duk wasu abubuwan da na miki, ki rokar min yafiyar Ummi nah , sannan ki shafa min kan Alynerh ki kula min da ita, and promise me ba za ki ɗin ga nuna mata banbanci ba saboda ta rayu da ni, sannan ki roki Kowa ya yafe min duk wani abu da na musu, sannan ki fada ma Papi Ina son sa ba zan kuma daina son sa ba pls.” Ta faɗa tare da fara kalmar shahada ta na iddasa wa ta cika.

A firgice Liyana ta ɗago tare da kallon yadda take fidda wani siririn murmushi.

Da wani mugun ḳarfi ta ce “Noooo, Marwa, sau nawa ki na cewa tare zamu tsufa mu aurar da su Alynerh, where are the promises?.” Ganin ihun ya yi yawa hakan ya sanya doctors fitar da ita daga ward din gabadaya.

Sannan suka gyara jikin Marwa tare da lullubeta hade da gyara yarinyar.

Kuka kawai take babu kakkautawa ta ma rasa wa za ta kira.

Daga karshe dai Aliyu ta Kira ta sanar masa.

A firgice ya tattara yaransa ya nufo hospital ɗin kamar wani mahaukaci, in Banda Innalillahi babu abin da yake nanatawa.

Alynerh ce ta karasa wajen Liyana tare da faɗin “Ammi where’s Ummi?.” ta faɗa da muryar kuka dan ganin iyayen nata na kuka.

Wani zallar tausayin yarinyar ne ya kamata hakan ya sanya ta rungumeta tare da fashewa da kuka, dan tafi sabawa da Marwa.

Kafin yamma har an hallara a cikin hospital ɗin sannan aka nufo gida aka mata wanka aka nufi gidanta na gaskiya da ita.(haka rayuwa take daman, Allah ya sa muyi kyakkyawar karshe).

Babu Wanda bai zo ba a dangin liyan dan sai a ranar ma Ammi ta san yadda dakin Liyar yake.

Amir ma kamar zai haukace haka ya yi ta kuka Sultan na taya sa yi.

Liyana kam idan ta yi ido hudu da clothset dinta take sake Fashewa da kuka.

Har aka yi sadakan bakwan Marwa Liya ba ta samu kanta ba.

Dan sai da ta saka Hydar siya mata sabon clothset ta fara sabon zubin kaya dan ba zata taba warware linkin da Marwar ta mata ba.

After 5 years

Alhamdulillah suna zaune Lafiya tsakaninta da Aliyu.

Yaranta na da 7 years Ya’r Marwa da aka mata yanka da Maryam sunan mahaifiyyarta na asali kuma ake kiranta da Marwa ta na da 5 years.

Rayuwarsu suke cikin farinciki da Qaunar juna.

Aliyu ya gina gidan marayu da masallatai uku da sunan Marwa.

Sannan ya mallakawa Liyana wajen shakatawansa.

Every blessed Friday kam sai sun je kabarin Marwa sun mata addua.

“Wife, ki shirya muje gidan Mami da Ammi gobe zamu koma China in shaa Allah.”

Wani kalar murna yaran ke yi banda Liyana da ta kurawa linkin da Marwa ta Taya ta kusan shekaru 6 da suka wuce ido.

Kwallan da ya zubo mata ta share tare da kulle clothset ɗin sannan ta nufi dayan da take zuba kayanta a yanzun.

Kayan da zata saka ta zabo sannan suka wuce gidan Mami.

Ta Taya ta hira sosai daga nan suka bar gidan ta na kallon gidan Neneh ta Kara fashewa da kuka ta na tuna memories da dama.

Daga nan suka wuce gidan Ammi sun yi hira sosai ta na kallon gidan da duk ya canza mata.

Sai da dare suka bar gidanta, dan Abbhi ba ya ma kasar, kamar za ta yi kuka sai da ya ce mata zai zo har China sannan ta ware suka nufo hanyar gida.

Shima sai da suka biya gidan su Ilham da Assultanah, Amir nata tsokanar ta har suka dawo gida.

Washegari da safe jet dinsu ya daga zuwa china.

Ji take tamkar ta bar wani gangar jikinta a Nigeria.

Tun da jirgin ya daga take kuka har suka zo China ba ta bar shasheka ba.

Hydar har ya lallasheta ya gaji yaran ma duk sun yi bacci a jet ɗin.

Sun isa China Ma shaa Allah sun fara gudanar da Sabuwar rayuwarsu duk da Liyana ba ta daina kewar Marwa ba dan a ɗakin da Marwar ke zaune a nan China take kwanciyyarta da rana.

ALHAMDULILLAH anan ni Faridat Aliyu Ibrahim (Pending Amarya) zan kawo karshen littafina mai suna THE REGRET.

Allah ya yafe min kurakuren da suke ciki.

Littafin nan gaba daya na sadaukar da shi ga Yayyuna sannan Qawayena. Na gode sosai da gudumowar da kuka bani Musamman my Aunty Maryama Allah ya raya miki yaranki ya sa ki fi karfin makiyanki ya Baki duk abin da kike so Sannan ya shiga cikin lamarinki.

To All my friends who stood by me kuma Ina muku godiya , ban manta da ku ba.

Ga duk Fans dina masu karanta littafina kuma Allah ya saka muku da alheri. Musamman su Unaisah, Dimple Oum daughter, Faiza Idris da ma wayanda ban kira ba Allah ya hada fuskokinmu a Aljannah ❤

sannan Ina muku Albishir da sabon novel dina mai suna IMAM bayan sallah In shaa Allah, Ramadan Mubarak to my lovely Readers □□□□

Buh Imam is a paid Book

#Vip 1000

Regular 500

Ma’assalam

Fi Amanillah ❤□□

Soft Noorah ✍

Kuyi haḳuri mun fara kenan sai mun dire storyn Allah ya mana jagora □□